Collection
"Devenir Citoyen"

Lexique

Haoussa Français

Démocratie et Développement à la base

Terminologie essentielle

EMOCRATIE

Collection "Devenir Citoyen"
Réalisé avec l'appui de La Coopération Suisse au Niger
Décembre 2000

Préface

Le processus de décentralisation après les évènements dramatiques aux quels il a conduit le 9 avril 1999 suite aux irrégularités ayant émaillé les élections du 7 février 1999, suscite de nouveaux espoirs avec la promesse des autorités de la Vème République d'organiser et de mettre en place des assemblées et exécutifs locaux.

Il va de soi la mise en places de telles institutions va nécessiter de nouveaux comportements et attitudes tant aux plans politique, administratif, social que politique et accroître la responsabilisation des populations dans la gestion de la cité et rendre effective la démocratie à la base.

Ces attitudes et comportements des citoyens sont nécessaires à l'accompagnement des normes officielles de l'Etat de droit (séparation des pouvoirs, liberté d'opinion , d'association, élections libres et transparentes, etc. ..), au renforcement de la démocratie et à la création des conditions propices à un développement durable, maitrisé, contrôlé par les populations et bénéfique pour tous.

En effet l'élection des conseillers régionaux, départementaux et locaux donnera l'occasion aux structures décentralisées de mieux concevoir, gérer et contrôler les actions de développement à la base. Ceci nécessite une plus large communication entre administrés et administration, entre une minorité utilisant le français comme langue officielle et une majorité jusque-là laissée à l'écart de la conception des actions entreprises à son nom.

Mais pour rendre effective, l'esprit de démocratie de proximité sous-tendue par les lois décentralisatrices, une des conditions nécessaires, est l'acquisition, en langues maternelles, par les élus locaux, en majorité des leaders d'opinion locaux (paysans, éleveurs, commerçants.. ne sachant ni lire, ni écrire dans la langue officielle), les compétences indispensables pour comprendre le milieu, les techniques modernes de planification, de gestion d'une collectivité.

Il est donc impératif de disposer, dans les langues de ces élus, d'une terminologie adéquate afin qu'ils s'approprient les outils indispensables à la gestion de la collectivité d'une part, de l'autre pour la création des conditions permettant la communication entre les principaux acteurs de la vie sociale et rendre ainsi possible une vie politique locale en langues comprises par tous.

C'est pour atteindre un tel objectif que Démocratie 2 000 a initié un programme d'éducation à la démocratie dont l'objectif est de toucher les franges les plus nombreuses de la population, notamment les ruraux par l'utilisation des supports et médium en langues nationales.

Ce choix s'explique par le fait que, les programmes de vulgarisation, en français, du droit, de la promotion de la démocratie et de la formation des organisations

paysannes ou de base excluent l'essentiel des cibles visées. Et les rares programmes en langues nationales restent peu compris parce que la terminologie, les concepts et le vocabulaire utilisés sont "académiques", inaccessibles, non standardisés et souvent non acceptés par les populations, réduisant du coup la compréhension des messages et l'impact de ces programmes.

Aussi D. 2000, pour aller à la rencontre et préparer le terrain à la décentralisation, a-t-elle initié, un programme d'information et de formation pour le développement local (INFODEL). Ce programme a une double finalité : d'une part préparer l'environnement institutionnel et les outils pour les ONG, associations et projets de developpement permettant la formation des futurs élus afin qu'ils assurent la charge de leur mission en acquérrant les compétences nécessaires et, de l'autre, mettre à la disposition de la société civile des outils susceptibles de lui permettre de se constituer, au niveau local, en contre-pouvoir responsable.

Le projet " Terminologie électoral en langues Hausa et Zarma, sous programme de ce vaste chantier, a pour objectif de fournir aux personnes physiques comme morale intéressées par la promotion de la démocratie et les questions de developpement participatif le vocabulaire essentiel de la vie administrative, parlementaire, des droits de l'homme, de la justice, de la gestion...bref de la bonne gouvernance.

Le présent document est le résultat de plus de deux ans de travail, de plusieurs équipes et spécialistes de D. 2000. Il a été constitué à partir d'un corpus initial en Français puis traduit " en laboratoire ". Le produit qui en est issu a été testé sur le terrain pour obtenir un vocabulaire standardisé, accessible et accepté par les différents locuteurs des variantes régionales des langues Hausa et Zarma. Certes, ce document comporte de nombreuses omissions et des imperfections. Vos remarques et suggestions contribueront sans nul doute à l'améliorer. L'essentiel n'est-il pas d'oser et de poser le jalon pour l'avenir ?

Nous ne saurons terminer cette préface, sans adresser nos vifs remerciements, au bureau de Coordination de la Coopération Suisse pour le soutien actif apporté à ce projet et surtout pour sa conviction que l'avenir est dans le développement local.

Nos remerciements vont également à tous ceux qui ont apporté leur soutien à ce travail et particulièrement à Messieurs Hamadou Soumana Souna, Ousséini Soumana, Boubacar Sabo, Mahaman Ragi Adamou, Aboubacar Issoufou, Sidi Abdouraouf et Omar Issifi.

Ali R. Sékou Maïna
Chef département programme Ong D2000

HAUSA

Abdiquer : Kasawa : Yin murabus, fasawa, zarumi ya kasa gaban abokin hamayyarshi

Abnégation : Bada-kai : Ku-zari. Shugaban jamhuriya yana gayyatar yan ƙasa da su bada kansu ga ayyukan ginin ƙasa.

Faire preuve d'abnégation : nuna kuzari : bada kai cikin tafiyar da wasu ayyuka, bada ƙoƙari.

Abolir : Sokewa : An soke bauta a shekarar 1848.

Abolir une loi : Soke doka, kashe doka.

Abrogation : Sokewa : kashewa

Absence de volonté politique : Rishin kyakkyawar niyya a fannin siyasa : rishin himma a fannin siyasa. Rishin kyakkyawar niyya a fannin siyasa ke hana ci-gaban harsunan ƙasa a Nijar.

Absentéisme parlementaire : Ƙaurace wa ayyukan majalisar dokoki : Kin halartar ayyukan majalisa daga wani ɗan majalisa ko rukunin yan majalisa. Yan majalisa na bangaren adawa sun ƙaurace wa ayyukan majalisa don nuna rishin jin daɗinsu bisa wariyar da suke huskanta cikin buron majalisar dokoki.

Absolu : Mai tsanani : wanda ba ya da sassauci, mai tsananin iko, mai kauce wa demokarasiya. Shigowar mulkin demokarasiya ta kawo ƙarshen mulkin masu tsananin iko.

Pouvoir absolu. Tsananin iko : ikon kama-karya

Abus : Zaƙewa : wuce gona da iri wajen tafiyar da iko

Accéder : Cimma : tarar da wani guri, wani hali, samu - ƙasar Nijar ta cimma mulkin kanta a ranar 3 ga watan Agusta 1960.

Accélération : Gaggautawa : Sauri/gaggawa wajen aikata wani abu. Gaggautawa wajen ɗaukar matakin amincewa da dokar kasahin kuɗi yana bada damar zartar da wasu tsare-tsaren da ke sahun gaba.

Accession : Samu : Cimma wani guri, wani hali. Ranar 3 ga watan Agusta 1960, ita ce ranar samun mulkin kan Nijar

Accord : Yarjejeniya : 1.) Cikakkar yarda bayyananna ko wadda ba a bayyana ba tsakanin ɓangare biyu ko hiye da haka. Yarjejeniyar da aka samu tsakanin gwamnati da yan tawaye ta bada damar kawo kwanciyar hankali a arewancin ƙasa. 2.) Haɗin gwiwa tsakanin ɓangare biyu ko kiye da haka. A lokacin zaɓen shugaban jamhuriya, an samu haɗin gwiwa tsakanin jami'yun siyasa daban-daban.

Accord de coopération - yarjejeniyar kafa huldɗa : huldɗa tsakanin ɓangare biyu ko kiye da haka.

Accord commercial - huldɗar kasuwanci : amincewar saye da sayarwa tsakanin ɓangare biyu ko hiye da haka.

Accord international : yarjejeniya tsakanin ƙasashe : shiri tsakanin ƙasashe.

Accorder une audience : Saduwa : tattaunawa/zantawa, bada lokacin saduwa daga wani babban mutum. Shugaban jamhuriya ya sadu da shugabannin jam'iyun siyasa na ɓangaren adawa.

Accréditer : Wakiltawa : bai wa wani cikakken ikon aikata wani abu. Shugaban jamhuriya ya wakilci jakadai a ƙasashe maƙwabta.

Accroissement : Yaɗuwa : 1.) bunƙasa, ci-gaba, ƙaruwa. Yaɗuwar al'umma

2.) hakkin da ke kawo ma mutun ƙarin wani abu. Magada (masu gadon) sun samu ƙarin miliyan 2 dangane da hakkinsu.

Acculturation : Yada al'adu : Halin wanda ya saki al'adunshi don ya rungumi wata al'ada. Sai ƙasa ta ɗauki ƙwararrun matakai don hana matasa yada al'adunsu.

Acculturé : Wanda ya yada al'adunshi : wanda al'adunshi suka kubce mashi kuma ya rungumi wata al'ada. Hanyoyin sadarwa na zamani na sa matasa suna yada al'adunsu.

Accumulation : Tarawa : Tsibewa, haɗa abubuwa wuri guda. Tara dukiya.

Accumulation d'expérience : Samun ƙwarewa : tara sani.

Accumulation des pouvoirs : tare iko : samun muƙamai da yawa sa'a guda.

Accusation : Zargi : aza wa wani ƙazahi ko laifi. Gwamnati ya ƙaryata zargin da y'an adawa suka yi mashi.

Accusé : Wanda aka zarga : mutumen da aka ɗora wa laifi. Juju ya yi wa wanda aka zarga tambayoyi.

Accuser : Yin zirgi : ɗaukar mutum a wanda ya yi laifi. An zarge shi da cin kuɗin gwamnati.

Acquis : Hakki : Y'anci ko hanyar aikata wani abu. Kungiyar ƙwadago tana kiran magoya bayanta da su tashi tsaye don kare hakkinsu.

Acquis du peuple. Hakkin al'umma : abun da aka tabbatar da hakkin al'umma ne.

Acquitter un accusé : Sallamar wanda aka zarga : Sakin wanda ake zargi. An sallami wanda ake zargi saboda rishin cikakkar shaida.

Acte : Takardar shaida : takarda mai haƙiƙantar da wani

abu. An ba shi takardar shaidar saidawa.

Acte de décès : takardar shaida rasuwa : takarda ma tabbatar da rasuwar wani mutum.

Acte de mariage : takardar shaidar aure : takarda mai tabbatar da an yi aure.

Acte de naissance : takardar aihuwa : takarda mai tabbatar da aihuwar yaro.

Acte délictueux - Babban laifi : abun da shari'a ke hukuntawa.

Acte fondamental - Babban mataki : ginshiƙi cikin tafiyar da ayyukan wata ma'aikata ko wani gwamnati.

Acte historique : Abu na tarihi : abun da ba ya mantuwa, mai mahimmanci cikin tarihi.

Acteurs politiques : Ma'abutan siyasa : waɗanda ke taka mahimmiyar rawa a fagen siyasa cikin ƙasa. Ya kyautu ma'abutan siyasa su yi aiki don amfanin ƙasa kawai.

Action : Aiki : Abun da wani ya yi - Aikinshi ya ƙayatar da kowa.

Action civique - Aikin kishin ƙasa : aikin da ake amfanin ƙasa kawai, bauta wa ƙasa.

Action de développement. Aikin ci-gaba : tsare-tsare na ci-gaban al'umma.

Action économique : Aikin tattalin arziki : hanyoyin da ake ɗauka don bunƙasa tattalin arziki.

Action publique : Aikin kariyar al'umma : gabatar da shari'a don kare hakkin al'umma.

Action sociale : Aikin kyautata rayuwar al'umma : abubuwan amfanin da wani mutum ko wata ƙungiya ke yi.

Activité : Harakoki : Ayyukan da mutum ko ƙungiya ke yi a wani fanni. An dakatar da harakokin siyasa bayan da aka yi juyin mulki.

Activité économique : harakokin tattalin arziki : ayyukan ɗan Adam na biyan buƙatun al'umma ta hanyar sarrafa kayayyaki da kuma saye da sayarwa.

Activité politique : Harakokin siyasa : dukan ayyukan da suka shafi tsare-tsaren siyasa.

Activité sportive : Harakokin motsa jiki : dukan ayyukan da suka shafi wasannin motsa jiki.

Activités professionnelles - Harokokin aiki : dukan ayyukan da suka shafi wata sana'a.

Actualité : Al'amurran yanzu : dukan abubuwan da ke wakana a halin yanzu. Sauraren labari bisa al'amurran yanzu.

Ad'hoc : Na masamman : datacce, wanda ya zo daidai da halin da ake ciki. An kafa wani kwamiti na masamman don sassanta ɓangarorin biyu.

Adage : Salon magana : Kalami da ya d'auko tushe daga shari'ar gargajiya ko ta zamani. Wani salon magana ya ce : Duk wanda ya taka doka, doka na taka shi.

Adaptation : Daidaita : dacewar wani abu da wani hali. Sake tsarin koyarwa a Nijar na bukatar a daidaika tsare-tsaren koyarwa su dace da al'adun kasa.

Adapter : Daidaitawa : maidawa daidai da ... Ya kyauta a daidaita tsare-tsaren koyarwa su dace da al'adun kasa.

Adapter aux exigences de la situation : Daidaitawa da yadda hali ya yi : maida wani abu ya dace da halin da ake ciki.

Adéquat : Datacce : wanda ya yi daidai. Datattar shawara

Adhésion : Goyon baya : 1.) Yarda da wani ra'ayi ; goyon bayan wata yarjejeniya. 2.) Shiga cikin wani bangare. Goyon bayan da mutane suka kawo wa jam'iyyar, ya ba ta damar kahuwa cikin jahar.

Administrateur : Mahukunci : Wanda ke kula da tafiyar da ayyukan wani kampani ko wata ma'aikata. Ya kamata mahukunta su rika sauraren kukan talakkawansu.

Administratif : Na hukuma : wanda ya shafi hukuma. An aika takardun aiki na hukuma a ofushi minista.

Droit administratif : Ilimin dokokin aikin hukuma : dukan ka'idodin tafiyar da ayyukan hukuma.

Division administrative : Tsarin hukumomi : Kafa yankuna, jahohi, lardina, gundumomi da sauran su a cikin kasa.

Administration : Hukuma : dukan ma'aikatun gwamnati. Kauyace harakokin siyasa a cikin ma'aikatun gwamnati na kawo cikakken tattalin dukiyar kasa.

Administration civile : Hukumar farar hula : tsarin iko inda farar hula ke tafiyar da harakokin kasa.

Administration coloniale : Hukumar yan mulkin mallaka : tsarin iko inda yan mulkin mallaka ke tafiyar da harakokin kasa.

Administration militaire - Hukumar soji : Tsarin iko inda sojoji ke tafiyar da harakokin kasa.

Administré : Talakka : wanda ke bin wata hukuma. Talakkawa sun yi wa magajin garin jaharsu kyakkyawa tarbe.

Administrer : Hukunta : Jagaranta, tafiyar da harakokin kasa ko na masu zaman kansu. Magajin gari ke hukuntar garin.

Adapter : Amincewa : yarda ta

hanyar jefa ƙuri'a. Majalisar dokoki ta amince da doka mai kawo sauyi ga matsayin ma'aikatan gwamnati a ranar 7 ga watan Apirilu 1999.

Adoption : Amincewa : yarda ta hanyar jefa ƙuri'a. Majalisar dokoki ta yi zaman taronta don amincewa da doka mai lamba 98-12 kan sabon tsarin bayar da ilimi da horo.

Adresse : Adireshi : tabbatacciyar hanyar saduwa da wani. Sauya adireshi.

Affaire : Haraka : 1.) dalilin yin shari'a. An tsayar da shi saboda wata harakar cin dukiyar ƙasa. 2.) dukan harakokin kuɗi, da na masana 'antu, da na kasuwanci kasuwanci, cibiyoyin harakoki ne.

Affaire nationale : Harakar ƙasa : dukan abubuwan da suka shafi ƙasa.

Affaire publique - Harakar jama'a : dukan ayyuka na amfanin jama'a.

Affecter : Keɓewa/tadawa : 1.) Keɓewa. Gwamnati ta keɓe wa ma'aikatar ministan kyautata rayuwar al'umma maguɗan kuɗi. 2.) **Tadawa :** sake wurin aiki. Kowace shekara ana tada malaman makaranta.

Affiche électorale : Liƙe-liƙen yaƙin neman zaɓe : Takarda mai rubutu, da yadi mai tambari da launin jam'iyyar siyasa da ake liƙawa don pargagandi. A lokacin yaƙin neman zaɓe, ana ganin liƙe-liƙen yaƙin neman zaɓe ko'ina cikin gari

Affilier : Shiga : goya baya, zama mamba. Kungiyar ƙwallon ƙafa ta Nijar ta shiga cikin FIFA. (Kungiyar ƙwallon ƙafa ta duniya).

Affinité : Kusanta : kama, dangantaka, zumunci. Jam'iyun siyasa masu kusantar juna sun haɗa gwiwa.

Affirmation : Tabbaci : sanarwa mai haƙiƙanta gaskiyar wani abu. Shugaban jamhuriya ya bada tabbacin shirya zaɓe na ƙananan hukumomi.

Affirmer : Tabbatar da : haƙiƙantar da, dimantar da. Ministan ma'aikata ya tabbatar da niyyarshi ta aiki da ƙungiyoyin ƙwadago.

Affront : Cin zarafi : cin mutunci, zagi. Cin zarafin wani.

Africain : Ɗan Afirika : Na Afirika. Shugabannin ƙasashen Afirika na kira ga ƙasashen duniya da su ba su hannu don kawar da yaƙe-yaƙen da ke addabar nahiyar.

Afrique : Afirika : Ɗaya daga cikin nahiyoyi biyar (5) na duniya inda baƙaƙen mutane suka hi yawa. Afirika ce tushen ɗan Adam.

Age de la retraite : Shekarun ritaya : wa'adin da doka ta tsayar na barin aiki ga ma'aikaci.

Kayyade shekarun ritaya.

Age nubile : Shekarun aure : Karshen balaga. Cikin kauyuka, ana yin aure kahin shekarun aure su cika.

Agence : Kungiya : ma'aikata mai kula da wani aiki na masamman ; kungiyar kasar Nijar mai kula da samar da aiki, ita ke duba takardun marasa aiki.

Agent : Ma'aikaci : ma'aikacin gwamnati ko ma'aikaci mai zaman kanshi. Ma'aikatan gwamnati sun tsunduma cikin yajin aiki saboda rishin albashi.

Agglomération : Cinkoso : rukukin gidaje. Y'an cin rani suna kawo cinkoso cikin birane.

Aggravation : Tsanani : Karin karhin hukunci. Abun da ke kara karhin hukuncin wani laihi. Noman tserewa (gudu) daga gidan kaso ya kawo tsanani ga hukuncinshi.

Aggravation de la situation sociale - Tsananin halin rayuwa : gurbacewa/lalacewa/ tabarbarewar halin rayuwa.

Aggraver : Tsanantawa : Kara hukunci. An tsananta hukunci saboda rishin ladabi ga malamin shari'a

Agissement : Tashin hankali : abubuwan da ba su dace ba. Tashin hankalin da y'an makaranta suka yi ya rikita zirga-zirga a cikin birnin Yamai.

Agitation : Tashin hankali : Tarzoma, zanga-zanga, tashin hankalin al'umma. Y'an tarzoma sun kona tayoyi kan tili.

Agiter : Tada hankali : yin tarzoma, bayar da tsora. Yajin aikin da kungiyar kwadago ke shirin shiga, ya tada hankalin hukuma.

Agrément : Izini : amincewa daga wajen wata hukuma, yarda. An haramta sayo bindiga in ba da izinin ministan cikin gida ba.

Agression : Hari : Kai wa wani bugu ko cin mutuncinshi. Wad'ansu mutane da ba a san ko su wa ne ne ba sun kai wa y' an adawa hari. 2.) Kai farmaki maras hujja ga wata kasa. Y'an kasa sun nuna kishin zucci lokacin da sojojin haya suka kawo wa kasarsu hari.

Agricole : Na noma : mai yin noma, da ya shahi noma. Nijar kasa ce ta noma.

Agro-pastoral : Na noma da kiwo : abun da ya shahi noma da kiwo. Kasar na dogara ga arzikinta na noma da kiwo.

Aide publique : Taimakon kasa : agaji, gudunmuyar kud'i ko ta kayan aiki da ake bai wa wata al'umma. Bai wa kasa taimako.

Avis : Yanki : wuri, waje, hilin da aka kebe don yin wani abu. An kebe wani yanki na aje motoci gaban ma'aikatar.

Aire culturelle : yanki na wata al'ada : wajen da ake yin wata al'ada.

Aire géographique : yankin ƙasa : ƃangare na faɗin ƙasa.

Aire linguistique : yankin ƙasa inda wani ko wasu halayen harsuna ke bayyana.

Ajournement : Ɗagin rana : gusa rana, maidawa har wata rana. Rishin shaidu ya kawo ɗagin ranar shari'a.

Alarme : Karaurawa : sanarwa a game da zowar wani hatsari. Ko da aka kaɗa ƙaraurawa, sai yan zanga-zanga suka watse.

Aléa : Haɗari : abun da ke faɗowa kwatsam ; abun da ba a zato. Wannan harakar tana da haɗari.

Aléa climatique : Haɗarin yanayi : canje-canjen yanayi da ba a zato.

Aliénation : Sakin hakki : Kyauta, taimako, barin hakki. Ya saka wa yaron da ya yi riƙo wasu daga cikin dukiyoyinshi.

Aliénation culturelle : sakin al'adu : barin al'adu, yadda al'adu.

Alignement : Biya : goyon baya, gasa, kwaikwayo. Tsarin tattalin arzikin ƙasa yana biyar na ƙasashe maƙwabta

Alinéa : Mataki : sakin layi. Mataki na 1 na ayar doka ta 17 ta usular Afirika bisa hakkin ɗan Adam da na al'ummomi, ya ce : Samun ilimi da horo yanci ne na kowane ɗan Adam».

Allégeance :*Girmamawa : nunin goyon baya, nunin biyayya. Ya kamata yan ƙasa su girmama ƙasarsu.

Allègement : Sassauci : ragin nauyi. Ƙasashe masu tasowa sun roƙi gungun ƙasashe 7 ma fi arziki, da su yi masu sassauci a game da basussukansu.

Alliance : Haɗin gwiwa : haɗin kai, yarjejeniya, ƙawance. Haɗin gwiwar da jam'iyun 2 suka yi, ya ba su damar lashen zaɓe.

Allocution : Jawabi : taƙaitaccen bayyani da hukuma ke ambatawa a wani hali. Shugaban jamhuriya ya ambata wani jawabi a lokacin buɗe taron majalisar dokoki.

Alphabétique : Na abacada : Mai bin jerin haruffan abacada. Jerin sunayen yan takara ya bi tsarin abacada.

Alphabétisation : Yaƙi da jahilci : aikin koya karatu da rubutu ga waɗanda ba su san baƙi ba. Tsare-tsaren aikin yaƙi da jahilci sun kawo ragewar mizanin jahilci.

Alternance : Sauyi : yawan juyi tsakanin abu biyu (2) ko hiye. Sauyi dangance da demokaraɗiya.

Alternance politique : Sauyin mulki : juyin ragamar iko tsakanin jam'iyun siyasa biyu (2) ta hanyar zaɓe.

Ambassade : Ofushin jakadanci : wakilci na yau-da-kullum

na wata ƙasa a wata ƙasar waje. Ya je ofushin jakadancin don neman "biza".

Ambassadeur : Jakada : Wakilin yau-da-kullum na wata ƙasa a cikin wata ƙasar waje ko a wata ƙungiyar ƙasashen duniya. Jakada ya miƙa takardunshi na jakadanci ga shugaban jamhuriya.

Ambition : Guri : Son samu, kuri. Ɗaukar guri

Amélioration : Kyautatawa : gyara, maidawa na ƙwarai. Kyautata halin rayuwar al'umma na sa ci-gaban ɗan Adam.

Aménagement : Gyara : Mataki na masamman, shakka ko wani sauyi da ake kawowa ga wata doka. An kawo wa doka gyare-gyare.

Aménagement du territoire : tsarin ƙasa : kalkasa ayyukan tattalin arziki cikin faɗin ƙasa dangane da albarkatun ƙasa da ma'aikata.

Aménagement hydro-agricole : Gandari : hili inda ake noman rani.

Amendement : Cin gyara : gyaran huska da ake ma dokar da za a miƙa wa majalisar dokoki ; kyautatawa. Majalisar dokoki ba ta amince ba da cin gyaran da y'an ƀangaren adawa suka yi.

Amitié : Aminci : shiri. Hulɗa tsakanin ƙasashe biyu (2) ta ƙarfafa amincinsu.

Amnistie International : Kungiyar duniya ta ahuwa : ƙungiya ce ta duniya da ta kewaye wa siyasa, mai lura da halayen take hakkin ɗan Adam. Kungiyar duniya ta ahuwa ta yi Allah waddai da gallazawar da aka yi wa y'an kason ra'ayin siyasa.

Amnistie : Ahuwa : doka mai soke wani hukunci. An yi wa y'an kaso ahuwa.

Amorce : Farko : fari, somawa. An samu matsaloli tun farkon mahawarar majalisar dokoki.

Ampleur : Kamari : bunƙasa girma, Al'umurra sun yi ƙamari cikin ƙasa.

Ampliation : Ruƀi : batagwayyar takardar farko a ma'aikata. Ruƀinyawa.

Amplifier : Fifitawa : ƙarawa, labarun ƙarya da y'an jarida suka bayyana, sun fifita al'amarin.

Amputation : Yanka : datsa, ɗiba. Ma'aikata ba su amince ba da yankan kuɗinsu da aka yi.

Analphabète : Jahili : wanda bai san baƙi ba, wanda bai iya karatu da rubutu ba. Yawancin al'ummar Nijar jahilai ne.

Analyse : Nazari : binciken wani al'amari. Halin siyasa a Nijar yana buƙatar a yi cikakken nazari kan shi.

Anarchie : Rugumutsi : hargitsin da ga hito daga rishin

iko. Jahar tana huskantar rugumutsi.

Animation : Faɗaka : hanyoyi da dubaru da ake amfani da su don jayo hankalin mutane da waye kansu. A wuraren yaki da jahilci ana faɗakar da mutane kan ciwon SIDA.

Annexe : Rataye : mataki na ƙari, na ciko. Rataye ga doka

Annexer : Mamayewa : mayar da a ƙalƙashin mulkinsa. Kasar Irak ta mamaye ƙasar koyait a ranar 2 ga watan Agusta 1990.

Anniversaire : Cikon shakara: ranar zagayowar shekara ko shekaru ta wani al'amari da ya faru. Kowace rana ta 9 ga watan Faburari 1990, ranar cikon shekara ta kashe wasu yan makaranta, ƙungiyarsu na nuna bakin cikinta.

Anniversaire de la prise du pouvoir : Cikon shekarar ɗaukar mulki : bikin tuna ranar ɗaukar mulki.

Annonce : Sanarwa : shaidawa. Sanarwar tsagaita wuta tsakanin gwamnati da yan tawaye ta sanyaya zukatan jama'a.

Anomalie : Kuskure : abun da bai yi daidai ba, da ya kyauce wa ƙa'ida. An gano kurakurai da dama cikin wallafa kundin.

Anonymat : Boyon suna : Halin, ƙin bayyana suna, hali inda ba a san wanda ya aikata abu ba. Lokacin da ya yi magana ya so a ɓoye sunanshi.

Apanage : Gatanci : mallaka. Babu jam'iyar siyasar da za ta nuna gatanci a game da kahohin labaru.

Apartheid : Wariyar launin fata : bambancin launin fata a Afirika ta kudu. Wariyar launin fata, cin zarahin ɗan Adam ne.

Apatride : Maras matsayin ɗan ƙasa : Wanda ba ya da takardun matsayin ɗan ƙasa. An kore maras matsayin yan ƙasa.

Appareil : Tsarin ayyuka : dukan abubuwan da ke taimakowa don cimma wani guri. Ya kyauta gwamnati ya rika lura da yadda tsarin ayyukan hukuma ke tafiya daidai.

Appareil administratif : Tsarin ayyukan ma'aikatu : dukan matakan da ke kawo tsari cikin tafiyar da ayyukan ma'aikatu.

Appareil repressif : Tsarin ayyukan ban tsoro : dukan kayan aiki da mutanen da ake amfani da su don bada tsoro.

Apparence : Alama : Kamannun wani abu ko na mutum. Nuna alamar banza.

Appauvri : Talautawa : Maidawa matalauci. Rikice-rikice sun talautar da ƙasar.

Appauvrissement : Talaucewa : maidawa matalauci, halin wanda ya talauce. Talaucewar al'umma.

Appel : 1. Ɗaukaka ƙara : Kai kuka wajen hurumi na gaba da

nuna rishin amincewa da hukuncin da aka yanke ; hanyar tada shari'a. Babu damar d'aukaka ƙara bisa ga shari'ar da aka yanke.

2. Kira : gayyata. Gwamnati ta yi kira ga masu kyakkyawar niyya da su kawo ƙoƙarinsu.

Appel d'offres : Kiran kwangila : sanarwar da ake yi ga y'an kwangila don su nemi kwangilar.

Applicable : Mai aikatuwa : wanda ake iya aikatawa. Matakin da ake iya aiki da shi.

Application : Aiki da ... : halin aikatawa. Za a fara aiki da ƙudirin cikin wata mai zuwa.

Apport : Gudunmuwa : kawo ƙoƙari. Ginin ƙasa na buƙatar gudunmuwar dukan y'an ƙasa.

Appréhender : 1. Kamewa : tsayar da wani. Y'an sanda sun kame ɓarawo.

2. **Ganewa :** sani ta kan wani abu. Cikakken nazarin da aka yi kan al'amarin ya sa an gano matsalolin da ke kawo cikas cikin tafiyar da tattalin arzikin ƙasa.

Appréhender les réalités : Gane halayen da ake ciki : sanin halayen da ake ciki.

Approche : Hanya : husa'a, dubara, ra'ayi. Hanyar da kowa ke kawo ƙoƙarinsu.

Approprier : daidaitawa : kimantawa. Ya kyautu a daidaita kishin kud'i da halin tattalin arziki.

Approprier (1) : Mallakewa : mayar da abun wani naka

Appui : Taimako : gudunmuwa, agaji, goyon baya. Taimako wajen tafiyar da ci-gaban ƙasa. Taimako ga tsarin kalkasa mulki.

Aptitude : Iyawa : isa, ƙarhin yi. Iya amfani da y'ancinshi.

Apurement : Shahewa : shahe bashi

Arbitraire : Maras ƙa'ida : wanda babu gaskiya, Mulkin kama-karya, mulki ne maras bin ƙa'ida.

Arbitrairement : Ba ƙa'ida : ba tare da bin ƙa'ida ba, ba tare da bin gaskiya ba. An kama shi ba ƙa'ida a lokacin zanga-zanga.

Arbitre : Alƙali : wanda aka zaɓa don yanke shari'a bisa wata rishin jituwa. An zaɓi wata macce mai shiga tsakani tamkar alƙali don sasanta gwamnati da y'an adawa.

Ardent : Mai Kaifi : mai zafi, mai ƙarfi. Jawabi mai kaifi.

Arène : Fage : hilin jama'a inda y'an siyasa ke gwagwarmaya. Fagen siyasa.

Aridité : K'eƙasa : bushewar wuri, sallacewar wuri. K'eƙasar wurare.

Arme : Makami : abun da ake amfani da shi don kare kai, hujja. Hujjojin siyasa.

Arme de guerre : Makamin yaki : duk abun da ake amfani da shi wurin yaki. Makamin kare dangi, mummunan makamin yaki ne.

Armistice : Yarjejeniyar tsaida yaki : yarjejeniya mai nuna an jinginar da yaki. Rattaba hannu kan yarjejeniyar tsaida yaki.

Armoiries : Hatimi : Tambarin da ke bambanta kasa, ko wata zura'a. Hatimin jamhuriyar Nijar ya kunshi allon nan mai launin tsanwa da rana mai kyalin zinariya. Daga saman ranar a hannun dama, akwai mashi da takobi (2) a gilme. A hannun hagum akwai zangarniyar hatsi uku, d'aya a tsaye, biyu a gilme. Daga kasan ranar akwai kan saniya ; dukan su da kyalin zinariya. Allon na girke kan tuta hud'u na jamhuriyar Nijar. An rubuta «jamhuriyar Nijar» daga kasa.

Arrestation : Kamu : tsaida wani ta matakin shari'a ko y'an sanda. Y'an sanda sun kama wad'anda ake zargi.

Arrestation arbitraire : kamu maras hujja.

Arrêt : Hukunci : matakin shari'a da wani hurumi na gaba ya yanke. Wanda ya kai karan ya amince da hukuncin da kotin shari'a ya yanke.

Arrêté : Doka : matakin da hukuma ke d'auka don zartar da ayyuka. Ta hanyar doka ce ake yin tashe-tashen ma'aikatan gwamnati.

Arriéré : Bashi : kud'in da ba a biya ba a lokaci. Ma'aikata na neman a biya su bashin albashinsu.

Arroger (s) : Mallakewa : mayar da abun wani naka. Mallake iko.

Arrondissement : Gunduma : Yankin hukuma wanda yake tsakanin jaha da karamar gunduma. A Nijar, Suparepe ne shugabannin gundumomi.

Art : Dubara : husa'a, iyawa. Siyasa dubarar yaudara ce.

Article : Ayar doka : sashe mai lamba ko maras lamba na wani matanin doka. Matakan ayar doka.

Articulation : K'ididdiga : lissahi guda-guda na abubuwan da za a kai gaban shari'a. K'ididdigar abubuwan da suka sa kaiwar kara don kishin aure.

Artificiel : Na kirar d'an Adam : abun da d'an Adam ya kirkira. A kasar Libiya, akwai gulbi kirar d'an Adam.

Artisant : Mai aikin hannu : mutunen da ke yin aikin hannu da kanshi, wanda ya kera wani abu.

Artisant de la paix. Mai aikin wanzar da zaman lafiyar.

Artiste : Mai fasaha : wanda ke kera abun fasaha. Mai fasaha ya nuna wa jama'a abubuwan da ya kirkiro.

Artistique : Na fasaha : abun da ya shafi fasaha, abun da aka yi da kyau. Abu na fasaha.

Asile : Mafaka : inda ake iya samun malaɓa. mafakar siyasa.

Aspect : Huska : Kowane fanni inda ake iya duba wani zance. Ya kyautu a yi nazari ta kowace huska kan halin zaman rayuwa da halin siyasa a cikin ƙasa.

Aspects importants de la nation : Mahimman fannoni na ayyukan ƙasa : abubuwan da ke sahun gaba ga ƙasa.

Aspiration : Fata : maida dukan buƙatu wajen guri guda. Fatan kowace jam'iyyar siyasa na ta samu iko ne.

Aspiration légitime au progrès technique et scientifique : cikakken fata na buƙasa ilimin husa'a da na kimiyya : buƙatar bunƙasa ilimin husa'a da na kimiyya.

Aspiration du peuple : fatan al'umma : buƙata, guri na al'umma..

Assainir : Tsabtatar da : gyarawa, daidaitawa. Gwamnatin ƙasar Nijar ta ɗauki matakan tsabtatar da tsarin kashe-kashen kuɗin ƙasa don tada komaɗar tattalin arziki.

Assainissement : Tsabta : daidaita, gyara. Tsabtacewar tsarin kasahin kuɗi ya bada damar maido da bunƙasar tattalin arziki.

Assainissement budgétaire : tsabtacewar tsarin kasahin kuɗi : rage giɓi ga kasahin kuɗin ƙasa, sake daidaita halin kashe-kashen kuɗin ƙasa.

Assemblée : Majalisa : taron mambobin wata ƙungiya ko waɗansu mutane da ake gayyata don su yanke shawara bisa wasu ƙayyadaddun harakoki. Kiran taron majalisa.

Assemblée constituante : Majalisar tafiyar da tsarin mulki : majalisa mai izinin kafa tsarin mulki ko cin gyaranshi.

Assemblée constitutive : Majalisar tsarin mulki : majalisa mai hakikanta yanci.

Assemblée consultative : Majalisar ban shawara : majalisa mai bada shawarwari bisa abubuwan da suka shafi aikinta.

Assemblée exécutive : Majalisar zartarwa : majalisa mai kula da zartar da dokoki.

Assemblée extraordinaire : taron majalisa na masamman : taron gaggawa na majalisa.

Assemblée générale : Babban taro : taron da ya shafi yawanci ko dukan mutanen wani rukuni.

Assemblée législative : Majalisar binciken dokoki : majalisar dokoki : majalisa mai kafa dokoki cikin ƙasa.

Assemblée ordinaire : Kayyadadden taron maja-

lisa : zaman taron da majalisa ke yi a lokuttan da doka ta tsaida.

Assemblée plénière : Babban taron majalisa : zaman taron majalisa mai haɗa dukan mambobin da ta ƙunsa.

Assemblée populaire : taron al'umma : taron da kowa da kowa ke halarta.

Assemblée communale : Majalisar gari : majalisa mai kula da kafa dokoki cikin gari.

Assemblée départementale : majalisar ƙaramar jaha : majalisa mai kula da kafa dokoki cikin ƙananan jahohi.

Assemblée régionale : Majalisar jaha : majalisa mai kula da kafa dokoki cikin jaha.

Assentiment : Amincewa : yarda, na'am, samun shiga. Takardunshi sun samu amincewar kwamiti mai kula da bayar da alawus ɗin ɗalibai don ci-gaba da karatunsu.

Assiéger : Mamayewa : kamewa, yayyabewa. leburori sun mamaye ofushin shugaban ma'aikata.

Assiette imposable : Lanho : jula. Ya kamata a sassauta wa yan kasuwa lanho don su samu ƙarhin kafa masana'antu.

Assignation : Ɗauri : Kamu, gabatar da mutum gaban shari'a. Kungiyar kare hakkin ɗan Adam ta yi Allah waddai ta ɗaurin da aka wa maduggan yan adawa.

Assignation à résidence : Ɗaurin talata : tilasawa wani kar ya huta daga gida ko daga garin da yake.

Assigner : Ɗaurewa : Kamewa, gabatar da mutum gaban shari'a. Ɗaure mutum.

Assimilation : Rikiɗa : sawaya, ɗaukar kama. Yan gudun hijira sun rikiɗa cikin al'adun ƙasar da ta karɓe su.

Assise : Girkuwa : suna, yin sayu. Jam'iyyar ta samu girkuwa da kyau.

Assistance : Taimako : gudunmuwar da ake samu ko ake bayar. Ƙasashen Afirika na buƙatar taimakon kuɗi da na ilimin husa'a da tayar da komaɗar tattalin arziki.

Assistance sociale : Taimakon al'umma : gudunmuwar da ake bai wa wani ko wasu mutane da ke cikin halin ƙaƙa nike.

Assistance technique : Taimako na ilimin husa'a : gudunmuwar ƙasashen duniya ga ƙasa mai tasowa.

Association : Kungiya : haɗin gwiwar mutane cikin wani tsari don cimma wani guri. Kafa kungiya.

Association locale des coopératives : Haɗin gwiwar kungiyoyin gari : haɗin gwiwar masu sarrafawa, da masu saye, da masu saidawa na gari.

Association socio-culturelle : Kungiyar yaɗa al'adu : mutanen da ke haɗuwa cikin wani tsari don yaɗa al'adun gargajiya.

Association socio-professionnelle : Kungiyar ma'aikata : haɗuwar mutane masu aiki iri ɗaya cikin wani tsari don kare hakkin mambobinsu.

Association de défense des droits de l'homme : Kungiyar kare hakkin ɗan Adam : mutanen wani tsari masu kula da kare hakkin ɗan Adam.

Association de développement : Kungiyar neman ci-gaba : haɗuwar mutane cikin wani tsari don neman ci-gaba.

Assumer : Cikawa : ɗauka a kai, ɗaukar nauyi. Cika wani aiki.

Assurance : Tabbaci : alkawali, dimun. Shugaban ƙasa ya bayar da tabbacin shirya zaɓe maras gardama.

Assurer : Tabbatawa : hakikkantawa, dimuntawa. Minista ya tabbatar wa ƙungiyoyin ƙwadago da za ya aiki da su hannu cikin hannu don shawo kan matsalolinsu.

Atelier : Taron ƙara wa juna ilimi : taron aiki. An shirya wani taron ƙara wa juna ilimi na ɗan jarida.

Athéisme : Kafurci/mulhidanci : tabi'ar wanda bai san da Allah ba.

Atout : Alheri : mai amfani, sa'a. kawo haske cikin harakokin zaɓe, abun alheri ne na zaɓe ya yi kyau.

Attaché : Wanda aka aika : mutumen da aka maida wata ma'aikata. Ɗan jaridar wata ma'aikata.

Attachement : Bada gaskiya : Ƙamna, so, shaƙuwa. Magoya bayan jam'iyar sun bada gaskiya ga gurorin jam'iyyarsu.

Attaque : 1. Farmaki : hari. Kai farmaki da makamai.

2. **Zargi :** Ƙaƙe. Ɗan adawa sun mayar da martani bisa kan zargin da gwamnati ya yi masu.

Atteinte : Taki : Kawo asara, cin mutunci, ƙeta, saɓa wa... Taka ɗanci.

Atteinte à la sureté de l'état : Ketatar ƙasa : saɓa wa amfanin ƙasa.

Atteler (s') : Mayar da hankali : mayar da himma, da ƙoƙari. Gwamnati na mayar da hankali cikin tahiyar da tsarin sayar da kampanoninta.

Attestation : Shaida : abun da ke nuna wani tabbaci, hakikanci, gaskiya. Shaidar cin wata nasara.

Attirer : Jawowa : Tunzurawa, kira. Jawo mutane

Attitude : Hali : yadda mutum ke zama da sauran mutane, tabi'a. Samun kyakkyawan hali.

Attribut : Na ƙashin kai : abun da ya shafi mutum shi ɗaya ko masamman wani abu. Abun da ke bambanta shi. Iko na ƙashin kan shugaban ƙasa.

Attribution : Iko/bakin iko : yanci. Kayyade bakin ikon paraminista.

Audience : 1. **Shari'a :** zaman shari'ar wani koti. Shari'a ta gaban jama'a.

2. **Tattaunawa** da ake samun yi da wani babban mutum neman tattaunawa da wani babban mutum.

Audio-visuel : Gani-da-ji : haɗa sauti da hotuna cikin dubarun sadarwa. Hanyar gani-da-ji (hanyar radiyo-mai-hoto)

Augmentation : Ƙari : haɓaka, kyautatawa. Ƙarin albashi.

Augmentation des revenus : Ƙarin amfani : kyautatata abun da ake samu.

Auguste : Mai daraja : wanda ake girmamawa. Majalisa mai daraja.

Auspices : Jagoranci : taimako. An samu damar zaman sasantawa tsakanin gwamnati da yan tawaye a ƙalƙashin jagorancin masu shiga tsakani na ƙasashen waje.

Austérité : Tsauri : Sa tsauri cikin tafiyar da tattalin arziki.

Authentique : Na ainahi : abun da babu wata gardama kan tushenshi, asulinshi. Don samun damar jefa ƙuri'a, ya kyautu kowane ya zo da takardarshi ta ɗan ƙasa ta ainahi.

Auto-actualisation : Aiki da zamani : tafiyar da harakoki kamar yadda lokaci ya bayar. Aiki da zamani na matsalolin tattalin arziki, yana na buƙatar ƙasa ta sa tsauri cikin tafiyar da ayyukan tattalin arzikinta.

Auto-détermination : Niyyar kai : yancin zaɓen hanyar siyasa ko ta tattalin arzikin ƙasa daga yan ƙasar.

Auto-développement : Bunƙasa kai : zaɓen hanyar ci-gaba da kansa.

Auto-encadrement villageois : Horon juna na gari : horon da mutanen gari ke yi wa junansu, ƙaruwa da juna.

Auto-évaluation : Auna kai : hanyar da wani kampani ko wata ƙasa ke bi don ganin iyakar ƙarfinshi ko ƙarfinta.

Auto-gestion : Tattalin kai : tattalin da mutane ke yi wa hukumarsu.

Auto-suffisance alimentaire : Halin ciyar da kai : halin wata al'umma ko wata ƙasa mai isassun albarkatu na biyan buƙatunta wajen cimaka ba tare da ta nemi taimako daga ƙetare ba.

Autonome : Mai yancin kai : mai mulkin kanshi, wanda ba a iya

tilasa wa abin da bai so ba. Nijar ƙasa ce mai y'ancin kanta

Autonomie : Y'ancin kai, cin gishin kai : y'ancin kai, y'ancin kafa dokarshi ta kanshi.

Cin gishin kai : Sabon tsarin jahohin ƙasa na bai wa jahohin damar cin gishin kansu cikin tafiyar da aikinsu.

Autonomie financière : Y'ancin kai, cin gishin kai a fannin kuɗi : cin gishin kai wajen tafiyar da harakokin kuɗi.

Autonomie de gestion : Y'ancin kai na hukuma : Cin gishin kai wajen tafiyar da tsarin hukuma

Autorisation : Amincewa : Bayar da dama, yardewa, tarkardar shaida. An amince wa y'an ƙwadago da su gabatar da zanga-zangarsu.

1.) Autorité : Iko : tsari mai sanya ladabi, da darattawa, hukuma ; ikon shugaban ƙasa.

Organes du pouvoir : hukumomi. Hukumomin jahohi na aiki da umurnin da aka ba su.

Autorité administrative : mahukunci : Ma'aikacin gwamnati mai gudanar da hakumanci.

Autorité coutumière : hukumomin gargajiya : Sarakan gargajiya

Autorité du barrage de kandaji : ma'aikatan gandari na garin kandaji : Ma'aikata masu kula da tsarin tafiyar da gandarin kandaji.

Autorité du liptako Gourma : Ma'aikatan liptako Gurma : ma'aikata masu kula da tafiyar da aiki a Loptako-Gurma.

Autorité politique : mahukunta masu tafiyar da hukumanci

Autorité publique : mahukuntan ƙasa masu kiyaye doka.

Auxiliaire : Ƙaramin kwami : mataimaki, ma'aikacin da ake ɗauka a ƙayyadadden lokaci, mutanen da ke bayar da hannu, wanda bai kai matsayin saura ba, mafi ƙaramin matsayi. An aza wa ƙananen kwamumuwa nauyin tafiyar da aikin.

Auxiliaire de justice : Mataimaki a fannin Shari'a : masanin shari'a, mai bayar da hannu cikin tafiyar da harakokin shari'a.

Aval : Amincewa : goyon baya, tabbaci, yarda. Nuna amince-warsa ; bayar da yardarsa

Avancement : Karin girma : ɗaukakawa, ci-gaba, ingantawa. Ya samu ƙarin girma na musamman.

Avant projet : Shire-shiren wani abu : rubuta wani tsarin doka da ba na dindindin ba, ko na tsarin mulki, ko na wata yarjejeniya. Bincikar wani tsarin doka.

Avantage : amfani : riba, alheri cin amfanin wani abu.

Avec détermination : Tare da cikakkar niyya : da hima, da ƙwazo, cikin tsayin daka, da zuciya guda, da cikakkar yarda. Sojin ya sanya cikakkar niyya wajen kare ƙasarshi.

Avènement : Shigowa : zowa, isowa shigowar mulkin demokaraɗiya a ƙasar Nijar.

Avenir : Makoma : halin zuwa gaba, ƙarshe. A cikin mafi yawan ƙasashe masu tasowa, makomar matasa tana cikin duhu.

Aventure : Yawan dandi : abun da ba a san yadda zai ƙarewa ba. Shiga uwa duniya, ba duniya gaba shiga yawan dandi.

Avilir : Wulaƙantar da : Cin mutunci, kunyatar da. A cikin waɗansu gidajen kaso, abubuwan da ake yi wa ɗan kaso, na wulaƙantar da su ne.

Avis : Ra'ayi : Abin da mutum ke tsammani kan wani abu, shawara.

2) **Yanke shawara** : ra'ayi mai zaman shawara.

Kwaƙƙwaran ra'ayi : girkaken ra'ayi mai hujja.

Avocat : Lauya : mutunen da ke cikin tsarin lauyoyi, kuma yana bayar da shawara kan fannin shari'a, ko a game da wata rishin jituwa, kuma yana kariyar mutane a gidan juju. Wanda aka kama da laifi ya buƙaci gudun-muwar lauya don shi kare shi.

Lauyan koti : lauya mai kariya, mai shiga tsakani.

Babban lauya : lauya mai taimaka wa shugaban kotin ƙoli, kuma mai iya zama muƙaddashinshi

Lauyan da ke cikin ƙungiyar ƙasa da kotin tayar da ƙara : Lauya mai kula da kariya, da agaza wa waɗansu ɓangarori gaban ƙungiyar ƙasa da kotin tayar da ƙara.

Avoir la main mise sur : Samun hannu cikin wani abu : yin kane-kane cikin wani abu, mallaka. Kungiyar zaɓe ta ƙasa na da hannu dumu-dumu cikin tafiyar da tsare-tsaren zaɓe.

Axe : Hanya : manufa, hanyar da aka tsaga wa wani abu. Hanyar siyasar Nijar ta dogara kan cewa ci-gaban ƙasa mai tasowa daga yunƙurin al'ummarta yake.

B

Bailleur : Masu bada lamani : mutum, ko wata kungiya mai bada rance, ko mai yin tallafi. Kungiyoyi masu bayar da lamani sun amince da su sake kulla huldɗa da Nijar.

Balance : Halin daidaici : halin daidaitar wani abu, sakelu. Fasalin kasuwancin Nijar gurguntacce ne.

Balance de paiement : Rarar ciniki : kundi mai kumshe da yarjejeniya daban-daban ta kasuwanci tsakanin kasa da kasa.

Bannière : Karkashi : zama kasan wani : zama karkashin wani.

Bannir : Haramtawa : Yardawa, tilasa wa mutum da ya bar kasa da sharaɗin kar ya sake sanyo kafa cikin ta. Haramta wa mutum zama cikin wata kasa.

Banque : Banki : ma'aikatar da ke kula da adano, da kuma kuɗin da mutane ke kaiwa ajiya. Ya buɗa asusu a banki.

Bankin kasashen Afirka ta yamma : ma'aikata mai kirkira kuɗi, kuma ta tafiyar da tsarin harakokin kuɗi a kasashen Afirka ta yamma.

Barrage : Shinge : abun da ke tarewa, yin banga-banga, adawa. yan adawa a majalisar dokoki sun yi shinge a game da doka mai kawo canji a cikin ma'aikatun gwamnati.

Bas niveau de vie : Mawuyacin halin rayuwa : rayuwa mai wahala. Talakkawa na fuskantar matsaloli da yawa saboda mawuyacin halin rayuwar da suke ciki.

Base : 1/ Magoya baya : Dukan magoya bayan wata jam'iyar siyasa, ko sandika, ko wata kungiya. Magoya bayan jam'iyyar sun yi allawadai da shawarar da magabatansu suka gabatar masu.

2) **Matakai** : sabbin hanyoyi, madogara. An ɗauki sabbin matakai don sake komawa zaman tattaunawa. **Matakai na gari** : hanyoyi na kwarai, na kirki.

Bataillon : Bataliya : rundunoni soji da suka kumshi sojojin kasa, da sojojin lema da kuma waɗansu sojoji can daban ; shugaban bataliya.

Bâtir : Ginawa : aikata abin amfanin jama'a, tattali. Ya kyautu kowane ɗan kasa ya kawo gudun-muwarshi don gina kasar Nijar. Gina kasar Nijar.

Bâtir notre destinée commune : Kyautata makomarmu : gyara rayuwarmu, daɗaɗa rayuwarmu.

Bénédiction : Yarda : amincewa, Samun yardar wani

Bénéficiaire : Mai cin riba : mai cin gajiya, mutunen da ke cin amfanin wani abu, wani matsayi. Masu cin ribar makaranta.

Bénéficier : Amfana : samun sa'ar wani abu. Sun ci sa'a an saukaka masu

Besoin : Bukata : marmari, muradin abin da ke doli ; Bukatun talakkawa kan fannin abinci suna da yawa.

Bétail : Busashe : dukan dabbobin da ake kiyo. Kasar Nijar na fitar da busashe a kasashen waje.

Bien public : Dukiyar kasa : abun jama'a, na al'umma gaba d'aya. Bai kyautu ma'aikatan gwamnati su rika cin dukiyar kasa ba.

Bien être : Jin dad'in rayuwa : Cikakkar kwanciyar hankali da samun wadata a fannin lafiya da kuma fannin arziki.

Bien fondé : Kan gado : Wanda ya dace da doka, kan gaskiya. Roko mai kan gado.

Biens et services : Kayayyakin aiki : Dukan kayayyakin da ake amfani da su don tafiyar da wani aiki. Ya kyautu a yi tattalin kayayyakin aiki na kasa.

Bilan : Sakamako : Balas mai rara ko mai gibi na wani aiki. Ya kawo sakamako na gari bayan da ya ja ragamar harakokin.

Bilatérale : Na tsakanin bangare biyu : wanda ya shafi bangare biyu, soken mashi. Kasar Nijar ta sanya hannu kan wata yarjejeniya da makwabciyarta a game da abin da ya shafi tsaro.

Bloc : Gungu : had'in gwiwar jam'iyu, kawance. Jam'iyun siyasa na bangaren adawa sun had'u gungu guda.

Blocage : Kawo cikas : tarewa, hana ruwa gudu, takunkumi. Kawo cikas kan wani abu. **Dakatar da zuba jari :** tsayar da tallafi kan fanni kud'i, ko kayayyakin aiki.

Kawo cikas cikin tafiyar da aikin hukumomin kasa : hana ruwa gudu cikin tafiyar da harakokin kasa.

Blocus : Takunkumi : Mataki na tsabbace kasa, na ware kasa. Sanya wa kasa takunkumi.

Blocus économique : Takunkumin karya tattalin arziki : d'aukar matakin karya tattalin arzikin kasa.

Bon : Takardar izini : cikakkar shaida mai bai wa wani izini na aikata wani abu. Samun izinin d'auko kaya.

Bon de trésor : katin izini ta bitalmani : Kati mai canzuwa da kud'i da bitalmani ke bai wa mutum.

Bonheur : Farin ciki : cikakken jin dad'i, wadata, farin ciki. Fatan samun farin ciki.

Bonne gouvernance : Iko na adalci : gudanar da harakokin hukumanci kan gaskiya. Ya kyautu kowane gwamnati ya tafiyar da iko na adalci.

Boycott : Kauracewa : Yin ƙafar angulu ga harakokin kasuwancin mutum, ko na ƙasa, ƙin halartar wani abu. Kaurace wa zaɓe.

Boycotter : ƙwaurace wa : Yin ƙafar angulu cikin waɗansu harakoki. Y'an adawa sun ƙaurace wa zaɓe.

Brader : karyar da : sayar da abu a banzace, ƙaɗar da ; karyar da masana'antu.

Braderie : karyarwa : gwanjo, banzatar da, sayen wulaƙanci. Y'an sandika sun tashi tsaye kan niyyar gwamnati ta karyawar masana'antun ƙasa.

Brochure : Kundi (ƙasida) : ƙaramin littafi. Kundin wayar da kai (ƙasidar wayar da kai).

Budget : Kasashin kuɗi : Lissahin kuɗin da za su shiga, da waɗanda za su fita cikin asusun ƙasa a shekara. Kasahin kuɗin ƙasa.

Budget communal : Kasashin kuɗin kwamin : lissahin kuɗin da za su shiga da waɗanda za su fita cikin shekara a asusun kwamin

Budget départemental : kasashin kuɗin departama : lissahin kuɗin da za su shiga da waɗanda za su fita cikin asusun départama a shekara.

Budget régional : kasahin kuɗin jaha : lissahin kuɗin da za su shiga da waɗanda za su fita cikin asusun jaha a shekara.

Budget primitif : kasahin kuɗin shekara mai zuwa : lissahin kuɗi wanda ya ƙumshi kuɗin da za su shiga da waɗanda za su fita a shekara mai zuwa.

Budget supplémentaire : Karamin kasahin kuɗi : lissahin kuɗi masu kawo gyaren fuska cikin kashe-kashe kuɗi.

Bulletin : takardar shaida : takardar da ake bai wa masu amfani da wani abu.

Bulletin d'information : Hilin labaru : Taƙaitattun labarun yini da ake gabatarwa a gidan radiyo, ko a gidan radiyo-mai-hoto.

Bulletin de liaison : takardar dangantaka : tarkardar da ke taimakawa wajen ƙulla dangantaka da ci-gaba da yin ta tsakanin ma'aikatu daban-daban.

Bulletin de vote : takardar zaɓe : ƙuri'ar da mai zaɓe ke jefawa cikin akwati.

Bulletin nul : takardar zaɓen da ba ta cikin lissafi : ƙuri'ar da aka jefa ba kan ƙa'ida ba, wadda ke kawo ruɗani, ba a gane ma'anarta.

Takardar zaɓen y'an ban ruwanmu : ƙuri'ar da ake jefawa don nuna cewa zaɓen bai damu mutum ba.

Bureau : Buro : 1.) ma'aikata. Buron, ma'aikatar magajin gari.

Bureaucratie : tattara riko : tattare hakumanci cikin hannu mahukunta, ko cikin hannun jam'iyyar siyasa, ko cikin hannun wani kampani. Tattare iko cikin hannun mahukunta shi ne ya kawo sakaci cikin ma'aikatun gwamnati.

Bureaucratisation : halin tattare iko : kawo halin tare iko wuri d'aya. Halin tattare iko cikin ƙasa.

But : manufa : guri, abun da ake fatan cimma. Manufar yaki da jahilci ita ce ta taimaka wa dattijawa da su koyi karatu da rubutu.

But suprême : babban guri : gurin da mutum ya sanya sahun gaba.

C

Cabinet : Sashen ma'aikata (fada) : buro mai kula da shirye-shiryen takardu cikin ma'aikata.

Conseil de cabinet : Taron shawarar sassan ma'aikata.

Cabinet ministériel : sashen ofushin minista (fadar minista) : buron da ke kula da tsare-tsaren takardu a ma'aikatar minista.

Cadre : Babban ma'aikaci : ma'aikatan da suka samu dogon karatu, masu albashi mai tsoka.

Cadre moyen : matsakaicin ma'aikaci, madaidaicin ma'aikaci.

Cadre conceptuel : datattar hanya : hanyar da ake tsagawa don gudanar da wani tsari.

Cadre d'action : kayyadadden. Tsarin aiki : Shirin masamman da aka yi don gudanar da wani aiki.

Cadre juridique : fannin shari'a a fuskar shari'a, hanyar shari'a.

Cadre réglémentaire : Kan ka'ida : wanda bai kauce wa hanyar gaskiya ba, na daidai.

Caduc : Sokakke : wanda ya zama banza, wanda ba ya aiki. Sokakkar doka.

Caisse : Asusu : ma'aikata mai kula da adanon kudi, kuma ta kula da jujjuyawa.

Caisse de crédit : Asusun bayar da bashi.

Caisse d'épargne : Asusun tsimi : ma'aikatar kudi mai kula da ajiyar kudi bakin gwargwado kuma ; ta tsibe su, tana fitar da ribar adanon kowace shekara.

Caisse de compensation : asusun ciko : ma'aikatar kudin da ake aza wa nauyin kawo ma jama'a agaji.

Caisse de sécurité sociale : asusun kyautata dadin rayuwar jama'a : ma'aikatar kudi mai kula da tabbatar da jin dadin rayuwar jama'a.

Caisse de stabilisation des prix : Asusun daidaita farashi : ma'aikatar kudi mai kula da daidaita farashin kayayyaki a cikin kasa.

Caisse nationale de crédit agricole : Asusun bai wa manoma bashi : ma'aikatar gwamnati mai bai wa manoma tallafi.

Caisse Française de développement : Asusun yan kasar faransa don ci-gaba. Kungiya mai bayar da agaji.

Caisse Populaire d'Epargne et de Crédit : Asusun jama'a na tsimi da bayar da bashi : asusun da yan kasa ke ajiyar

kuɗi, kuma su samu damar cin bashi.

Caisse de Prêts aux Collectivités : Asusun bashi na ƙananan hukumomi : ma'aikata mai bayar da bashi cikin ƙananan hukumomi da jahohi.

Calamité : Jaraba : masifa, bala'i. Jarabar duniya.

Calomnie : tsegumi : Ɓata mutum, gulma, ɓata sunan mutum. Farin jininshi ya rage a game da tsegumin da aka yi ta yi kanshi.

Campagne : parpagandi : Yaƙin neman zaɓe : dukan kalamai na daɗin baki da ake yi don jawo hankalin jama'a don su jefa wa wani, ko waɗansu mutane ƙuri'unsu. Parpagandin zaɓe. Parpagandin siyasa. Yaƙin neman zaɓe.

Campement : zango : wurin da aka zauna ba da niyyar ɗore zaman ba ; rigga. Zangon makiyaya.

Canal : Hanya : dalili, da hannun wani. An aiko mashi wani ɗan ƙumshi ta hanyar gidan waya.

Candidat : Ɗan takara : mutunen da ke neman a zaɓe shi kan wani matsayi, ko wani muƙami. Shiga takarar zama dipite.

Candidat indépendant : Ɗan takarar indapenda : ɗan takarar da ke shiga neman zaɓe ba ƙarƙashin innuwar jam'iyya ko guda ba.

Canton : Karkara, kantoma : Yanki ne a cikin tsarin rarraba gunduma. Karkara na ƙumshe da ƙauyuyyuka da dama ko garuruwa.

Capacité : Iyawa/iyaka : ƙoƙari, ɗauka, ci. Bakin iyakar ganewar mutum.

Capital : 1/ Mahimmin : ginshiƙi, na sahun gaba. Ya bada mahimmin ƙoƙari wajen warware matsalar.

2) **Jari :** bakin gwargwadon kuɗin da kampani ke juyawa da su ; uwar kuɗi. Ya fara kasuwanci da jari mai ƙarfi.

Capitale : Babban birni : Birnin da gwamnati yake girke. Babban birnin wata ƙasa.

Capituler : Bada kai : Yin murabus, sallamawa. Bada kai gaban abokin hamayya.

Caractéristique : Alama : mai bambantar da, alama ce ta yankin yanayi mai zafi. (ikwata)

Carence : kasawa : rishin samun cika alƙawali, ko cika wani aiki. kasawar iko.

Carrière : Aiki : aiki mai hawa-hawa. Yin aiki kan fannin koyarwa.

Cas de forfaiture : Aikin almuzuranci : (almubazzanci), Maguɗi. halin tayar da alƙawali, abun kunya, ma'aikacin gwamnati da ake tuhuma da

aikata aikin almuzurauci cikin tafiyar da aikinshi. Ana hukunta ma'aikacin da ke aikata aikin almuzuranci (almubazzanci) ko magudi.

Cataclysme : Babban rugum: bala'i : girgizar ƙasa, asara mai biyo bayan girgizar ƙasa, ko wani iska mai ƙarfin gaske. Girgizar ƙasa.

Catégorie : Hayi/Kashi/iri/ matsayi : dukan mutane, ko waɗansu abubuwar masu hayi ɗaya.

Catégorie sociale : Matsayi cikin al'umma.

Catégorie principale : Hayin mutane masu muƙami : mutane masu babban matsayi, masu faɗi a ji.

Caution : Kuɗin tabbaci : kuɗin da mutum ke zubawa kahin ya shiga takara. Tsarin mulkin ya ƙayyade cewa kowane ɗan takara mai neman zama shugaban ƙasa sai ya zuba kuɗin tabbaci (garanti) har miliyan biyar.

Cellule de cordination : Cibiya : magama, ko reshen wata ƙungiya. Cibiyar jam'iyyar siyasa.

Cellule de coordination du programme de privatisation : Cibiyar tsarin yaye kamfanoni : reshen ma'aikata mai kula da tsara hanyoyin sayar da masana'antun gwamnati.

Censure : Rishin amincewa : Takunkumi : ƙuri'ar da y'an majalisa ke jefawa don nuna rishin amincewarsu, don nuna rishin ƙaunar gwamnati. K'uri'ar rishin amincewa da gwamnati.

Centralisation : Tattara wuri guda : gangamewar kayan aiki wuri guda. Tsaro a wuri guda. Y'an mulkin kama karya su ne suka shahara wajen tattara iko cikin hannunsu.

Centraliser : Tattarewa : gamewa wuri guda, dinkemewa. Tattare iko wuri guda.

Centre : Tsakar fage : tsakiya, muhimman abu, cibiya. A lokacin zaman taro na ƙasa kan fannin koyarwa, sake sabon tsari koyarwa shi ne tsakar fagen tattaunawa.

Centre de santé communautaire : Gidan likitar al'umma : ma'aikata mai kula da lafiyar jama'a.

Cérémonie : Biki : Shagulgullan nunin murna, ko jin daɗi ta hanyar shirya sabgogi. Mutane da yawa sun halarta wajen bikin buɗa taro.

Cérémonie solennelle : Babban biki : shagulgulla a bainar jama'a.

Certificat : Takardar shaida : takardar da hakuma ke bayar, mai gaskantar da wani abu.

Certificat médical : takardar binciken lafiya.

Certificat de jugement supplétif : takardar shaidar haifuwa : takarda mai zaman matsayin takardar haifuwa da ake bayar a gidan juju, a gaban shaidu.

Certificat de nationalité : Takardar shaidar ɗan ƙasa : takarda mai nuna mutum ya cika ɗan ƙasa.

Certificat de prise de service : Takardar kama aiki : takardar da ke nuna cewa mutum ya soma aiki a cikin wata ma'aikata.

Certificat de résidence : Takardar zaman gari : tarkardar da ke tabbatar da mutum na zaune cikin wani gari.

Certificat de vie et charge : takardar ɗaukar nauyi : takardar da ke tabbatar da yawan iyalan da mutum yake ciyar da su.

Cessation de fonction : Daina aiki : tsayar da aiki, barin aiki. Antare. Tun da ya daina aiki, ba ya yin komi sai kula da garkarshi.

Cessez le feu : tsagaita wuta : dakatar da bada wuta na wani ɗan lokaci kaɗan, tsayar da masanyar wuta. Sanya hannu kan yarjejeniyar tsagaita wuta.

Chambre administrative :

Champ de bataille : hilin daga : hilin da ake gobza yaki. Mutum ya mutu hilin daga.

Champion : 1) **Gwani** : mai kare wani abu. Gwannan girka kundin tsarin iyali cikin ƙasa.

2) **Zakara** : wanda ya ci galaba wajen waɗansu wasannin motsa jiki. Kantu ya zama zakaran ɣan kokowa a Nijar.

Championnat : gasar wasa : gasar wasa wadda a ƙarshe ake bai wa zakara tukwici. Gasar wasan ƙwallon kwando.

Chancelier : mai adanon hatimin ƙasa : mutunen da ke da nauyin adanon hatimin ƙasa. Janaral Ali Shaibu yana cikin tsarin masu adanon hatimin ƙasa.

Chancellerie : ma'aikatar mai adanon hatimin ƙasa : buro, hukumar adanon hatimin ƙasa.

Changement : Juyi : kamun ludai, sauyi. K'asar Nijar ta daɗe tana samun juyi kan fannin siyasa tun alif da ɗari tara da tasi'in (1990).

Chantier : hilin aiki : wuri inda aka tattara kayan aiki don gudanar da wani aiki.

Chapitre : kai : aji, ajin da ke bin juna cikin littafi ; rarrabe-rarraben kasahin kuɗin ƙasa

Charges de l'Etat : Nauyin da ya rataya wuyan gwamnati : abin da ya zama tilas ga gwamnati. Nauyin da ya rataya wuyan gwamnati yana da yawa.

Charte : Usula : mahimman ƙa'idodi na wata ƙungiya. Usular

majalasar d'umkin duniya usular kare hakkin d'an adam.

Charte de l'O.U.A. : Usular had'in kan afirka.

Châtiment corporel : duka : duka mai tsanani ; shan dukar tsiya, dukar mutum.

Chef : Shugaba : Wanda ke shugabanta, mai iko.

Chef coutumier : Sarkin gargajiya : hukumomin gargajiya.

Guri : dubarorin cimma wani guri, tata.

Paraminista : mai shugabantar gwamnati

Baruma : mai shugabancin gundumomi.

Chef de délégation : Shugaban tawaga : wakili, jagoran tawaga.

Chef de l'Etat : Shugaban ƙasa : mutunen da ke jan ragamar ƙasa.

Chef de personnel : Shugaban ma'aikata : ma'aikaci wanda ke da nauyin shugabancin sauren ma'aikata.

Sarki : wanda ke rike da sarautar gargajiya a cikin birni.

Chef de section : Shugaban sashe : jagoran jam'iya, ko sandika.

Chef de service : Shugaban ma'aikata : mai shugabancin ma'aikata

Chef de tribu : Shugaban ƙabila : mutunen da ke jagorancin ƙabilun da suka fito jaha guda.

Chefferie traditionnelle : Sarautar gargajiya : hukumancin gargajiya. Ana girmama sarautar gargajiya bakin gwargwado a ƙasar Nijar.

Cheptel : Bisashe : dukan dabobin da ake kiyo cikin jaha, ke cikin ƙasa. Fari ya kawo sanadiyar mutuwar bisashe da yawa.

Chiffres d'affaires : Cinaki : Cinakin da masana'antu ke yi a cikin tsawon wani lokaci. Dibar tara kan cinakin da ake yi.

Choix : Zabe : tankade da rairaye ; nuna abin da mutum ke so.

Chômage : Zaman rishin aiki : Halin wanda ba ya da aikin yi. Ya kyautu gwamnati ya d'auki matakai don kiyaye zaman rishin aiki.

Chronogramme :

Circonscription : Yanki : rarrabe-rarrabe cikin tsarin ƙasa. Yankin zabe. **Jaha** : yankin da ke karkashin wata hakuma.

1) **Circonstances : Hali** : Wani abu na musamman, abun da ke aukuwa. A halin yanzu, gwamnati ba ya biyan albashin ma'aikata. 2) Halin tsanantawa.

Circonstances atténuantes :

saukaka da ya kyautu a yi wa mutum. Saukaka d'armi.

Circulaire : Sanarwa : wasika, ko ra'ayin da hukuma ke gabatarwa, a rumbanya sanarwa da yawa don isar da wani labari.

Circulation : 1/ Yawo : watsuwa, zirga-zirga, halin abun da ake samu ko'ina, mai jujuyawa.

Takardun jarabawa suna ta yawo ko'ina kahin a yi jarabawar, a shekarun ba.

2) Dukan abin da ya shafi harakokin saye da saidawa, masanyar kayayyaki. Masanyar kayayyaki da walwalar mutane. **Watsuwar labari :** bayyana labari ko'ina. **Zirga-zirga :** yawace-yawacen jama'a da na motoci kan hanyoyi.

Citation : zuwa shaida : nasi, gabata gidan juju a matsayin shaidu, ko don ceton wani. Zuwa shaidu.

Cité : Kasa : sunan da ake gaya wa kasa kan fannin shari'a. Ya kyautu kowane d'an kasa ya daratta dokokin kasa.

Citoyen : d'an kasa : d'an kasa wanda ya san y'ancinshi, kuma yana aikata abin da ya wajabta kanshi. **Y'an kasar Nijar :** al'ummar kasar Nijar masu cikakken y'anci, kuma masu aikata abin da ya wajabta kansu.

Civil : farar fula : mutunen da ba soji ba. Hukomomin farar fula. 2) Wanda ya shafi dangantaka tsakanin jama'a. Ya kai kara gaban jujun fasar fula.

Civique : Na d'an kasa : Abin da ya shafi d'an kasa, dangance da kokari da ya kyautu ya kawo wa kasarshi. Kare kasarsa, kishin kasa ne.

Clairvoiyance et pragmatisme : Niyya da aikatawa : d'aukar niyya da cika ta . Abokan aikinshi suna sonshi saboda niyyarshi ta aikatawa.

Clan : Zuri'a : iri na mutane daban-daban da ake samu cikin kabila. Aure tsakanin y'an zuri'ar biyu ya kara dankon zumunci tsakanin su.

Clandestin : Na sace : wanda ke yin abubuwa ba kan ka'ida ba, sarende ; na haure. Yin zirga-zirga a sace.

Classe : Gungu : mutane masu matsayi guda, wad'anda suke cikin hali guda. Gungun talakkawa. **Gungun masu iko : Mahukunta :** dukan masu tafiyar da harakokin hukumanci.

Classe oppressive : Gungun y'an muzgunawa : mutane masu gallaza wa wad'ansu wahala.

Classe ouvrière : Gungun lebarori : masu aikin karfi

Classe politique : Y'an siyasa : dukan mutanen da ke ra'ayin siyasa cikin kasa.

Classe sociale : Gungun

jama'a masu hali guda : dukan mutane masu halin rayuwa iri guda.

Clause : sharaɗi : matakai na musamman da aka tsayar kan wani abu. Daratta sharuɗɗan yarjejeniya.

Clémence : afuwa : ragowa, yafewa, tausayawa. Lauya yana neman a yi wa wanda ake zargi afuwa.

Clientélisme : lallashi : neman yin suna ta hanyar daɗin baki. Lallashin yan siyasa.

Climat : Yanayi/hali : halin da ake cikinshi. Halin yarda ya tabbata tsakanin masu neman tattaunawa.

Cloison : Bambance-bambace : rarrabuwa, rishin haɗin kai, bambance-bambance. Ya kyautu yan siyasa su kawar da bambance-bambance tsakanin su don ginin ƙasa.

Clôture : Rufi : shinge, ƙarshe, ƙarewa. An ɗaga ranar rufe taron majalisar dokoki.

Coalition : Kawance : haɗin gwiwa, ma'amula ta wani ɗan lokaci tsakanin ƙasashe, ko jam'iyun siyasa ko mutane, don aiwatar da wani abu. Kawance tsakanin jam'iyun siyasa a majalisar dokoki ya kawo sauyawar rinjaye.

Codage : Salo : Isar da wani zance ta hanyar da ba kowa ke iya ganewa ba. Yin salo wajen gabatar da rohoto mai sirri.

Code : Kundin tsari : kundi mai ƙumshe da dukan dokoki da matakai masu ƙayyade wani abu. Ya kyautu masu gida da ma'aikata su yi aiki da kundin tsarin aiki.

Code de la famille : Kundin tsarin iyali : kundi mai ƙayyade dukan tabi'oi, da halaye da suka kyautu cikin iyalai.

Code de travail : Kundin tsarin aiki : kundi mai ƙayyadde matakan tafiyar da aiki.

Code pénal : Kundin tsarin shari'a : kundi mai ƙayyade abubuwan da suka kasance laifi kan fannin shari'a kuma ya nuna hukuncin da ya danganta da kowane laifi.

Code rurale : Kundin tsarin karkara : kundi mai ƙayyade matakan tafiyar da rayuwa a karkara.

Codifier : Tsarintawa : tattara matakai, da ƙa'idodi share guda. An kafa wata ƙungiyar malamman shari'a don tsarinta matsayin yan siyasa.

Codifier les opinions politiques fondamentales : Tsarinta mahimman ra'ayoyin siyasa : Shiri da kawo kimtsi kan mahimman ra'ayoyin siyasa.

Coexistence : zaman tare : zaman tare tsakanin mutane. Zaman mafaɗata biyu yana kawo tashin hankali.

Coexistence pacifique : Zaman kwanciyar hankali : ƙarfafa dangantaka tsakanin ƙasashe biyu, ko gungun ƙasasashe masu ra'ayin siyasa guda.

Cogestion : Tafiyar da harakoki tare : haɗin gwiwa cikin tafiyar da waɗansu harakoki. Tafiyar da harakokin hukumanci tare da jama'a ya kawo haske cikin tafiyar da harakokin ƙasa.

Cohabitation : gwamnati mai ruwa biyu : gwamnatin gamin gambiza inda shugaban jamhuriya ba ya da rinjaye a majalisar dokoki. K'asar Nijar ta yi zama da gwamnati mai ruwa biyu a jamhuriya ta uku.

Cohabitation harmonieuse : Gwamnati mai ruwa biyu mai zaman laluma : zaman girma da arziki tsakanin shugaban jamhuriya da paraminista mai rinjaye a majalisar dokoki.

Cohabitation timultueuse : Gwamnati mai ruwa biyu mai zaman tashin hankali : zama na rishin jituwa tsakanin shugaban jamhuriya da paraminista mai rinjaye a majalisar dokoki.

Cohérence : tsari mai kyau : tsari cikin wani abu, daidaita. Tsararren jawabi.

Cohérent : mai tsari : Wanda ke ƙumshe da abin da ke a tsare. Ya gabatar da shiri mai cikakken tsari a gaban y'an majalisar dokoki.

Cohésion : Haɗin kai : dangantaka, gudun-muwa tsakanin mutane. Zumuntaka na kawo haɗin-kai cikin jama'a.

Coincidence : gamen katari : sa'ar gamuwa da wani abu, abkuwar wani abu da wani abu gaba d'aya. An yi gamen katari sun iso rana guda.

Collaborateur : Abokin aiki : mutanen da ke aiki tare, abokin haɗin gwiwa. Babban abokin aiki.

Collaboration : haɗin gwiwa: gudunmuwa, ma'amula, taimakon juna. Y'an sanda na neman haɗin gwiwa ga jama'a don kame wani mutum da ya yi kashin kai.

Collecte : tattara : roƙo, gangamawa wuri guda. Tattarar kuɗin lanho yana taimakowa wajen aikata abubuwa masu amfanin jama'a.

Collectivité : Zaman jam'a : dukan mutanen da ke zamne wuri guda, masu al'adu guda, masu guri guda. Zama cikin jama'a.

Collectivité territoriale : ƙaramar hukuma.

Collège électoral : masu zaɓe : dukan masu zaɓen da ake gayyata don su je, su jefa ƙuri'a. An sake gayyatar masu zaɓe da su je su jefa kuri'a.

Colloque : Taro : mafawara, taron ƙara wa juna ilimi. Yin zaman taro.

Colon : ɗan mulkin mallaka : mutunen da ya zo mallakar waɗansu mutane, wanda ya zo muzguna masu. Ɗan mulkin mallaka da yawa sun yada zango a Afirka a ƙarni na 19.

Colonialisme : Mulkin mallaka : Tsarin mulki na bida jama'a kan fannin siyasa, da al'adu, da tattalin arziki. Mulkin mallakar ƙasar faransa.

Colonialiste : Ɗan mulkin mallaka : mai ra'ayin mulkin mallaka, mai aikata shi. Mulkin mallakar ƙasashen turai ya kawo cikas cikin tafiyar da tattalin arziki, da jin daɗin rayuwar al'umma.

Colonisation : Mulkin mallaka : mallakar da wata ƙasa ke yi wa wata ƙasa kan fannin siyasa, al'adu, da tattalin arziki.

Combat : Yaƙi : faɗa tare da amfani da makamai, ko hannu goma don kai farmaki, ko don kare kansa. Yaƙin caccar baki ya haɗa yan takara biyu masu neman zama shugaban jamhuriya.

Combat d'idées : Yaƙin bazar da ra'ayi : yaƙin barbaza ra'ayin mazahabarsa.

1) Comité : Kwamiti : haɗuwar mutane kaɗan da aka tsamo daga cikin jam'a don su yanke shawara kan waɗansu harakoki. Kwamiti mai ƙumshe da harakoki mutane kaɗan.

Comité régional de développement : Kwamitin jaha na ci-gaba : Kwamitin tattalin ci-gaban jaha.

2) Mutanen da aka zaɓa don tafiyar da wata haraka : An girko wani kwamitin dattawa don warware matsalolin da ake ciki.

Comité de pilotage : Kwamitin zartarwa kwamiti mai bi sau-da-ƙafa : kwamitin da aka azawa nauyin bin waɗansu harakoki san-da-ƙasa.

Comité de rédaction : kwamitin wallafawa : kwamiti mai kula da rubuce-rubuce.

Commande : izini : bai wa ɗan kasuwa izinin ɗauko waɗansu kayayyaki, aikin wani ƙayadaddden lokaci. Bai wa ɗan kasuwa izinin ɗauko kaya.

Commando : Ɗan ta-kife : Sojojin kima da ake bai wa horo na musamman, don aikata waɗansu ayyuka cikin duhu ; sojin ƙundumbala ; komando na yaƙi.

Commémoratif : Na cikon shekara : ranar da ake tunawa da wani mutum, ko wani abu da ya faru. A kowace ranar uku ga August, ana shagulgulan cikon shekara ta samun yancin kai.

Commenter : Ƙara bayyani : kawo gyaren fuska kan wani abu, kwatantawa. Ƙara bayyani kan doka.

Commerce : Kasuwanci : yin saye da saidawa, fatauci. Matan

Nijar sun fara mayar da hankalinsu wajen kasuwanci.

Commissaire : komsar : mutunen da ke da nauyin tafiyar da wad'ansu ayyuka cikin wani gajeran lokaci. Komsar na polis.

Commissaire aux comptes : Mai larwan kud'i : mutunen da ke la'akari da kud'in da ke shiga da masu hito cikin wani asusu.

Commissaire de police : Komsar na polis : Ofisan polis mai shugabantar kwamsariya.

Commission : Kungiya : hukuma, mutanen da ake zabe don su yi nazari kan wani abu, ko su yi wani bincike. Kungiyar zabe.

Commission permanente : Kungiya ta dindindin : Kungiya mai gudanar da aiki yau-da-kullum.

Commission spéciale : Kungiya ta musamman : Kungiyar da ake kafawa don shawo kan wad'ansu matsaloli da suke kunno kai.

Commission temporaire : Kungiya ta gajeran lokaci : Kungiya ta wucin gadi

Commission d'enquête : Kungiyar bincike : Kungiya mai gudanar da larwai da bincike.

Commission d'appel d'offres: Kungiya mai binciken takardun yan kwangila : Kungiyar da ake kafawa don ta binciki takardun yan kwangila.

Commission nationale de lutte contre la délinquance finany cière et fiscale : Kungiyar kasa mai yaki da almuzuranci da dukiyar kasa : Kungiyar da kwamitin had'in kan yan kasa (C.R.N) ya kafa don gudanar da bincike bisa kan yanda tsohin hukumomi suka tafiyar da harakokin kud'i.

Commission paritaire : Kungiyar da ta kumshi ma'aikata da masu gida-jensu : Kungiyar wadda ta kumshi wakillan ma'aikata da masu gidajensu, a yawa daidai wa daida.

Communauté : Al'umma : mutanen da ke zaune wuri guda; masu dangantaka ta fuskar al'adu, ko kasuwanci, ko siyasa. Zama cikin al'umma guda.

Communauté internationale : Al'ummar duniya : dukan kasashen duniya, musamman wad'anda ke karkashin inuwar kungiyar majalisar d'unkin duniya (O.N.U).

Commune : Kwamin : Karamin yanki cikin tsarin rarrabe-rarrabe wanda magajin gari ke hakumanci. Birnin Yamai rabe yake a kwamin uku.

Communication : Sadarwa : Isar da wata magana, had'i. Harshen abin isar da sadarwa ne.

Communiqué de presse : Sanarwa : ra'ayin da wata

ƙungiya ko hukuma ke gabatar wa jama'a. Fitar da sanarwa.

Communiquer : Sanar da : Isar da labari, shaidawa. Sanar da wani labari.

Communisme : Komisanci/ Ra'ayin gurguzu : tsarin tattalin arziki da na zamentakewa wanda ya dogara kan mayar da komi na jama'a. Tsarin komisanci yana ta tabarɓarewa tun shekara alif ɗari tara da tasa'in (1990).

Communiste : Ɗan ra'ayin komisanci. (Ɗan ra'ayin gurguzu) : mai bin aƙidar komisanci. Tsarin mulki na komisanci.

Compatibilité : halin abun da ke zuwa daidai (da ke dacewa) : halin abun da yake daidai da wani abu, wanda ya zo ɗaya. Daidaitar jini

Compatriote : Dangi ɗan ƙasa : Ɗan asalin ƙasa guda. Shugaban ƙasa ya yi jawabi ga dangi ɗan ƙasa.

Compétence : Iya aikata wani abu/gwaninta/iyawa : Wani ƙoƙarin da aka sani ga hukuma na aikata waɗansu ayyuka cikin waɗansu ƙayadaddun sharuɗ-ɗa. Iya aikata wani aiki ga hukumomin shari'a.

Compétitif : Na gari : abin da ke iya gogayya da waɗansu, na ƙwarai, na kirki. Kampani na gari.

Compétition : Gasa/Takara/ ƙoɓala : halin da mutane da yawa ke neman zaɓe koɓalar zaɓe (takara).

Complément : ciko : ƙarin da ake yi wa wani abu don ya zama cikakke. Cikon bayyanai.

Complice : mai hannu cikin wata manaƙisa : Mai sanya hannu cikin wani aikin ɗan ƙasa. Sanya hannu wajen aikata sata.

Comploter : shirya wata cuta : shirya wata manaƙisa, wata maƙarƙashiya. Shirya juyin mulki.

Comportement : hali : dukan irin tabi'o'in mutum. Ciwon Sida ya kawo sauyawar halayen matasa kan harakar neman mata.

Composante : kashi : abin da wani abu ya ƙumsa, abubuwan da ke haɗuwa wuri guda su zama rukuni. Kashi daban-daban na ɗan ƙasa.

Composition : abubuwan da ke gida-gida da ake haɗawa wuri guda : shirya wani abu wuri guda. An bayyana wa jama'a kasashin gwamnati.

Compréhension : fahinta/ daɗin kai : fahimtar wani abu da sauƙi, ilimi. Yin daɗin kai.

Compromettre : ɓatawa : Ɗin wani abun da za ya baƙanta wa mutum rai, ƙetata, sanya mutum uku. ɓata makomar mutum.

Comptabilité : ilimin lissafin kuɗi : fusa'ar gudanar da lissafin harakokin kuɗin mutum, ko na masana'anta, ko na ƙasa. An

tafiyar da lisafin harakokin kampanin, yanda ya kamata.

Compte rendu : bayani : labari a takaice, rahoto. Ministan noma ya bayar da bayani kan harakokin noma cikin kasa.

Concentration : Cinkoso : gosulu, gangamuwar wad'ansu abubuwa wuri guda, dankalewa. Cinkushe hakumanci wuri guda.

Cinkushe hakumanci : halin kakkace hakumanci daga wajen manya-manyan hakumomi.

Concept : Tsari : bayanai kan mahimman shikashikan tsari : wata manufa, ko kuma wani abin da aka sarafa, dangance da gurin da ake son cim ma. Tsari sabo.

Conception : Tunani ; kirkira : yin nazarin wani abu cikin kansa. Nazari : kirkiro wani pureje.

Conception et élaboration des stratégies et politiques de développement : Nazari da girkar da hanyoyin ci-gaban kasa : Shinfid'a hanyoyi na gari don tabbatar da tsare-tsaren ci-gaban kasa.

Concertation : Shawara : sauraren ra'ayin dukan mutanen da wani tsari ya kumsa kahin d'aukar wata niyya. Magabatan jam'iyar sun shawarci magoya bayansu kahin su amince da ka'idodin tsarin jam'iyar.

Concillier : sasantawa : kawo shiri tsakanin mutane masu bambancin ra'ayi. Sasanta masu gaba da juma.

1) Conclure : Cim ma yarjejeniya : samun shiri ta hanyar yarjejeniya, magance wani abu. Cim ma yarjejeniya.

2) **Karewa :** a karshe : A karshen jawabinshi, ya kira yan kasa da su had'a kansu.

Conclusion : Kammalawa : karewa, karshe. Kammala ayyukan yarjejeniya.

Concorde : had'in-kai : amintaccen zaman tare, gane wa juna, shiri. Ranar ishirin ga April, rana ce ta had'in-kan yan kasa a Nijar.

Concours : taimako : gudunmuwa, had'in gwiwa. Taimakon kud'i.

Concret : ingantacce : hakikantacce, abin da ke nuna tabbacin wani abu, mai dimanta wani abu.

Majalisar dokoki ta gabatar da ingatattun shawarwari don warware matsalolin da ake fama da su.

Concrétisation : hakikantawa : cikawa : tabbatar da wani abu, aikatawa ; yana bakin kokarinshi don gurinshi ya cika.

Concurrence : Gasa ; kishi : rishin jituwa, gasa tsakanin mutane da yawa masu son cim ma guri d'aya. Gasar kasuwancin da ba ta dace ba.

Concurrent : ɗan takara : abokin adawa. Y'an takara da yawa sun shiga yaƙin zaɓe.

Concurrentiel : Na gasa : na kishi : abin da ake gasa da shi. Abubuwan da aka sarrafa na gasa.

Condamnation : Hukunci : yanke hukuncin ɗauri ga mutumen da aka kama da laifi. Ɗauri maras wa'adi.

Condamnation politique : Hani a fannin siyasa : yarda wani abu.

Condamnation réligieuse : Haramtacce kan fannin addinni: hananne, abin da bai dace a aikata ba a fuskar addini.

Condamnation définitive : Yanke shari'a bayan idon mutum : yanke hukunci ga mutunen da ya tsere.

Condamnation à mort : hukuncin kisa : mutumen da aka yanke wa hukuncin kisa. An kashe mutunen da aka yanke wa hukuncin kisa.

Condamné de droit commun: wanda aka yanke wa hukunci : mutunen da aka ɗaure kan ƙa'ida, ba tare da wani sasauci ba. An yi afuwa ga mutunen da aka ɗaure.

Condamner : Hukuntawa : yanke hukunci bayan an gabatar da shari'a. Hukunta wanda aka kama da laifi.

Conditions climatiques : Halayen yanayi : Harakokin noma ba su zuwa yanda ake son su a Nijar saboda halayen yanayin da ba su da kyau wani lokaci.

Conditions d'éligibilité : Sharuɗɗan zama ɗan takara : sharuɗan da ake shinfiɗawa wajen zaɓen mutane a wani matsayi. Sharuɗan zaɓen shugaban jamhuriya.

Conditions d'un développement équilibré : Sharuɗan cimma daidaitacen ci-gaban ƙasa : hanyoyin da suka dace don cimma ci-gaban ƙasa. Nauyi ya rataya a wuyan gwamnati na ya shinfiɗa sharuɗan cimma daidaitacen ci-gaban ƙasa.

Conduites des affaires : Jan ragamar harakoki : tafiyar da harakoki. Y'an ƙwadago sun yi Allawadai da yanda gwamnati ke jan ragamar harakoki.

Confédération : ƙungiya : haɗin-kan ƙasashe masu yancin kai da suka amince su saka wa waɗansu ƙungiyoyinsu cikakken iko. Zama cikin wata ƙungiya.

2) Haɗuwar ƙungiyoyi na ma'aikata, ko na y'an ƙwadago don kare hakkinsu. Ƙungiyar ƙasa ta ma'aikata (C.N.T).

Conférence : Babban taro : haɗuwar mutane da yawa wuri guda don tattaunawa kan waɗansu abubuwa, mafawara.

An yi taron ƙasashen yan ba ruwanmu a Afirka ta kudu a alif ɗari tara da tasa'in da takwas (1998).

Conférence débat : Taron canza miyau : tsararrar mafawara kan ƙayyadadden abu.

Conférence des cadres : Taron manyan ma'aikata : haɗuwar shugaban ƙasa da sauran mahukunta don tattaunawa kan matsalolin da suka shafi halin siyasa da na zamentakewa da kuma halin tattalin arziki.

Conférence des chefs d'état: Taron shugabannin ƙasashe: haɗuwa tsakanin shugabannin ƙasashe.

Conférence nationale souveraine : Babbar mahawarar ƙasa : zaman taro mai cikakken yanci wanda ya haɗa dukan wakillan jama'a daban-daban don tattaunawa kan matsalolin da suka shafi ƙasa.

Conférer : Sakawa : Bayar da, miƙawa. Tsarin rarrabe-rarrabe yana saka wa jahohi cikakken iko.

Confidence : sirri : faɗa wa mutum abubuwa a asirce. Faɗin sirri.

Configuration : kasancewa : kama, tsari, yadda abu yake. Yadda gwamnati ya kasance.

Confirmation : Tabbaci : yarda, amincewa, hakikanci. Tabbacin wata niyya.

Conflit : Faɗa : rigima, rishin jittuwa, hargitsi, jayayya. Faɗa da makamai.

Conflit de compétence : faɗan gatanci : faɗa a kan gatancin wani abu.

Conflit d'intérêts : faɗan son kai : rigima ko jayayya tsakanin mutum biyu ko hiye, inda kowa kanshi ya sani.

Conflit de générations : faɗan da ba na sa'a da sa'a ba : bambancin ra'ayi tsakanin waɗanda ba tsara ba.

Confrontation : 1) **Zozayya** : sanya jayayyar (gogayya) ra'ayi tsakanin mutane don kwatanta su.

2) **Fito-na-fito** : ɗauki-ba-daɗi . Fito-na-fito tsakanin jami'an tsaro da masu zanga-zanga ya haddasa rauninnika da dama.

Confrontation des idées : zozayyar ra'ayi : canjin ra'ayi tsakanin mutane don kwatanta su.

Confusion : Ruɗani : yamutsi, hargitsi, rishin tsari. Ruɗanin siyasa.

Congé : Hutu : izinin yin fashi, na dakatar da aiki, farmaso. Hutun biƙi.

Congé payé : hutu tare da biya : izinin fashin aiki kuma tare da albashi.

Congrès : Babban taro : Taron mahawarar mutane da yawa.

Jam'iyya ta yi kiran babban taronta.

Conjoint : 1.) **Haɗaɗɗe** : na game da .....

2.) **Miji da mata** : waɗanda aure ya haɗa.

Conjontion : **haɗi** : gami, taruwa, ɗori.

Conjontion des efforts : haɗin ƙarfi : gama ƙarfi don cin ma wani sakamako.

Conjonction des idées : haɗin ra'ayi : gama ra'ayoyi don neman warware wata matsala.

Conjonction des sensibilités : haɗin kan mutane daban-daban : tara dukan mutane su zama kan tsintsiya.

Conjoncture : 1.) **Hali** : halin da ya hito daga haɗuwar wasu abubuwa. Dataccen hali.

2.) Dukan abubuwan da ke nuna halin tattalin arziki, halin rayuwar al'umma, halin siyasa ko na yaɗuwar al'umma cikin wani ƙayyadadden lokaci.

Conjoncture économique : **Halin tattalin arziki** : gurɓacewar tattalin arziki, fatara.

Connivence : **gamin kai** : munahuci na ɓoye laifin wani, haɗa kai da wani. Game kai da wani.

Conquête : **farauta** : yin ƙoƙari cincin ƙarhinsa don samun wani abu, mallaka. Farautar iko.

Conscience : **hankali** : sanin ciwon kai. Samun hankalin kiyaye aikinsa.

Conscience nationale : kishin ƙasa : son ƙasarsa,

1.)**Conseil** : **Shawara** : neman ra'ayin wani kan wani abu. Bai wa wani shawara.

2.) Zaman taro don yanke shawara kan waɗansu abubuwa.

Conseil consultatif : kwamitin ban shawara : kwamiti mai bayar da ra'ayinshi cikin tafiyar da harakokin ƙasa.

Conseil économique culturel et social : kwamiti mai kula da tattalin arziki da kare al'adu da jin daɗin rayuwar al'umma : Kwamiti mai nauyin gudanar da bincike da bayar da ra'ayinshi kan harakokin tattalin arziki, da na al'adu, da zamantakewa.

Conseil d'administration : **Zaman shawarar mahukunta** : haɗuwar masu zuba jari don tattaunawa kan harakokin da suka shafi kawo tsari cikin masana'anta, ko wata ƙungiya.

Conseil des ministres : zaman taron majalisar ministoci : mafawarar ministoci a ƙarƙashin jagorancin shugaban ƙasa don yanke shawara kan rayyadaddun abubuwa.

Conseil municipal : kwamitin shawarar na gari : zaɓaɓɓun mutane da ke da nauyin tafiyar da harakoki cikin birane.

Conseil d'établissement : kwamitin shawara na makaranta : zaman mafawara mai haɗa mahukunta, malamman makaranta da y'an makaranta da uwayensu a cikin makaranta.

Conseil d'Etat : kwamitin ƙasa : kwamitin da ake shawarta kahin a gabatar da doka a majalisar dokoki, da kuma waɗansu ƙa'idodi kahin a bayyana su.

Conseil de développement : kwamintin ci-gaba : kwamiti mai ƙumshe da mutane masu kula da harakokin ci-gaba.

Conseil de sage : kwamitin dattawa : kwamiti da ke ƙumshe da dattawa masu nauyin aza ƙasa kan hanyoyi na gari.

Conseil de reconciliation nationale : kwamitin haɗinkan y'an ƙasa : kwamitin da sojoji suka girka don tafiyar da wucin gadi bayan juyin mulkin ranar tara (9) ga watan April 1999.

Conseil de département : kwamitin dapartama : kwamiti mai nauyin tafiyar da harakokin dapartama.

Conseil local : kwamitin jaha : kwamiti mai nauyi tafiyar da harakoki a cikin jaha.

Conseil extraordinaire : (zaman) taro na musamman : mafawara ta musamman.

Conseil général : babban (zaman) taro : (zaman) taro inda dukan mambobin ƙungiyar ke halarta.

Conseil local de développement : kwamitin jaha na ci-gaba : kwamiti mai kula da harakokin ci-gaban jaha.

Conseil supérieur de la communication : babban kwamitin sadarwa : kwamitin da ke kula da tsarinta kafofin watsa labaru.

Conseil supérieur de la magistrature : babban kwamitin malamman shari'a: kwamitin ban shawara wanda yake ƙunshe da malamman shari'a.

Conseil supérieur de la défence nationale : kwamiti mai kula da kare ƙasa a game da duk wani hari.

1) **Conseiller : Mai bada shawara** : mutumen da ke bayar da ra'ayi kan waɗansu ƙayyadaddun harakoki. Mai ban shawara a fadar shugaban ƙasa.

2) Mutumen da ke cikin wani kwamiti na hukumanci. Konsayen jaha.

Consensus : yarjejeniya yarda : haɗin kai tsakanin mutane, amincewar juna. Samun yarda tsakanin y'an ƙasa.

Consentement : yarda : amincewa, samun na'am daga kowa. An naɗa shugaban ƙungiyar zabe ta ƙasa mai zaman kanta tare da samun yardar dukan jam'iyun siyasa.

1) **Consentir : Bayar da yarda:** yaba wani abu, amincewa da shi. Yarda da bada bashi. 2) ɗaukar alkawali kan wani abu. Ɗaukar alƙawalin bada kansa.

Conséquence : Sakamako : wani hali da ke biyo bayan wani abu yajin aikin da malamman makaranta suka yi ya kawo mummunan sakamako cikin tafiyar da harakokin karatu.

Conservation des ressources naturelles : tattalin albakatun ƙasa : matakan da ake ɗauka don kiyaye albarkatun ƙasa.

Conservation et organisation de l'espace : tattali da kawo tsari ga muhalli : matakan da ake ɗauka don tattalin muhali da kariyar shi. An kafa ƙungiyoyi masu zaman kansu don tattalin huhalli da kariyar shi.

Considérant : ganin cewa : matakan da ke hujjatar da wani ƙudiri, ko doka, ko wajen yanke shari'a. Ganin cewa akwai son rai ga dokar da aka kafa, y'an sandika na neman a soke ta.

Considération : ƙauna : bincike a hankali, so ko ƙaunar da ake yi wa wani abu. Samun ƙaunar masu gidajensa.

Prendre en considération : lissafawa da : yin la'akari da wani fanni cikin gudanar da wani abu.

Consolidation : ƙarfafa : zaunar da abu da kyau, ƙara mishi ƙarfi. Cikin hanyar ƙarfafa huldɗa tsakanin ƙasar Nijar da makwabtanta na kudu, an kafa wani kwamiti na ƙasa da ƙasa.

Consommateur : masu saye: mutanen da ke amfani da kayayyaki don biyan buƙatunsu. Y'ancin masu saye.

Consommation : sha : amfani da waɗansu kayayyaki, ko abubuwa da ke cikin buƙatun tafiyar da rayuwar mutum. Shan wutar lantarki.

Constat : Shaida : rahoton da malamin shari'a ke rubutawa don bayyana yanda aka gabatar da wani abu. Shaidar malamin shari'a.

2) Sakamakon biciken yanda wani abu yake tafiya.

Constitution : Tsarin mulki : dokokin da ke kafa tsarin harakokin tafiyar da ƙasa. Amincewa da tsarin mulki.

Constitutionnalité des lois : Dacewar dokoki da tsarin mulki : dokokin da ba su kauce wa tsarin mulka ba, waɗanda suka daidaita da tsarin mulki. Bincike kan dacewar dokoki da tsarin mulki.

Construction nationale : ginin ƙasa : tattalin ƙasa, kawo ci-gaba. Ginin ƙasa ya rataya a wuyan kowane ɗan ƙasa.

Consul : Ƙaramin jakada : Aikakken ma'aikaci na wata ƙasa don tafiyar da harakokin hukumanci cikin wata ƙasa.

Karamin jakada ya biya bukatun Kasarsu kan gaskiya.

Consulat : Ofushin karamin jakada : ma'aikatar da karamin jakada ke shugabanta. Mutum ya tafi Ofushin karamin jakada.

Consultatif : Na ban shawara: mai bada shawara. Buro na ban shawara.

Consultation : Shawara : kwamiti mai bincike don yanke shawara kan wata haraka. Shawarar kwararru.

2) Samun ra'ayin mutum, neman ra'ayin yan kasa, jefa kuri'a.

Shugaban jamhuriya ya roshe majalisar dokoki bayan da ya samu ra'ayin yan kasa.

Consultation directe : zabe da kai : tsarin zabe wanda mai zabe ke zabar d'an takara da kanshi.

Consultation indirecte : zabe daga wakillai : tsarin zabe inda wakillai ne ke zaben d'an takara.

Consultation populaire : Kuri'ar neman ra'ayi : zabe wanda masu zabe ke jefa kuri'a don nuna amincewarsu ko rishin amincewarsu.

Consulter : shawarta : neman ra'ayin jama'a. Shawartar yan kasa ta hanyar shirya zaben amincewa ko na rishin amincewa.

Contentieux : rikici : rishin jituwa, gardama mai iya kaiwa har koti. Warware rikici.

Contentieux électoral : rikicin zabe : rikicin da yake barkewa a sanadiyar rishin amincewa da sakamakon zabe.

Contestation : jayayya : rishin amincewa, gardama, tsayayyar adawa, kin yarda. Babbar jayayya ta kunno kai a game hiddawar da aka yi mishi daga cikin masu shugabancin jam'iyar.

Contexte : hali : dukan abubuwan da wani abu ke faruwa a cikinsu, yanayi. Halin siyasar da ake ciki yana bukatar a zauna kan teburin tattaunawa tsakanin gwamnati da bangaren yan adawa.

Contexte géopolitique : Halin siyasa dangane da tsarin mahalli da yanayi.

Continent : Nahiya : yankin duniya. Kasar Afirika na d'aya daga cikin nahiyoyi biyar na duniya.

Continuité de l'Etat : Halin tafiyar da harakokin hukumanci jika da jika : kiyayewa da yanda harakokin hukumanci suke tafiya ; bi-sau-da-kafa. Kiyayewa da tafiyar harakokin hukumanci jika da jika.

Contradiction : sabani : rishin yarda, karyatar da wani. Gano sabani cikin zancen wani.

Contrainte : Matsi/matsala : 1) Tilasawar da ake yi wa mutum, ko wani abu, taka hakki. Aikata wani abu ba tare da an tilasa wa mutum ba.

2) **Tuhuma** : tilasawa wani ya biya abin da ake bin shi. Matsalar aiki.

Contraste : Bambanci/gibi : Bambanci tsakanin abubuwa biyu. A ƙasar Nijar akwai babban bambanci (gibi) tsakanin birane da ƙauyuka.

Contrat : Yarjejeniya : amincewa da juna, yarda da juna. Kungiyoyin sandika biyu sun rattaba hannu kan wata yarjejeniya mai tabbatar da haɗuwarsu wuri guda.

Contre-pouvoir : Adawa : masu sukar ra'ayin gwamnati, masu larwan ayyukan da yake yi. Yin adawa.

Contresigner : Rattabawa : haƙƙikantar da, tabbatar da, sanya hannu don nuna amincewarsa. Rattaba hannu kan wani ƙudiri.

Contribuables : Masu biyan tara : mutane masu biyan duk waɗansu kuɗi da suke wajibi a gare su a cikin ƙasa. Kamar lanho, asangam da saurensu. Kuɗin masu biyan karo.

Contribuer au développement équilibré de la nation : Sanya hannu cikin bunƙasa tattalin arzikin ƙasa : bada ƙoƙarinsa cikin tafiyar da harakokin ci-gaban ƙasa.

Contribution : gudummuwa : agajin da kowa ke kawowa, tarbace. Ya wajabta ga kowane ɗan ƙasa ya kawo gudun-muwarshi don ginin ƙasa.

Contrôle : Dubi/la'akari : larwai, binciken abu dala-dala, nazari. Babban asusun ƙasa ke da nauyin la'akari da kuɗin da ke shiga da masu fita cikin ƙasa.

1) **Contrôler : Dubawa/yin larwai** : bi sau-da-ƙafa, larwan kuɗi.

2) Kiyayewa. Kiyayewa da kuɗin ƙasa.

Contumance : ƙin amsa ƙara : halin da wanda ake zargi ya ƙi gabata gaban koti. An yanke hukunci a bayan idon yan ta'adar da suka ƙi amsa ƙara.

Convention : Yarjejeniya : abubuwan da suke amintattu ga kowa, yarda ; yarjejeniya tsakanin ƙasashen duniya.

2) Matakan da ke biyo bayan wata yarjejeniya. Ka'idodin jama'a.

Conviction : tabbaci : yarda, amincewa. Samun tabbaci ga wani abu.

Conviction politique : amincewa da wani tsarin siyasa : kawo cikakken goyan baya ga wani tsarin siyasa.

Conviction universelle : Amintacce ga duniya : Abin da duniya gaba ɗaya ta yi imani da shi.

Convocation : Kira : gayyata. Amsa kira.

Convocation du collège électoral : Gayyatar masu zaɓe : kiran masu zaɓe wajen jefa kuri'a.

Convoquer : kirawowa : gayyatowa, sanya wani ya zo. Kiran taro.

Coopération : 1) Kawo gudun-muwa kan harakokin da suka shafi jama'a, taimako, agaji. Samun gudun-muwa.

2) Kawo tamaiko, ko agaji cikin harakokin arzikin wata ƙasa, huldɗa. Huldɗa tsakanin ƙasa da ƙasa.

Coopération de l'organisation judiciaire : huldɗa kan fannin tsarin shari'a : gudummuwa da ake kawowa cikin tsarin shari'a.

Coopération en matière culturelle, scientifique et technique : huldɗa kan fannin raya al'adu, da ilimin kimiyya da fasaha : gudun muwa da wata ƙungiya ke kawowa cikin fannin tsarin raya al'adu da ilimi da kimiyya.

Coopération des transports, des communications et des télécommunications : huldɗa kan abubuwan da suka shafi zirga-zirga da sadarwa.

Coopération de lutte contre les calamités naturelles : huldɗa kan fannin yaƙi da hamada : yarjejeniya tsakanin ƙasashe don yaƙi da hamada, da wasu matsalolin da ke aukuwa.

Coopération en matière de défense : huldɗa kan harakokin tsaro : gudun-muwar da ake kawo wa wata ƙasa cikin tafiyar da harakokin tsaro.

Coopération en matière de santé : huldɗa kan fannin kiwon lafiya : gudummuwar da ake kawo wa wata ƙasa wajen tafiyar da kiyaye lafiyar mutane.

Coopération en matière de gestion des ressources hydrauliques : huldɗa kan fannin tanadin ruwa : gudummuwar da ake kawo wa wata ƙasa kan fannin tanadin ruwa.

Coopération linguistique : huldɗa kan fannin ilimin harshe : gudun-muwar da wata ƙasa ke kawo wa wata ƙasa kan fannin tattalin harsuna.

Coopération sud-sud : huldɗar ƙasashen kudu: huldɗa tsakanin yankunan da ke kudu.

Coopérative : Ƙungiya : 1) Kampani, ko wata masana'anta inde masu zuba jari ke da hakki daidai wadaida. Kafa ƙungiya.

2) Ƙungiyar haɗin gwiwa. Ƙungiyar karkara.

Coordinateur local : Babban mai kawo tsari : mutanen da ke nauyin tsarinta wani abu. Babban mai kawo tsari ya halarci waɗansu ayyuka da mutanen yanki suka shirya.

Coordination : Sanya tsari : haɗin (shirya) waɗansu

abubuwa don cim ma wani guri.

Sanya tsari cikin harakokin masana'anta.

Coordonner : tsarintawa : tsarinta wani abu da niyyar cim ma wani guri. An naɗa wani wakili don tsarinta harakokin jama'a.

Corps : Gungu (sashe) : haɗuwar mutane wuri guda dangance da irin ayyukansu. Gungun malaman makaranta.

Corps diplomatique : Gungun (sashen) yan jakadanci : dukan jakadai da ke wakilci cikin wata ƙasa. An gayyaci gungun jakadai ga wata mafawara wadda shugaban ƙasa ke jagoranci.

Coorespondance : Dangantaka: Kaɗafa donƙon zumunci ta hanyar wasiƙa, ko ta hanyar sadarwa. Aika sakon dangantaka.

Corrompu : mai karɓar cin hanci : wanda ake saye, ko wanda ake sayewa. Tashi tsaye kan masu karɓar cin hanci.

Corruption : Cin hanci : Yin cin hanci ; amfani da kuɗi don sanya mutum ya yi abun da ake so.

Côter : Tofa albarkacin bakinsa: Yaba darajar wani abu, bada ra'ayinsa. Tofa albarkacin bakinsa kan ɗan takara.

Cotisation : tarbace : kuɗin da ake tattarawa don yin waɗansu kashe kashen kuɗi da suka shafi jama'a. Tarbacen ƙungiyar yan ƙwadago.

Couche : Aji : Tsara guda, masu hali guda. Matsakaicin aji.

Couleur : Launi : 1) Kamannu, alamun da waɗansu abubuwa kan iya ɗauka dangance da halin da ake ciki. Jam'iyar siyasar da jarida ke kawo wa goyon baya.

Coup d'Etat : Juyin mulki : Sake gwamnati ta hanyar amfani da ƙarfi, jirkice mulki da ƙarfi. Juyin mulki.

Coup de froid : 1/ Hatsari : 2/ gurɓacewar dangantaka tsakanin ƙasa da ƙasa tak ɗaya. Hatsari tsakanin ƙasashe masu iyaka da juna.

Coupable : Mai laifi : 1) Wanda aka kama da laifi. Kama mutum da laifi.

2) aikata aikin da jama'a ba su amince da su ba, na Allawadai. Aikata aikin Allawadai.

Coupe abusive de bois : Saran daaji : Kashin itatuwa ba ƙa'ida. Ma'aikata mai kula da kare muhalli na yaki da yan sara dawa.

Cour : Koti : mashara'anta. Lauyan da ke rataye ga wani koti, da ke hakunta hukumomi idan sun aikata mugun aiki.

Cour de justice : gidan juju : mashara'anta.

Cour de sureté de l'Etat : Kotin da ake hukunta masu cin amanar ƙasa.

Cour martiale : kotin soji : Kotin da ke yanke wa manya-manyan sojoji hukunci.

Cour suprême : Kotin ƙoli : babban koti.

Cour d'appel : kotin ɗaukaka ƙara.

Cour de cassation : kotin ɗaukaka ƙara mafi girma.

Cour des comptes : kwamitin ƙarwan kuɗi : mutanen da ke da nauyin ƙarwan ƙa'idodin lissafe-lissafen kuɗin ƙasa.

Haute cour : Koti ta musamman : Kotin da ke ƙumshe da y an majalasa, don yanke wa shugaban ƙasa ko ministoci hukunci idan sun ci amanar ƙasa.

Cour internationale de justice : kotin duniya ta shari'a : kotin da ke da nauyin yanke hunkunci tsakanin ƙasashe.

Couronnement (un roi) : naɗin sarki.

Courrier : sarki da gidan waya : Abin da ya shafi dukan wasiƙu da waɗansu sakonnai da ake gabatarwa ta hanyar gidan waya. Aika saƙo ta hanyar gidan waya.

Course aux armements : Neme-Nemen ƙayayyakin yaƙi: ƙoƙarin tattara kayan yaƙi masu hallaka ɗan Adam. Neme-Nemen mallakar kayayyakin yaƙi ya yi ƙamari a zamanin yakin cacar baki.

Court-terme : cikin gajeren lokaci : cikin taƙaitaccen lokaci, a lokaci kaɗan.

Court circuiter : ratse : Kewayawa, ɗaukar hanyar mafi sauƙi. Hanyar da ya bi ta ratse wa ƙa'ida.

Coût : kuɗin abu : yanda aka sawo shi. Yanda kuɗin gyare-gyare suka tashi.

Coutume : gargajiya : al'ada, abin sabo. Riƙe gargajiya.

Coutumier : Na gargajiya : wanda ya danganta da gargajiya. Shara'ar gargajiya.

Couverture sanitaire : Tamaiko kan fannin kiyaye samun lafiya : dukan ayyukan samun lafiya da jama'a ke buƙata waɗansu yankuna da ke cikin ƙasashe masu tasowa ba su samun cikakken tamaiko kan fannin kiyaye lafiya.

Couverture végétale : tsanwa : bakin yawan hakukuwa da itatuwan da ke fitowa a wani wuri.

Créance : Y'anci ; bashi : hanyar doka mai baiwa mutum izinin karɓar kuɗi ko wani abu daga hannun wani. Karɓar bashi.

Créancier : wanda ke bin bashi : mutunen da ya bada rancen ya waɗansu kuɗi, wanda tambayo kuɗi.

Créancier de l'Etat : Wanda ya tambayo gwamnatii.

Création : Kirkirawa/girkawa : tsirawa, kafawa, fitar da. Kafa masana'anta.

Création de fonds de solidarité : Girka asusun tamaiko : kafa wata kungiya mai kula da karɓar tarbacen masu kyakyawar niyya, da kuma gudanar da lissafin kuɗin. jawo hankali wajen girka asusun tamaiko.

Création des commissions d'enquêtes parlementaires : Kafa kungiyar bincike ta yan majalasa : kafa kungiya mai kula da tafiyar da bincike, da yin nazarin waɗansu harakoki a majalasar dokoki. Yan adawa na neman a kafa kungiyar bincike ta yan majalasa.

Crédibilité : daraja : Sake samun daraja.

Crédibilité internationale : samun daraja cikin kasashen duniya : samun amincewa da yarda daga wajen kasashen duniya.

Crédibilité nationale : samun daraja cikin kasa : samun amincewa da yarda ga yan kasa.

Crédit : 1) daraja, so, yarda. Nuna daraja wajen wani.

2) bashi. Samun bashi.

Crime : kashin kai : kashin kai na gangan. Aikata kishin kai.

Crime de droit commun : kashin kan da ake hakuntawa ba tare da an kauce wa dokoki ba.

Crime de génocide : Kishin kare dangi : tsara kashe-kashen wata kabila.

Crime de guerre : kazamin kishin kai a yaki : kishin maras kyan gani da ake aikatawa a lokacin yaki.

Crime de haute trahison : Aikin cin amana : laifin haɗa kai da wata kasar waje don cuta wa kasarsa.

Criminel de guerre : mai aikata kazamin kashin kai a yaki : mutunen da ke kashe mutane ba ji ba gani wajen yaki.

Crise : matsala : mawuyacin lokaci cikin tafiyar da rayuwar mutum, ko ta jama'a. Matsalar kuɗi.

Critère : sharaɗi : matakan da ake bi cikin tafiyar da wani nazari, ko wani abu daban. An aza tsautsauran sharuɗɗa wajen zaben yan takarar.

Critique : 1) **Gulma** : Cin naman mutum, sukar mutum, bata sunan mutum. Yin gulma.

2) **Na mawayacin hali** ; kazamtace.

Croissance : Bunkasa/tashe : ci-gaba, karuwa. K'asar da ke ci gaba.

Croissance économique : bunkasar tattalin arziki.

Croissance et développement : tashe da ci-gaba : samun ci-gaba.

Culpabilité : Halin laifi : halin wanda aka kama da laifi, mai laifi. Binciken da aka yi, ya tabbatar da laifin wanda ake zargi.

Culte : Kauna : bauta, son wani abu hiye da misali ; kaunar babban mutum.

Culture : Noma : 1) noman wuri, ko wata cimaka. Noman shinkafa.

2) **Al'adu**, tarbi'ar jama'a. Al'adun Afirka.

Cycle : Zagayo : tsarin wani abu : abubuwa masu faruwa lokaci zuwa lokaci dangance da yanda tsarinsu yake. Zagayon rani da damana.

D

Danger : haɗari : abin tashin hankali, mai kawo cikas. Nuna bambancin jaha yakan kasancewa babban haɗari wajen neman samun haɗin-kan yan ƙasa.

Dangereux : mai haɗari : abin da ke iya ƙashewa, wanda ke ƙumshe da haɗari. Magani mai haɗari.

Débat : Mafawara : tattaunawa kan waɗansu abubuwa. Cancanza miyau.

Mafawarar da aka yi a majalisar dokoki ta ƙayatar ƙwarai.

Débat politique : mafawara kan fannin siyasa : tattaunawa kan zantuttukan da suka shafi siyasa.

Débat riche et enrichissant : mafawara mai amfani : tattaunawa kan wani abu mai amfani, kuma mutane su kawo ra'ayoyi masu mahimmanci.

Déboucher : cin ma : samu, kaiwa, bayar da dama. An cin ma kwanciyar hankali cikin ƙasa a game da tattaunawar da aka yi tsakanin ministan ma'aikata da ƙungiyar yan ƙwadago.

Décadence : mutuwa/ raguwar ƙarfi : cima tashensa, wagircewa, taɓarɓarewa. Mutuwar jam'iyar ta biyo bayan rishin magance matsaloli da ke kunno kai cikin jam'iyar.

Décentralisation : tsarin rarrabe-rarraben ƙasa : Bai wa jahohi yancin kai. Rarrabe tsarin hukumanci.

Décentralisation administrative : rarraba tsarin hukumomi : sanya hakumanci cikin hannuwan zaɓaɓɓin mutane.

Décentraliser : rarrabawa, rage cinkoso : Bai wa jahohin ƙasa yancin kai. An shirya zaɓen ƙannanan hukumomi da na jahohi don rarraba tsarin hukumanci.

Décharger : Sauƙaƙewa : raba mutum da wani nauyi. Sauƙaƙa wa ɗan kaso ɗarmin da aka yi mishi.

Décision : hukunci : matakin da ke ga shugaban jamhuriya ya ɗauka dangance da yanda tsarin mulki ya ba shi yanci. Hukuncin da malamin shari'ar ya yanke ya gamsar da ɓangarorin biyu.

Déclaration : Sanarwa : jawabi wanda a cikin shi ake sanassar da wani abu, ake bayyanawa. Fitar da sanarwa.

Déclaration de guerre : kaɗa gangar yaƙi : jawabi wanda a cikin shi wata ƙasa ke nuna wa wata ƙasa ƙiyayya da kuma niyyar kai mata hari.

Déclaration universelle des droits de l'homme : Kalamin duniya gaba ɗaya na kare

hakkin d'an Adam : kundi mai kumshe da hakki daban-daban na d'an Adam da aka tsara ayar doka zuwa ayar doka.

Déclaration des biens : Bayanin kadarorin da mutum ya mallaka : bayanai kan dukan abubuwan da mutum ya mallaka.

Décloisonnement : soke shimge : kauce dukan abubuwan da ke kawo cikas cikin sadarwa.

Décoder : Warwarewa : Bayyana abin da wani zance ya kumsa dala-dala. Warware zance.

Décollage : Yunkura, tayar da tattalin arziki : samun ci-gaba cikin tattalin arziki.

Gwamnati ya shirya wani tsari don tayar da tattalin arzikin kasa.

Décolonisation : Neman y'ancin kai : Fita daga zama karkashin mulkin mallaka, samun y'ancin.

Déconcentration : Ragewar cunkoso : tsarin hukumanci mai saka wa jahohi hukumanci don rage cunkoso. Rage cunkoson hukumomi.

Découpage : rarrabawa : yayankawa. Rarraba jaha.

Décret : kudiri : matakin da hukumar zartarwa ke d'auka. Zaman taron ministoci ya d'auki kudurori da yawa.

Décrier : Yin allawadai : yin tir da wani abu, kin amincewa. B angaren y'an adawa sun yi. Alla wadai da wariyar da ake nuna wa magoya bayansu.

Dédommager : biya diyya ; rankawa : biyan mutum game da wata barna da aka yi mishi. Y'an kasuwa na neman a biya, masu diyya a game da barnar da ambaliyar ruwa suka yi masu.

Déduction : Cirewa : rage kud'i daga cikin wad'ansu masu yawa. Mai lissafin kud'i ya cire kud'i cikin albashi.

Défaitisme : Sarau : halin wanda ba ya sanya rai ga nasara, sararre. Sarewar d'an takara.

Défection : Fita : barin abokin kokowarsa, ko jam'iyarsa. Fita daga jam'iyarsa.

Défendre : karewa : hanawa, tsarewa. Kungiyar y'an kwadago ta tashi tsaye don kare hakkinta.

Défense : Tsaro : tsaro, hani. Sojoji na da nauyin tsaron kasa.

Déférer : Gabatar da : kai wanda ake zargi gaban koti, kai wani zance gaban hukumomin shari'a. An gabatar da mai laifin a gaban wata koti ta musamman.

Déficit : Gibi/karanci : rishi, rishin wad'ansu abubuwa dangance da bukatun jama'a. karamcin abinci.

Déficit chronique : babban karamcin (babban gibin) wani

abu rishi mai daɗewa na wani abu.

Déficit budgétaire : giɓin kasahin kuɗin ƙasa : abin da babu, rishi a cikin bidje don daidaita kuɗin da ke shiga cikin aljihun gwamnati da kuɗin da ake kashewa.

Déficitaire : Mai ƙaramci/mai giɓi : wanda ke ƙumshe da rishi, wanda bai zo daidai ba da hasashen da aka yi. Ƙaramcin kasahin kuɗi/Giɓin kasahin kuɗi.

Dégénérer : rikiɗa : ɓata ainahinsa, sake kama. Zanga-zangar ɗalibai ta rikiɗe a lokacin ɗauki-ba-daɗi tsakaninsu da yan sandar kwantar da tarzoma.

Dégradation : taɓarɓarewa : lalacewa. Taɓarɓarewar al'adu.

Dégradation des ressources naturelles : taɓarɓarewar albarkatun ƙasa : tabarɓarewa muhalli, gurɓacawar muhalli.

Dégradation de l'environnement économique : taɓarɓarewar tattalin arziki : kwantawar harakokin tattalin arziki, lafawar harakokin tattalin arziki.

Dégradation des relations diplomatiques : taɓarɓarewar dangantaka ta jakadanci tsakanin ƙasa da ƙasa. : gurɓacewar dangantaka tsakanin ƙasashe, cikas tsakanin dangantakar jakadanci.

Degré : Aji : hawa, gala. Ajin karatu

Délai : wa'adi : lokacin da ake ƙayyade wa mutum don shi aikata wani abu. Aikata wani abu cikin taƙaitaccen wa'adi.

Délégué : wakili : aikakke, jagora. Wakilin yan ƙwadago

Délibération : yanke shawara : nazari da bincike kan wata haraka kahin ɗaukar niyyar yanke shawara ga hukumomin shari'a. Bada sakamako.

Délibérer : yanke shawara : Yin nazari de lissafi kahin ɗaukar wata niyya. Yanke shawara kan wata haraka.

Délinquance : Shashanci/ dukan ɓatanci : abun da jama'a ke yin tir da shi. Tashi tsaye kan shashanci.

Délinquance juvénile : shashancin matasa : ɓatancin matasa.

Délit : Laifi : taka doka. Kama mutum da laifi.

Délits connexes : laififika masu alaƙa da juna waɗanda koti guda ke yanke wa shari'a.

Délocalisation des agents de l'Etat : tadin ma'aikatan gwamnati : sauya wa ma'aikatan gwamnati wurin aiki. Tadin ma'aikatan gwamnati.

Demande : tambaya : bayana abin da ake buƙata, abin da ake so. Gabatar da wata tambaya.

Démanteler : tarwatsawa : wargazawa ganowa, burkutawa, ɗagowa. Yan sanda sun

tarwatsar da wani gungun miyagu.

Démarche : hanya : dubarun cin ma wani guri. Ɗaukar wata hanya.

Démarche de motivation : hanyar (dubarun) ƙirƙirawa : hanyar da ke taimakawa wajen ƙirƙira wani abu.

Démarche participative : hanyar (dubarun) jawo hankali : hanyoyin da ake ɗauka da niyyar jawo hankali jama'a.

Démarche progressive : Hanyar (dubarun) ci-gaba : dubarun ci-gaba mai zuwa hawa-hawa.

Démarrage : somawa : farawa, tashi. An jinkirta somawar yaƙin neman zaɓe.

Démembrement : reshe : ɓangare, sashe, rabin wani abu. Ma'aikata mai kula da karɓar haraji, reshen babbar ma'aikatar karɓar lanho ce.

Démission : Murabus : raba kansa da wani nauyi, kasawa. Shugaban jamhuriya ya amince da murabus kin da paraminista ya gabatar.

Démobilisation : ragin kuzari: sarewa, ragin kuzari cikin wani abu kiki-kakan da ke dakwai wajen zaman tattaunawa ya rage wa masu yajin aiki kuzari.

Démocrate : ɗan demokaraɗiya : wanda ke son demokaraɗiya, wanda ya amince da matakan demokaraɗiya. Zama cikakken ɗan demokaradiya.

Démocratie : mulkin demokaraɗiya : tsarin mulki wanda a cikinshi jama'a ke zaɓen magabatanta. Mulkin demokaraɗiya ya shigo ƙasar Nijar a shekaru na alif ɗari tsara da tasa'in (1990).

Démocratie directe : tsarin mulki inda a cikinshi al'umma ke gudanar da cikakken yancinta.

Démocratie participative : tsarin mulki wanda a cikinshi jama'a ke sanya hannuwansu cikin harakokin jan ragamar ƙasa.

Démocratique : wanda ya dace da demokaraɗiya : wanda bai saɓa wa ƙa'idodin demokaraɗiya ba, mai daratta ra'ayin jama'a. Dokar da ta dace da demokaraɗiya.

Démographie : yawan mutane : ƙidayar mutane, lissafin mutane, ƙaruwar yawan mutane wanda ya wuce mizani.

Dénommer : laƙa suna : sanya wa wani abu suna, laƙa suna. Laƙa wa kampani suna.

Dénoncer : yin Allawadai : nuna ƙin amincewa, suka, yin tir yan ƙungiyar ƙwadago sun yi Allawadai da karyar da kampanonin ƙasa da aka yi.

Déontologie : ɗa'a cikin aiki: dukan ƙa'idodi, da kuma abin da ya wajabta kan masu wani aiki dangane da aikinsu.

Don bai wa kafofin watsa labaru cikakkar darajarsu, ya kyautu da y'an jarida su yi d'a'a cikin aikinsu.

Département : Dipartama : birni cikin tsarin rarrabe - rarraben jaha.

Gwamnan jaha ya shiga rangadi cikin dipartama.

Département ministériel : ma'aikatar minista : ma'aikata wadda minista ke shugabanci.

Dépendance : zama ƙarƙa-shi : zaman dogara. Halin wanda ake d'auke da shi, wanda ake mallaka. Zama ƙarƙashin wani.

Dépendance de l'extérieur : Dogara ga ƙasashen wajen: jiran komi daga ƙetare : halin ƙasar da ke tara wa ƙasashen waje hannu don biyan buƙatunta.

Dépendance économique : halin ƙasar da ke ƙarƙashin wata ƙasa kan fannin tattalin arziki.

Déplacement : rangadi : balaguro wanda yake yi cikin tafiyar da aiki. Shugaban ƙasa ya shiga rangadi cikin garuru-wan ƙasa.

Dépolitisation de l'adminis-tration : kawar da siyasa cikin ma'aikatun gwamnati : kawar da wariya mai alaƙa da siyasa cikin tafiyar da ma'aikatun gwamnati. Kawar da siyasa cikin ma'aikatu yakan kawo tsari cikin ma'aikatun ƙasa.

Dépolitisation de l'armée : hidda hannuwan sojoji daga cikin harakokin siyasa : haramtawa sojoji shiga cikin harakokin siyasa.

Sai sojoji sun hidda hannuwansu daga siyasa idan ana fatan su cika aikinsu da kyau.

Déportation : Hijira : korar mutum daga cikin ƙasa kan ra'ayin siyasa.

Zamanin mulkin kama-karya, y'an adawa da yawa sun yi gudun-hijira.

Dépositaire de : Mai nauyin : mai amanar, wanda aka bai wa adanon wani abu, wanda aka aza wa wani nauyi.

Shugaban jamhuriya shi ke da nauyin tafiyar da hukumancin ƙasa.

Dépôt : 1/ Ajiya. 2/ ma'adana: wurin da ake ajiyar wad'ansu abubuwa. Ma'adanar makamai.

Dépouillement : Bincike : lissafin ƙuri'un zaɓe bayan an kammala zaɓe. An nuna hara-kokin binciken zaɓe a gidan radiyo.

Dépouiller : bincikawa : lissafa ƙuri'un zaɓe. Bincikar ƙuri'u.

Député : d'an majalasa : dipite, mutunen da jama'a suka zaɓa don ya wakilce su a majalasar dokoki. Zaɓen d'an majalasa.

Dérapage : kaɓɓa : sakin hanya, fad'in wani zancen

wanda bai dace ba. Guje wa duk wata kaɓa.

Dérapage politique : kaɓɓa kan fannin siyasa : aikata wani abin da bai dace ba kan fannin siyasa.

Déroulement : gudana : halin aukuwar waɗansu abubuwa, wakana. Bincike ya nuna yanda harakokin suka gudana.

Désapprobation : rishin amincewa : ƙin yarda, adawa kan wani abu, yan ƙwadago ba su amince da ayar dokar da aka fitar ba.

Désarroi : ɓacin rai zullumi : ɓacin rai, zama cikin zullumi

Désenclavement : Hidda kaɗaici : magance halin keɓewar wuri ta hanyar kyautata hanyoyin sadarwa.

Désengagement : fidda hannu : fitar da hannunsa daga cikin wani abu, ƙaurace wa abun. Gwamnati ta fitar da hannuwanta daga cikin waɗansu harakoki.

Désengagement de l'Etat : fidda hannun gwamnati : yayewa : halin da gwamnati ke barin ɗaukar wani nauyi da ya rataya a kanta.

Désengager : fitar da hannu: tada alƙawali, halin da babu ruwan mutum cikin wani abu. Jam'iyarshi ta nuna da babu hannunta cikin sanawar da ya gabatar.

Déséquilibre : ƙaramci : rishin daidaituwar wani abu, rishin isarshi. Ƙasar Nijar ta samu gudummuwar cimaka don magance ƙaramcin abinci da take fuskanta.

Désert : Hamada : yanki mai wuyar zama saboda rishin kyaukyawan yanayi. Hamadar Tenere.

Déserter : yin gudu : tserewa, nisantar wuri, barin wuri. Rishin kwanciyar hankali ya sanya jama'a sun yi gudu daga jahar.

Désertification : mamayar Hamada : wurin da ya ƙeƙashe saboda rishin kyaukyawan yanayi. Yaki da Hamada.

Désertique : ƙeƙasasshe : wanda ya bushe, mai fari. Ƙeƙasassar jaha.

Désister : murabus : sake shawara, jaye sunansa. Ya samu an zaɓe shi saboda abokin takararshi ya yi murabus.

Désobéissance civile : ƙin daratta doka : ƙin daratta doka ga jama'a, bori, rishin bin tsari. Yan adawa suna kiran magoya bayanta da su ƙi daratta doka.

Dessein : guri : fatan da ake son cin ma, manufa. Yin wani guri.

Dessein national : gurin ƙasa: cikakken abin da ƙasa ta sanya gaba, wanda take son cim ma.

Destabilisation : Rikita/tunkuɗa : tarwatsawar hukumomin ƙasa, kawo tangarɗa. Ana shirya zanga-zanga jika-da- jika da

niyyar tunkuɗar da gwamnati.

Destabilisation de la nation : kawo rikice-rikice cikin ƙasa: sanya ruɗani, da zanga-zanga cikin ƙasa.

Destin : Ƙaddara : rabo, makoma, abin da ke aukuwa cikin rayuwar mutum ba tare da ya buƙace shi ba. Abin da yake ƙaddara ga jama'a.

Destinataire : Mai sabtu : mutunen da aka aiko wa wani saƙo. mai sabtun wasiƙa.

Destituer : tsigewa : sabke mutum daga kan wani matsayi, hiddawa. Tsige wani wakili.

Détacher : ratayawa : kai ma'aikaci ga wani aiki, sanya shi cikin wata ma'aikata. Rataya ma'aikaci ga ga wata ma'aikata.

Détenir : tsarewa : tsare mutum gidan kaso, ɗaure shi. tsare ɗan kaso.

Détente : sauƙi : samun kwanciyar hankali kan halin zamentakewa da kan fannin siyasa. Yarjejeniyar da aka cin ma a game da zaman tattaunawar da aka yi ya kawo sauƙi cikin ƙasa.

Détention : r: tsarewa, sanya mutum gidan kaso. Zama cikin halin ɗauri.

Détenu : ɗan kaso : mutunen da aka ɗaure gidan kaso.

Détenu politique : Mai kason ra'ayin siyasa.

Détenu de droit commun: wanda aka ɗaura kan ya taka doka : mutunen da aka ɗaura kan laifin da ba ya da alaƙa da siyasa.

Détenu politique : mutunen da aka ɗaure kan ra'ayinshi na siyasa : wanda aka ɗaure a dalilin ra'ayinshi na siyasa da ya gabatar.

Détermination : cikakkar niyya. 1) ɗaukar niyya aikata wani abu. Aikata wani abu da cikakkar niyya.

2) **Ƙayyadewa :** iyakancewa, ƙa'idewa. Ƙayyade gurori.

Détermination des moyens : ƙayyade matakai : ƙayyade hanyoyin da za a ɗauka.

Détérioration des termes de l'échange : ƙayyade halayen masanyar kuɗi : daidaitar da harakokin canjin kuɗin cikin duniya.

Déterminer : ƙayyadewa : kimantawa, lissafawa. Ƙayyade sharuɗɗan cim ma guri.

Détournement des deniers publics : handamar dukiyar ƙasa : satar kuɗin ƙasa ; cin kuɗin ƙasa. Ana tuhumar shi saboda ya handami kuɗin ƙasa.

Détourner : cikin kuɗi : satar wani abu, yin sama da faɗi. Cin kuɗi.

Détracteur : ɗan sukar ra'ayi : mutunen da ke ɓata sunan wani, mai karya wa wani daraja,

adawa y'an sukar ra'ayin gwamnati ba su ci nasara ba.

Détriment : maimaki : zaben aikata wani abu cikin abubuwa da yawa ; aikata wani abu maimakin wani.

Dette : bashi : bai wa wani rancen kud'i. Biyan bashi.

Dette de l'Etat : bashin kasa: dukan kud'in da ake bin kasa.

Dette extérieur : bashin da kasar wajen ke bin wata kasa : dukan rancen da wata kasa ta d'auko kasashen waje.

Dette interne : bashin cikin gida : dukan bashisshikan da y'an kasa ke bin gwamnati.

Deuxième lecture : sake bincikar doka : bincike aji na biyu da y'an majalisar dokoki ke yi wa doka. Gabatar da doka don sake bincikar ta.

Dévalorisation : banzatar da: rage darajar wani abu, rena shi. Banzatar da al'adu.

Dévaluation : karya daraja : rage darajar kud'in kasa dangance da darajar zinariya. Karya darajar SFA (C.F.A).

Développement : ci-gaba : wadata, bunkasa. Ci-gaban kasa.

Développement à la base : ci-gaba daga al'umma : tsarin da ake shinfid'awa don kyautata rayuwar jama'a.

Développement accéléré : gaggautaccen ci-gaba : samun ci-gaba cikin karamin lokaci, da gaggawa.

Développement économique et social : Bunkasar tattalin arziki da kyautata rayuwar jama'a : bunkasar tattalin arziki da samun wadatar jama'a.

Développement intégré : ci-gaba da kai : ci-gaban da ke amfanar masu tanada shi.

Développement local : ci-gaban jaha : tsarin ci-gaba don jin dad'in rayuwar mutanen jaha.

Développement participatif : gudun-muwar kowa da kowa don ci-gaba : tsarin ci-gaba mai bukatar goyon bayan dukan y'an kasa.

Développement rural : ci-gaban karkara : shinfid'a tsarin raya karkara.

Devenir : zuwa gaba. Makoma : kwanakin gaba, abin da za ya faruwa a gaba. Ya kyautu dukan y'an kasa su mayar da hankalinsu kan makomar kasa.

Dévise : take : 1) Kalamai masu nuna gurin da aka sanya gaba. Zumunci, aiki da ci-gaba shi ne taken Nijar.

2) Kud'in kasa dangance da sauran kud'in kasashe.

Devoir : wajibi : nauyi. Abin da ya zama tilas. Aikata abin da ya wajabta kan mutum.

Devoir sacré : Muhimmin waji-bi : wajibin da ake darattawa kan gaskiya, wanda ba a iya takewa.

Devoirs des Etats : Nauyin da ke kan gwamnati : Abin da ya wajabta kan gwamnati dangance da jama'a, ko da wad'ansu ƙasashe.

Dévouement : Dukufa (bada) kai : yin namijin ƙoƙari, aikata wani abu kan gaskiya, tsakani da Allah. Dukafa (Bada kai) ga soja don tsaron ƙasarsa.

Diagnostiquer les insuffisances : bincikar matsaloli : ƙididdige abubwan da babu, abin da ya rago cikin wani abu. Ya kyautu a binciki matsalolin da ke akwai don warware su.

Dialecte : yare : karin harshe da yake sawaya daga wata jaha zuwa wata jaha. Ya kyautu a yi nazari kan yaren ƙasa daban-daban don daidaita harsunan ƙasa.

Dialogue : Tad'i/tattaunawa : canza miyau tsakanin mutane, don cin ma wata yarjejeniya. Gwamnati na fatan ganin an koma tattaunawa da shi da y'an sandika.

Didactique : (Na wa'azi) fasahar koyo da bada ilimi : mai saukaƙe koyarwa, abin da ake wallafa don koyarwa. Littafin fasahar koyo da bada ilimi.

Difficultés de trésorerie : matsalar kud'i cikin ƙasa : matsalolin rishin kud'i : fuskantar matsalolin rishin kud'i.

Diffusion des informations : watsa labarai : sanasar da jama'a kan wad'ansu abubuwa ; bayar da labaru. Tabbatar da halin watsa labaru.

Dignité : Mutunci : girma da darajar da ake bai wa mutum. Kare mutuncin d'an Adam.

Dignité du peuple : mutuncin al'umma : d'arajar al'umma, mutuncin ƙasa.

Dignité humaine : mutuncin d'an Adam : darajar d'an Adam.

Dilapidation : ɓana : ɓata wani abu, yin amfani da shi ba kan gado, pacaka. A na zargin shi da ɓannatar da kud'in ƙasa.

Dilapider : ɓannatar da : banzatar da, wulaƙantar da, amfani ba kan gado, sata. Ɓannatar da dukiya.

Diligenter une enquête : gudanar da bincike gaggauta: tafiyar da bincike tare da himma. Y'an sanda sun maida himma ga gudanar da bincike don gano mutanen da suka aikata kishin kai.

Diplomate : Mai'aikacin huld'ar jakadanci : jakada ; mutanen da ke da nauyin wakillar d'asarshi a ƙasar waje. An karɓi jakada a fada.

Diplomatie : Aikin Jakadanci : aikin ya shafi wakilci, wanda ye shafi dangantaka tsakanin

ƙasa da ƙada. Amfani da hanyar jakadanci don warware wata matsala.

Diplomatique : Na jakadanci : wanda ke da dangantaka da jakadanci aikin jakadi. Dangantaka ta jakadanci.

Diplôme : Digiri : takardar shaida samun ci-gaba da karatu, da karatu. Damƙa wa mutum digiri.

Directeur : Darakta : mutanen da ke shagabantar wata ma'aikata. Daraktan masana'antar ya shirya wata mafawara da sauran ma'aikatan.

Directeur de Cabinet : Shugaban fada : mutanen dake shugabantar wata fada.

Directeur de l'administration centrale : darakta na wata cibiyar hukuma : darakta mai jan ragamar wata babbar mahakunta.

Directeur général : babban darakta : babban shugaban wata ma'aikata.

Direction : shugabanci : gabata, wurin tafiyar da hakumancin wata ma'aikata. Wurin shugabancin wata ma'aikata.

Direction de campagne : magabatar yaƙin zaɓe : buro mai kula da tafiyar da yakin zaɓe.

Dirigeant : shugaba : mahukunci, mai jan ragama, magabaci. Shugaban ƙasa ya gayyaci shuwagabanin jam'iyu daban-daban.

Discipline : ladabi : 1/ dukan kyaukkyawan halaye da ke kawo tsari cikin zaman jama, darattawa. Nuna ladabi ga ƙungiyar sandika.

2/ **Sashen ilimi, na karatu.** Sashen ilimin kimiyya.

Discours : jawabi : yin bayyanai a bainar jama'a a albarkacin wata mafawara. Shugaban ƙasa ya karanta jawabin buɗa zaman taron majalisar dokoki.

Discours programme : jawabi kan tsare-tsare : jawabi wanda a cikinshi ake bayyana tsare-tsaren da ake da niyyar gabatarwa.

Discréditer : ɓata suna : shirya ƙaryace-ƙaryace kan mutun, kada girma. ɓata sunan abokin takara.

Discrimination : bambanci : nuna son rai tsakanin jama'a, raba ɗaya, biyu. Mata sun tashi tsaye don yaƙar bambancin da suke fuskanta.

Discrimination à l'égard des femmes : nuna wa mata bambanci : ƙwaruwa, mayar da mata ƙarƙashin maza a ko'ina.

Discrimitation ethnique : ƙabilanci : nuna wariya ga al'umma dangance da ƙabila, ɗabilanci.

Discrimination raciale : bambancin launin fata : Nuna wariya ga al'umma dangance da launin fatarta.

Disposition : mataki : ƙa'idodin da doka ko wata yarjejeniya ta tsayar da. Matakan ayar doka.

Disposition transitoires : matakan wucin gadi : matakai, ko ƙa'idodin da doka ke tsayar da don amfani da su cikin wani gajeran lokaci.

Dispositions finales : matakai na ƙarshe : matakan da aka amince da su, kuma ana aiki da su har kullum.

Dissolution de l'Assemblée Nationale : Rushe majalisar dokoki : ɗaukar ƙudiri na tsayar da wakilcin dipitoci a majalisar dokoki. Shugaban ƙasa na da ɣancin rushe majalisar dokoki.

Dissuader : razanawa : kashe jiki ; bai wa mutum tsoro, turza mutum tsatsauran matakar tsaron da ɣan sanda suka ɗauka ya razana masu zanga-zanga.

District : unguwa : shiyya. A shekarar alif ɗari tara da tamanin da biyar aka fara rarraba garin yamai a unguwa-unguwa.

Divergence : Bambanci rishin jituwa ; rishin gane wa juna. Bambancin ra'ayi.

Diverses : Iri daban-daban : iri-iri, da yawa barkatai. Aji iri daban-daban na koyarsuwa.

Diversification : sassauyawa : garwayawa, cancanzawa. Sassauya abubuwa.

Diversité : Halin yawan iri : abin da ke iri da yawa. Yawaita al'adu.

Diversité, symbiose, synthèse des forces sociales : yawantawa da daidaitar ra'ayuyyukan jama'a.

Division : 1/ Gungun ma'aikatu : haɗuwar ma'aikatu da yawa wuri guda. Shugaban gungun ma'aikata.

2/ **Baraka,** samun ɓaraka cikin jam'iya.

Division territoriale : tsarin jahohi : tsara ƙasa a yankuna-yankuna. Tsarin jahohin ƙasa.

Doctrine : Ra'ayi : dukan ra'ayuyyuka da wani tsari ke bayyanawa. Zama ma'abucin wani ra'ayi.

Document : Mahujjaci : littafin da aka wallafa mai bayar da bayanai, ko waɗansu abubuwa na tarihi. Aika mahujjaci ta datattar hanya.

Document officiel : takarda (mai cikakkar shaida) ta hakuma : takardar da ta hito daga hannun hukuma, wadda hakuma ta sanya hannu kanta.

Dogmatique : Maras kolo-kolo : wanda ke bayyana ra'ayinshi ba tare da wani ɓoyon komi ba. Mutum maras kolo-kolo.

Doléance : koke-koke : yin ƙorahi kan wanni abu, gabatar da buƙatunsa, yin Allawadai kan wani abu. Ma'aikata sun gabatar wa minista koke-kokensu.

Domination : Mallaka/ mama-

ya : danniya, hin ƙarhi. Mallakar miji.

Dominer la vie politique nationale : ɗaukar hankalin jama'a kan fannin siyasar ƙasa : Zancen shirya zaɓe ya ɗauki hankalin jama'a.

Dommages et intérêt : Diyya: kuɗin da ake bai wa wanda aka amshi wata ƙadararshi don amfanin jama'a, ko kuma wanda aka yi wa ƙaƙe. Kuɗin diyya.

Donner en gage : Jinginawa (Sanyawa jingina) ; sanya wata ƙadara cikin hannun wani da niyyar sake karɓar ta bayan biyan kuɗin da aka amsa. Sanya wani abu jingina.

Donner l'exemple : Zama abun koyi : fara yin abu na gari, aza waɗansu kan kyakkyawar hanya. Shugaban ma'aikatar ya zama abun koyi ga sauran abokan aikinshi kan abin da ya shafi tafiyar da harakokin kuɗi.

Dossier : Kundi/takardu : dukan takardu masu shaida da ake tattarawa wuri guda don tafiyar da wata haraka. Binciken takardu.

Dotation : Tanadi Kyauta : agaji na kuɗi, ko na waɗansu ƙadarori. An yi wa ƙungiya mai kula da shirya zaɓen ƙananan hukumomi da na jahohi tanadin kuɗi.

Doyen : Mafi daɗewa shugaba : wanda ya fi daɗewa a wani wuri, ko cikin wata ƙungiya. Shubagan kotin ɗaukaka ƙara.

Dramatique : Mummuna ; maras kyan gani, mai tayar da hankali. A game da ƙaramcin ruwan sama, bisashe na shirin shiga cikin mummunan hali

Drapeau : Tuta : ƙyalle mai launi guda ko da yawa masu nuna alamun ƙasa. Yin ƙasa-ƙasa da tutar ƙasa.

Droit : Y'anci : 1/ wanda bai saɓa wa ƙa'idodi ba, abin da al'umma ba ta haramta ba. Yin abin da ya dace da doka.

2/ **Dokokin ƙasa** : girmama dokar ƙasa.

. **Droit pénal : Dokokin hunkuntawa** : sashen ilimin shari'a mai ƙayyade hukuncin da ya kyautu ga mutum dangance da laifin da ya aikata.

. **Droit à l'éducation : yancin samun horo da ilimi** : nauyin da ya rataya kan gwamnati na bai wa kowane ɗan ƙasa damar samun horo da ilimi.

. **Droit à l'information : yancin samun labaru** : damar da ke ga kowane ɗan ƙasa da shi shaƙi labaru ta ko'ina.

. **Droit à la justice : yancin ƙara** : damar da ke ga kowane ɗan ƙasa na tuntuɓar shari'a idan hali ya kama.

. **Droit à la propriété : yancin mallakar abin kansa** : yancin da ke ga kowane ɗan ƙasa na mallakar abin hannunshi.

. **Droit à la santé : yancin samun ƙoshin lafiya** : yanci da ke ga kowane ɗan ƙasa na samun ƙoshin lafiya.

. **Droit à la sécurité : yancin zama cikin kwanciyar lafiya** : yancin da ke ga kowane ɗan ƙasa na ganin gwamnati ya tabbatar mishi da kwanciyar lafiya.

. **Droit à un recours : yancin ɗaukaka ƙara** : yancin da ke ga kowane ɗan ƙasa na samun halin ɗaukaka ƙara bayan an riga an yanke shari'a.

. **Droit administratif : ilimin shari'ar aiki** : sashen ilimin shari'a mai nazari kan tsarin tafiyar da aikin hakumanci.

. **Droit au travail : yancin samun aiki** : yancin da ke ga kowane ɗan ƙasa na samun aikin yi.

. **Droit civique : yancin ɗan ƙasa** : yancin da shari'a ta tanada wa kowane ɗan ƙasa cikin gudanar da aikin ƙasa.

. **Droit commercial : ilimin shari'ar kasuwanci** : sashen shari'a mai nazari kan dokokin tsarin kasuwanci.

. **Droit coutumier : shari'ar gargajiya** : shari'ar da ta danganta da gardajiya, dukan ƙa'idodin da suke na gargajiya.

. **Droit d'appel : yancin ɗaukaka ƙara** : yancin da ke ga kowane ɗan ƙasa na samun halin ɗaukaka ƙara bayan an yanke shari'a.

. **Droit d'asile : yancin samun mafaka** : yanci da ke ga kowane ɗan ƙasa na samun mafaka a wata ƙasa.

. **Droit d'auteur : yancin mawallafi** : 1/ yancin bugun gaba da abin da mawallafi ya wallafa.

2/ hakkin da ake ba shi a dalilin abin da ya wallafa.

. **Droit de grâce : yancin yin afuwa** : yancin da tsarin mulki ya tanada wa shugaban ƙasa na yin afuwa.

. **Droit de grève** : yancin shiga yajin aiki : tabbatacen yancin ma'aikata na dakatar da aiki har sai an shafe masu kukansu.

. **Droit de l'homme : Hakkin (yancin) ɗan Adam** : kiyaye mutumcin ɗan Adam.

. **Droit de manifestation : yancin shirya zanga-zanga** : yancin shirya jerin gwano don nuna wani hali na bakin ciki ko na farin ciki.

. **Droit de parler et d'écrire librement : yancin wallafawa da samun damar tofa albarkacin bakinsa** : samun damar wallafawa da tofa albarkacin bakinsa ba tare da wani shakku ba.

. **Droit fondamental : Cikakken tsarin shari'a** : tsarin shari'a

mai mahimmanci, mai tabbatar da yanci.

. **Droit international** : Tsarin shari'a ta duniya : dokokin shari'a da suka shafi duka duniya.

. **Droit juridique : Dokokin shari'a**: sashen ilimin shari'a mai nazari kan ƙaidodin masu tsarinta shari'a.

. **Droit public : Dokokin tsarin hukumomi** : sashen ilimin shari'a mai nazari kan dangantaka tsakanin hukumomi da talakawa.

Durée de législature : wa'adin aikin majalisar dokoki : tsawon lokacin da aka yanke wa majalisar dokoki. A ƙasar Nijar wa'adin aikin majalasar dokoki ba ya wuce shekaru biyar.

Durée de travail : tsawon lokacin aiki : tsawon lokacin da ma'aikaci ke yi kafin shi yi ritaya, ko kuma lokacin da yake ƀatawa wajen aiki kowace rana. An ƙayyade awa goma sha huɗu na tsawon aiki kowace rana.

Dynamique : Mai cika aiki/ mai ƙwazo : mai son aiki, mai ƙoƙori. Shugaba mai cika aiki.

Dynamisme : Kuzari/ƙwazo : ƙwazo da dubara. Waɗansu jam'iyun siyasa ba su da kuzari. (ƙwazo).

E

Ebauche : Somawa : farawar wani abu, gwadi. Aikin da masana'antum biyu suka yi niyya yana cikin halin somawarshi.

Echange : Masanya : 1/ canjin wadansu abubuwa da wasu, furfure. Masanyar yan kaso.

Echanger : yin masanya : 1/ jagwal, yin furfure. Yin masanyar wadansu abubuwa.

2/ Yin dangantaka kan fannin sadarwa. Yin masanyar wasikun jakadanci.

Echantillonnage : Neman Masu ra'ayi guda : dubarun gano mutanen da ke da ra'ayi guda a game da wani al'amari. An gano bakalin shugaban kasa ta hanyar neman masu ra'ayi guda.

Echéance : Karshen wa'adi : wa'adin da ake yanka wa wani abu, lokacin da wani abu za ya faruwa. Dan kasuwar ya biya bashinshi kafin karshen wa'adi.

Echéance électorale : lokacin zabe : ranar da za a shirya zabe.

Echec : Rishin cin nasara : hasara, gazawa, fadduwa, rishin ganin hasken wata haraka. Rishin cin nasara ga jarabawa.

Echelle : Hawa-hawa : tsarin jama'a dangance da matsayinsu daban-daban, ko mukaminsu. Hawa-hawan jama'a.

. Echelle de valeur : hawa-hawa ga daraja : hawa-hawa, bi-da-bi daga mafi daraja zuwa na karkashi.

. Echelle locale : hawa-hawan jama'a cikin yanki : hawa-hawan jama'a dangance da hallayensu a cikin wani gari.

. Echelle national : hawan-hawan jama'a cikin kasa; hawan-hawan jama'a cikin kasa dangance da halayensu.

Echellon : gala ; galar ma'aikaci, gàlar soji.

Eclairage : haske ; dubarun kwatance, , ra'ayi. Bayanan da jujun ya gabatar sun kawo haske cihin tafiyar da ayyukan koti.

Ecologie : Ilimin lafiyar yanayin kasa : ilimin kimiyya mai nazari kan rayuwar dan Adam kan doron kasa.

Economie : tattalin arziki : 1/ duk abin da ya shafi barakokin sarrafa abubuwa da amfani da su, harakokin kasuwanci cikin kasa. Arzikin kasa.

2/ Tafiyar da harakokin kudi cikin ka'ida. Yin tsimin dudi.

. Economie de marché : hujja jari : tsarin ci-gaba, mai hihita jari gwamnati ga yaye masana'antu su koma masu zaman kansu.

. Economie mondiale : arzikin duniya : dukan abubuwan da

suka shafi arziki a duniya.

. **Economie nationale : arzikin ƙasa** : dukan abubuwan da suka shafi mallakar ƙasa.

Ecouler : sayar da ; Samun cinali, sayar da wani abu har shi ƙare. Kungiyar manoma ta sayar da duk amfanin da ta noma.

Ecrouer : ɗaurewa : rufewa, tsarewa. Ɗaure mugu a gidan ƙaso.

Edicter : kafawa ; fitar da doka, ko waɗansu ka'idodi, tabbatar da. Majalisar dokoki ta kafa wata doka da za a bayyanawa a cikin mujallar hukuma.

Edification : Girkawa : ginawa, tsarawa. Gwomnati da ƴan tawaye sun ɗauki niyyar haɗa gwiwa don girka ƙarfafa kwanciyar hankali.

. **Edification d'une société : ginin ƙasa** : girka tattalin arzikin ƙasa da kyautata zayuwar jama'a.

Editorial : Sharhi : gabatarwa da ke sashen farko na jarida. Shugaban mawallafa shi ke da nauyin wallafa sharhin jarida.

Education : Aikin bayar da ilimi da horo : dukan harakokin da suka shafi hanyoyin bayar da ilimi da horo don ci-gaban ɗan Adam.

. **Education de base** : Horon farko : Aikin bayar da ilimi da horo ga ƙananen yara, tarbi'antar da yara.

. **Education et développement : Amfanin ilimi da horo cikin ci-gaban ƙasa** : ilimi mai taimakawa wajen cin ma jin daɗin rayuwar jama'a, mai sanyawa a cim ma tattalin arziki cikin ƙasa.

. **Education formelle : Horo a cikin makarantun boko** : horon da ake samu a cikin makarantu daidai yanda hukuma ta tsara.

. **Education informelle : horon gida** : horon da mutum ke samu cikin duniya ba tare da ya je makarantar boko ba. Horon gida.

. **Education non formelle** : horo daban da na boko : samun ilimi da horo da koyon waɗansu ayyukan hannu a cikin wurare daban da na boko.

. **Education spécialisée : Horon naƙasassu/Horo na musamnan** ; samun ilimi da horo a cikin wurare na musamman.

. **Education morale : tarbi'a** ; bai wa yaro aƙida da halaye na gari masu amfanar shi cikin zaman shi na duniya.

. **Education nationale : Ma'aikatar ministan ilimi da horo** : ma'aikata mai kula da harakokin bayar da ilimi da horo cikin ƙasa.

Effectif : Yawa ; bakin mutanen da aka ƙayyade wajen samun wani horo. yawan mutanen da ke ciki wani aji.

Effet rétroactif : Mai shafar abubuwan baya ; mai iya zuwa

ya dawo,wanda ke iya shafar abin da ya shuɗe. Dokar da y'an majalasar suka amince da ita kwanakin nan, ba ta da halin shafar abubuwan baya.

Efficace : Mai ƙarfi ; Mai amfani; mai cika aiki, na ƙwarai. Magani mai ƙarfin.

Efficience : Amfani : ƙarfi, inganci mai kawo abin ƙwarai. Amfanin tattalin arziki.

Effort : ƙoƙari : aikata wani abu da cikakkar himma, da zuciya guda don cin nasara a kai. Ɗan makaranta ya yi cikakken ƙoƙari don cin nasara ga jarabawa.

Egalité : daidaici : halin babu wanda ya fi wani, inda mutane suke ɗaya. Tsarin mulki ya amince da dukan y'an ƙasa daidai suke a gaban doka.

Elaboration : Wallafawa/ shiryawa : yin nazari kan wani abu don tsarinta shi ɓangarori biyu masu gaba da juna sun shirya tsari na zaman lafiya.

Elan : ɗaukakawa : yunƙuri : sanya wani aba ya ci-gaba. Ɗaukaka tattalin arziki. Yunƙuro da tattalin arziki.

Election : zaɓe : wakiltar mutun guda ko mutane da yawa ta hanyar jefa ƙuri'a. Shirya zaɓe.

. Elections municipales : zaɓen wakillan birane : zaɓen wakillai waɗanda za su ɗaukar nauyin tafiyar da harakoki a cikin birane.

. Elections anticipées : gaggautaccen zaɓe : zaɓen da ake shiyawa kahin lokacin da aka ƙayyade ya isa.

. Elections législatives : Zaɓen y'an majalasar dokoki: Zaɓen wakillan jama'a a majalisar dokoki.

. Elections locales : Zaɓen wakillan ƙayuyyuka : zaɓen wakillan da za su tafiyar da harakoki a cikin ƙauyuyyuka.

. Elections présidentielles : Zaɓen shugaban jamhuriya : zaɓen wanda za ya zama shugaban jamhuriya ta hanyar jefa ƙuri'a.

. Elections régionales : zaɓen wakillan jahohi : Zaɓen wakillan da za su tafiyar da harakokin jaha da hanyar jefa ƙuri'a.

Electorat : Masu zaɓe : jama'a masu zaɓe. Samun masu zaɓe.

Elément : ɗa : 1/ abubuwa guda-guda da ke haɗuwa su bada wani abu. Ɗa guda daga cikin waɗansu abubuwa.

2/ Mutanen da ke cikin wani gungu, ko rukuni. Y'an sandar kwantar da tarzoma.

Elevage : Kiyo : tattalin dabobi don cin amfanin su. Ya samu izinin dakatar da aiki har tsawon wani lokaci don yin kiyon bisashe.

Eleveur : Makiyayi : mutunen da ke kiwo. Ruggar makiyaya.

Eligibilité : Sharuɗɗan zama ɗan takara : cika ka'idodin zama ɗan takara. Tsayar da sharuɗɗan zama ɗan takara.

Eligible : Wanda ake iya zaɓe : mutunen da ya isa zama ɗan takara, wanda ya cika dukan sharuɗɗan. Ba dukan ɣan takara ba ne ake iya zaɓe.

Eliminatoire : tankaɗe da rairaya : zaben gwanai ta hanyar tankaɗe da rairaya. Kwombalar tankaɗe da rairaya.

Elire : Zaɓe : wakiltar mutum ta hanyar jefa ƙuri'a. Kowa da kowa ya jefa ƙuri'arshi don zaben shugaban jamhuriya.

Elite : ƙwararre : Shahararre, duk mutumen da aka sani da iya wani abu hiye da kowa, wanda ya fahimci wani abu. Yana cikin ƙwararrun ɣan siyasar jam'iyarshi?

Elu : zaɓaɓɓe : wakili, wanda aka zaɓa ta hanyar jefa ƙuri'a ; wanda aka wakilta. Wakillan jama'a.

. **Elu local : konsayye** : mutumen da aka zaɓe da sunan kwamin, ko dipartama, ko jaha.

. **Elu national : Dipite, ɗan majalisa** : mutanen da aka zaɓa da sunan ƙasa.

Emanation : buƙata, Abun ya fito daga : abin ke tasowa dage wani abu, mai fitowa daga wani abu. Cikakkar buƙatar jam'a.

Emancipation : samun ɣanci : kuɓuta, ceton kansa daga wata millaka, ko daga waɗansu zantuttuka maras hujja ; samun ɣancin kan mata.

Emaner : fitowa daga hannun wani : Iko ya fito daga hannun al'umma.

Embargo : takunkumi : matakan muzgunawa da ake ɗauka kan wata ƙasa don haramta mata huldɗa da sauran ƙasashe. Shugabannin ƙasashen da suke cikin ƙungiyar ɣan ba ruwanmu suna neman a ɗaga takunkumin da aka sanyawa ɗaya daga cikinsu.

. **Embargo économique : takunkumin karya tattalin arziki** : haramta huldɗa kan fannin tattalin arziki da wata ƙasa don karyar da tattalin arzikinta.

Emblème : Tambari : wata shaida mai dauƙe da wani take. Tambarin jam'iyar siyasa.

. **Emblème nationale** : tambarin ƙasa.

Emigration : Dandi, hijira : shiga uwa duniya, barin ƙasarsa. Tashe-tashen hankula da yunwa sune ka sanya mutane shiga yawan dandi cikin ƙasashen Afirka.

Eminent : cikakke : mashahuri, wanda ya zarce, mai girma. Yin cikakken ƙoƙari.

Emissaire : Manzo : Ɗan aike: Aikakke, mutumen da ke ɗauke

da wani saƙo. Shugaban ƙasa ya karɓi wani manzo na ƙasar waje.

Emission : shire-shiren ƙafofin watsa labaru : tsare-tsaren kafofin watsa labaru. Shire-shiren gidan radiyo.

. Emission de monnaie : buga kuɗi : sanya kuɗi cikin harakoki, cikin hada-hada.

Empêchement absolu : tsananin halin rishin dama, : hali wanda a cikinshi mutum ba ya iya aikata abin da ya saba, kasawa. Muƙaddashin ɗan majalasa ke maye kujerar ɗan majalasa da zaran ya shiga cikin tsananin halin rishin dama.

Emploi : Aiki : sana'ar da ke bai wa mutum damar biyan buƙatunshi. Neman aiki.

. Emploi civil : aiki farar fula : aikin da ya shafi farar fula.

. Emploi militaire : aikin soji : aikin da ya shafi sojoji.

. Emploi public : aikin jama'a : aikin da ya shafi tafiyar da harakokin ƙasa.

Emprisonnement : Ɗauri : tsare mutum gidan kaso, hana wa mutum walwala har tsawon wani lokaci. Kungiyar kare hakkin ɗan Adam A.N.D.D.H. tana Allawaddai da ɗauri na son rai da aka yi wa masu zanga-zangar da aka kama.

En cours : Da ake ciki: lokacin da ake yin wani abu, tsakar yi ; shekarar bana da ake ciki, tana bai wa manoma zaton samun alheri.

En gestation : da ake cikin shiryawa : wanda aka fara shiryawa sanarwar da za ta tabbatar da haɗin gwiwar jam'iyan biyu tana cikin shiri.

En pleine égalité : Matsayi guda : cikakken daidaitai, daidai da daidai, cikin adalci. Dukan ja'iyum siyasa matsayinsu guda a gaban doka.

En vertu de : Dangance da : a game da, da suna. Duk mutumen da ya aikata laifi, za a hukunta shi dangance da yanda doka ta ƙayyade.

En vigueur : Wanda ake aiki da shi : wanda ake amfani da shi. Za a fara aiki da doka da zaran an bayyana ta a mujallar hukuma.

Encadrement : jagoranci : horo, shiryar da. Lakuru sun samu jagoranci mai kyau lokacin da suna samun horo.

Enclavement : Halin ƙauya-tacce

Endemie : Alloba : kamuwar mutane da yawa da cuta iri ɗaya a lokaci guda, ko kuma wata cuta mai addabar jama'ar da ke zaune wuri guda lokaci zuwa lokaci.

Endettement : cin bashi : ɗaukar bashi, rancen kuɗi. Cin bashin ga ƙasa.

. **Endettement excessif** : hanɓararren cin bashi.

Endetter (s') : **Ɗaukar bashi** : ɗaukar rance, amsar bashi. ɗaukar bashi ba digi.

Endoctriner : **cusa ra'ayi** : ciwo kan mutum ta hanyar cusa mishi ra'ayuyyukan kansa. Madugan yan siyasa suna cusa wa magoya bayansu ra'ayin kansu.

Endogène : **Na zufar kansa** : abu wanda yake na ƙoƙarin kan mutum, wanda mutum ke yi wa kansa samun ci-gaba da zufar kansa.

Endurance : **Dauriya** : jimiri, dauriya ga gajiya ko wata wahala. Dauriyar kishirwa ga jama'a.

Energie : **ƙarfi** : Kuzari ; amfani da ƙarfi da zuciya guda wajen aikata wani abu. Cika wani aiki da ƙarfi.

Engagement : **alƙawali** : yarjejeniya ɗaukar alƙawali, ɗauka wa rai. Cika alƙawali.

Engagements internationaux : **yarjejeniya tsakanin ƙasashe** : alƙawalin da aka ɗauka tare da sauran ƙasashen duniya. Ya kyautu dukan ƙasashe su daratta yajejeniyar da suka rattaba hannu kanta tare da sauran ƙasashen duniya.

Enquête : **bincike** : datattar hanya mai bai wa mai gabatar da ƙara damar tabbatar da gaskiyar abin da ya faɗa. Gudanar da bincike.

Enregistrement : **rubutu cikin kundi** : tabbacin wani abu ta hanyar rubuta shi cikin kirgam tare da biyan waɗansu yan kuɗi a game da wannan. Biyan kuɗin rubutu cikin kundi.

Enrichissement illicite : **Tara dukiya ta haram** : arzikin haram ; cin kuɗin ƙasa don tara dukiya wadda ba ta halak ba. Ya kyautu a hukuntar da duk mutumen da aka kama da laifin tara dukiya ta haram.

Enseignement : **koyarwa** : aikin bayar da ilimi da horo. Sake tsarin koyarwa.

. **Enseignement élémentaire** : Koyarwa cikin ƙananan makarantu : aikin bayar da ilimi da horo a ƙananan makarantu.

. **Enseignement général** : **jimiltaccen ilimi** : samun ilimi da horo kan fanni daban-daban.

. **Enseignement professionnel** : **makarantun koyon aikin hannu** : makarantu inda ake koyon aikin hannu.

. **Enseignement technique** : **makarantun koyon fusa'a** : makaranta inda ake bayar da ilimi na fusa'a.

Entente : **Jittuwa** : **yarjejeniya** : Shiri, haɗin gwiwa, amincewa, ma'amula ƙasashen biyu masu gaba da juna sun cin ma Jittuwa.

Entériner : tabbatar da : gaskantar da wani abu ta hanyar doka. Tabbatar da wata haraka.

Entre autres : Baicin : banda. Baicin y'an sandika, akwai kuma wakilin gwamnati wajen mafawarar.

Entrée en fonction officielle : kama aiki : girkar da mutum cikin wani aiki a hakumce. Shugaban jamhuriya za ya kama aiki a hukumce bayan an yi bikin nad'inshi.

Entrée en vigueur : Soma aiki : lokacin da za a fara amfani da wani abu. Za a bayyana lokacin soma aiki da dokar da aka fitar da ita a hukunce.

Entrepreneur : d'an kwangila : mutanen da ke gabatar wani kampani, d'an kasuwa. Gwamnati na kira ga y'an kwangila da su kawo agaji ga mutanen da bala'i ya shafa.

Entreprise : Kampani : wurin harakokin kasuwanci, wurin sarrafa wad'ansu abubuwa na saidawa kafa kampani.

Entretien : Hira : samun canza miyau da wani, tattaunawa. Samun yin hira da wani.

Environnement : Muhalli : wurin da d'an Adam ke gudanar da rayuwarshi, duniya. Kariyar muhalli.

. **Environnement politique : yanayin siyawa**. Halin yanda siyasa ta kasance.

Envisager : yin Hasashe : yin hange, yin nazari kan wani abu ; sanya gurin yin wani abu, kiyasta a rai. Paraminista na hasashen tafiya rangadi cikin sauran garuruwan kasa.

Envoyé : Wakili : manzo, aikake. Shugaban jamhuriya ya sadu da wakilin bankin duniya da ke girke a kasar Nijar.

. **Envoyé extraordinaire : manzo na musamman** : d'an aike na musumman, wakili na masamman.

. **Envoyé spécial : wakili** : D'an jarida da ke zaune a wani gari don neman labaru.

Epanouissement : jin dad'in rayuwa : samun jin dad'i, yad'uwar wani abu. Al'umma ta fi jin dad'in rayuwa cikin tsarin mulkin demokarad'iya.

Epargne : tsimi, ajiya, tanadi: adanawa, boyewa. Mutane sun yin tsimi.

Epargner : yin tsimi : 1/ **yin adano, tanadawa, ajewa**. Mutanen jaha sun ajiye magud'an kud'i.

2/ **Kiyayewa**. Sanya hannu kan yarjejeniyar zaman lafiya za ta kiyaye wa jama'a farmakin da y'an tawaye ke kai masu.

Epidémie : Yad'uwar cuta : kamuwar mutanen da yawa da wata cuta wadda wani ke iya d'afa wa wani. annoba. Yad'uwar (annoba) d'an sankarau ta

haddasa mutuwar mutane da dama.

Epuiser : Gajiyar da : 1/ kashe jiki. Balaguron da ya yi ya gajiyar da shi.

2/ **Karewa**. Cimakar da aka kawo don agaza wa masu fama da yunwa ta kare ƙap.

Equilibre : Ɗaidaito : wanda ke girke da kyau. Daidaitaccen tattalin arziki.

Equipe : Rukuni : gungu daban-daban na mutane masu aiki tare don cin ma guri ɗaya.

. **Equipe gouvernementale : gwamnati** : dukan ministocin do gwamnati ya ƙumsa.

Equipement : Kayayyakin aiki : dukan abubuwan da ake amfani da su don yin wani aiki. Kayayyakin aikin wani kampani;

Eradiquer : ƙawar da : yaƙar wani abu. Kawar da jahilci.

Erosion : zaizayar ƙasa : dukan abubuwan da ke kawo taɓarɓarewar yanayi. An shibka dubban itatuwa don yaƙi da zaizayar ƙasa.

Esclavage : Bauta : halin danniya . An soke bauta.

Escorte : Rakiyar kare lafiya: mutanen da ke biye da wani mai muƙami don kiyaye lafiyarshi. Samun rakiyar sojawa.

Espérance : sanya rai : tsammani, zaton cin ma gurin da aka sanya gaba. Ɗaliban da suka yi jarrabawa suna sa ran cin nasara.

. **Espérance de vie : San ran tsawon rayuwa** : kimanta bakin tsawon rayuwar al'umma dangance da mizanin masu mutuwa ; tsammanin tsawon rayuwa.

Espoir : Sanya rai : 1/ kyakkyawar fata, sanya rai ga wani abu.

2/ mutum ko wani abu wanda ake kwanto kanshi, wanda ake aza babban guri kanshi. Dukan ƙasashen duniya na aza gurorinsu kan matasa

Esprit : Hali, ra'ayi, niyya : Niyyar bayar da kai.

. **Esprit de clan : ra'ayin ƙabilanci** : bazar da ra'ayuy-yuka don hihita ƙabilarsa nuna bambanci dangance da ƙabilarsa.

. **Esprit de dialogue : Halin mai son a tattauna** : mai fatan a yi zaman sa santawa.

. **Esprit de sacrifice** : Niyyar sa kai : halin mai bayar da kanshi don aikata wani aiki da zucciya guda.

. **Esprit de tolérance : Halin haƙuri** : halin wanda ya san ta zaman duniya, wanda ya iya zama da jama'a.

. **Esprit féodal : Ra'ayin mai son ƙwaruwar mutane** : mai son kanshi, mai son rangwane, mai cutar mutane.

Essentiel : Muhimmi : wanda ya kamata, wanda ya kyautu. Tsayawa kan mahimman abubuwa

Essor : Habaka : ci-gaba, bunkasa, samun wadata. Habakar tattalin arziki.

Ester : Shigar da kara : tuhuma. Shigar da kara gidan juju.

Estimation : kimantawa, kiyasi : kayyade bakin wani abu, kwatanta wani abu. Ma'aikatan ofushin magajin gari sun kimanta barnar da ruwan sama suka yi.

Etablir un véritable dialogue : zamnawa kan tebirin shawara : yin zaman tattaunawa, canza ra'ayi. Ya kiyautu a zamna kan tebirin shawara don cin ma yarjejeniya tsakanin bangarorin masu gaba da juna.

Etablissement d'enseignement : Makarantar boko : wuraren bayar da ilimi da horo. Gwamnati ya d'auki niyyar kafa sabbin makarantun boko cikin sauran biranen kasa.

Etablissement privé : Ma'aikata mai zaman kanta : ma'aikatar da ba ta gwamnati ba, wadda ba ta rataya wuyan gwamnati ba. Ma'aikatu masu zaman kansu na samun tallafi daga gwamnati.

Etablissement public : Ma'aikatun gwamnati : ma'aikatun kasa, wad'anda suke rataye a wuyan gwamnati. Shekarun baya-bayan ga, ma'aikatun gwamnati na fuskantar matsaloli da yawa?

Etape : lokaci : lokacin samun ci-gaban wani abu. An cin ma lokacin samun zama lafiya.

Etat : 1/ K'asa : Yanki mai kunshe da jama'a, mai hukumonin kanta, mai kuma tsarin mulkin kanta. K'asar Nijar.

2/ Jaha. Tarewar kasashe.

Etat civil : Shaidar matsayin mutum : ma'aikata mai fitar da takardun shaidar dukan bayyanai kan mutum.

Etat d'urgence : dokar ta baci : tsatsauran matakan da ake d'auka a game da wani hali mai tayar da hankalin y'an kasa, sintiri daga soja don kwantar da kankalin ja'a.

. Etat de droit : kasa mai aiki da doka.

. Etat de siège : tsarin hukumancin masamman : kafa dokoki na masamman masu tankwasar da y'ancin jama'a.

. Etat-major : 1/ Habsan sojoji : gungun manya-mayan sojoji masu bai wa wani babban soji hannu cikin tafiyar da ayyukanshi na hukullanci.

2/ dukan mutanen da ke gindin wani shugaba, mai mukami.

. Etat fédéré : kasa, jaha : kasar da ke cikin wata kasa ta tarayya.

. Etats unitaires : had'ad'd'iyar

ƙasa : ƙasar da babu halin rarraba ta

. **Etat signataire : ƙasashen da suka rattaba hannu** : ɗukan ƙasashen da suka sanya hannu kan wani abu don amincewa da shi.

Etatiser : Mayar da wani abu na ƙasa : mayar da wani abu , mallakar ƙasa. Mayar da kampani na ƙasa.

Etendre : Barbazawa : yadarwa, faɗaɗawa : ƙara girman wani abu. faɗaɗa hukumancinsa.

Ethique : Aƙida, ɗa'a : dukan kyakkyawan tabi'u na zama tare da mutane. Samun aƙida.

Ethnie : ƙabila : mutane masu matsiri guda, masu harshe guda da al'adu iri ɗaya. Ƙasar Nijar na ƙumshe da ƙabilu da yawa.

Ethnocentrisme : Ƙabilanci : hihita ƙabilarsa, nuna bambanci dangance da ƙabila. Haramta ƙabilanci.

Etranger : 1/ Baƙo : wanda ya fito daga wata ƙasa, ko kuma daga wata jaha. Baƙi ɗan yawon buɗa ido.

2/ dukan harakokin da suka shafi dangantaka da ƙasashen waje. Harakoki da ƙasashen waje

Etre en lice : Zama cikin Neman wani matsayi : shiga takarar neman wani matsayi. Ɗan takara biyu ke cikin neman zaɓe a zagaye na biyu.

Etre sous administration de : zama ƙarƙashin hukunci: zama rataye ga wani hukunci. Ofishin ɗan sanda ƙarƙashin hukuncin ministan cikin gida yake.

Etude de faisabilité : Nazari kan aikatuwar wani abu : gudanar da binciken don gano ta yanda wani abu ke yiyuwa . An yi nazari kan halin aikatuwar gandarin garin kandaji.

Etudes supérieures : Karatun ilimi mai zurfi : dukan harakokin karatun da suka shafi karatun jami'a da na tsangaya. Digiri na karatun ilimi mai zurhi.

Evaluation : Kimanci : ƙwanƙwance yanda wani abu ya ƙasance, yin lissafi a kai. Kimancin yanayin damana.

Evaluer : Kimantawa, : ƙayyade wani abu, lissafa shi. An kimanta ɓarnar da ambaliyar ruwa ta haddasa.

Evènement : Al'amari : abin da ke faruwa ko ya faru. Al'amarin siyasa.

. **Evènement historique : Al'amari na tarihi** : Abun da ya faru da ɗaɗewa kuma ana bikin tuna shi kowace shekara.

Evincer : Tsigewa : raba mutum da muƙaminshi ta hanyar amfani da ƙarfin damste, sabkewa, hiddawa. Tsige mutum daga kujerar mulki.

Evolution : Ci-gaba, Sauyi, ƙaruwa, wadata. Harakokin

kasuwanci suna ci gaba cikin kasuwar bayan fage.

Exaction : 1/ muzguna : duka, arkane, taushe hakkin jama'a; kungiyar kare hakkin d'an Adam ta yi Allawadai da muzgunawar da aka yi wa masu zanga-zanga.

2/**danfara, sata**. Y'an sanda sun shiga kamun ma'aikatan da ake zargin aikata danfara.

Exaltation : Yabo : tad'awa, yin kirari ga wani abu ; yabon wani mulki.

Excéder : Zarcewa : 1/ Wuce abin da aka sanya tsammani. A shekarar bana kud'in da gwamnati ya kashe sun zarce wad'anda suka shiga aljihunshi.

2/ **Wuce gona da iri**. Wuce gona da iri kan fannin hukumanci.

Excellente initiative : kyak-kyawar shawara : Shawara ta gari, mai kawo alheri. Matakin da y'an majalasar dokoki suka d'auka, kyakkyawar shawara ce.

Exception : Halin masamman : Halin abun da ba na yau-da-kullum ba. An d'auki wannan hanyar cikin hali na masamman.

Exceptionnel : Na masamman : 1/ Wanda ba a saba gani ba, wanda ba ya cikin tsarin da aka tsayar. An kirawo taron gaggawa na musamman.

Exlusion : Wariya ; Tsigewa : Kora, hidda mutum daga daga cikin wani tsari. Tsigewar da aka yi mishi daga cikin jam'iyar ta kawo rishin jituwa tsakanin jama'a.

Exclusivement : Masamman, Kawai : bai wa abu guda gaba, aikata shi shi kad'ai. Masamman harakokin siyasa ya bai wa gaba.

Exécutif : Na zartawa : hukuma mai nauyin zartar da dokoki da ka'idodi. An kafa kwamitin zartarwa na jam'iyyar.

Exécution : Yin wáni aiki, Aikatawa : 1/ Tafiyar da wani aiki, zartar da aiki ; wani kampanin kasa shi ne ya d'auki nauyin yin aikin gadar.

2/ Kashe mutumen da aka yankewa hukunci kashi. Al'ummar duniya na rokon a fasa kashe mutanen da aka d'aure kan ra'ayin siyasa.

. Exécution des lois : Aikin zartar da dokoki : aikatar da dokoki.

. Exécution du budget de l'Etat : Aikin zartar da kasahin kud'in kasa : Yin aiki da kasahin kud'in kasa da aka tsayar.

Exécution sommaire : Kisa : Kashe mutum ba tare da an yi mishi wata shari'a ba. Kashe mai laifi.

Exécutoire : Abun da za a rartar da : abin da za a aiki da shi, mai bayar da umurnin a aikata. Dokar da za a zartar.

Excellence : 1/ ƙwarewa : Dukan malamman makarantar sun yaba irin ƙwarewar da ɗalibi mai karatun ilimin shari'a ya nuna.

2/ **Mai girma** : Kalmar girmamawa. Mai girma paraminista ya yi jawabi kan tsare-tsaren da za ya gabatar a gaban ɣan majalisar dokoki.

Exemplaire : **Na ƙwarai** : abin koyi, kyaukyawa, na gari. Nuna tabi'a ta ƙwarai.

Exercice : **Aikin Tafiyar da** : Aikin gudanar da wani aiki, ko muƙami. Tafiyar da aiki.

. **Exercice de fonction** : **Aikin tafiyar da wani muƙami** : riƙe wani muƙami.

. **Exercice du pouvoir** : Aikin tafiyar da mulki : Jan ragamar mulki.

Exhorter : **kira, Gargaɗa** : jawo hankalin mutum ga yin wani abu ta hanyar yi mishi jawabi. Shugaban jamhuriya yana kira ga ɣan ƙasa da su mayar da hankali ga aiki.

Exiger : Nemi hakki : tilastawa, neman ɣanci, ɣan ƙungiyar ƙwadago suna neman a riƙa biyan su albashinsu kan lokaci.

Exil : Hijira : haramta wa mutum ƶama cikin ƙasa, korar shi daga cikin ƙasa. Sanya mutum gudun hijira.

Existence :1/ **Tsawon lokaci** : daɗewar wani abu gwamnati da aka girka ya samu tsawon wata guda.

2/ **Halin rayuwa**. Samun kyaukyawar rayuwa.

Exode : **yin tashi** : gushewar jama'a daga yankinsu. Sai an ɗauki matakai na gari don magance al'amarin tashin jama'a.

. **Exode rural** : **cin rani, diga** : baro karkara don zuwa birni neman aiki.

Exonération : Ragi : Yi wa mutum ragowa kan wani abu. An yi wa ɗan ƙwangila ragin kuɗin lanho.

Expansion : Ci-gaba, Haɓaka : Yaɗuwa, ƙaruwa. Harakokin kasuwanci na samun ci-gaba kwanakin baya-bayan nan.

Expatrié : **Baƙo** : Wanda ke zaune cikin ƙasar da ba tashi ba. A daratta baƙi.

Expédier : Aikawa : kaiwa, isar da. Aika wasiƙa.

Expérience professionnelle : **Horo, cikin wani aiki** : sanin da ake samu cikin wani aiki, goguwa wajen yin wani aiki. Ṣamun cikakken horo kan fannin wani aiki.

Expert : **ƙwararre** : wanda ya laƙanci wani abu da kyau. Ƙwararre kan fannin fusa'a.

Expiration : **ƙarshen wa'adi** : abin da ya kawo ƙarshen shi. ƙarshen wa'adin da aka ƙayyade.

Expirer : ƙarewa : kai ƙarshe, wakilcinshi bana yake ƙarewa.

Explication : Bayyani : kawo haske, kwatanci. kawo bayyanai kan wani abu.

Explicite : Mai haske : filla-filla, wanda ake ganewa da sauƙi, maras ɗaurin kai. Jawabi mai haske.

Exploit : Abun ƙwarai : yin abu na ƙwarai, cin nasara. maguji ya yi abun ƙwarai da ya lashe gudun tserere.

Exploitation : cin moriya : samun amfanin wani abu, wurin da ake samun abin amfani. Al'umma ta yi amfani da dukan abubuwan da suka dace don cin moriyar amfanin gana.

Exploration : Bincike : Ziyarta : Zuwa ganin wani abu da idonsa, larwai. Binciken wani wuri.

Explosion : 1.) **Fashe-fashe**

2.) **Murna** : nuna jin daɗi. Jama'a sun yi ta murna bayanda aka yanke shari'ar.

Exportation : fidda kaya ƙasashen wajen : fatauci : fitar da kayayyakin saidawa don kai su wata ƙasa. Fataucin bisashe ƙasashen waje ya fara ja da baya-vaya kwanakin baya-bayan ga a ƙasar Nijar.

Exposer : 1/ **Bazawa** : kalka-sawa. Barbaza kayayyaki.

2/ **Bayar da bayyanai** : bayar da haske kan wani abu.

Expression plurielle : Ra'ayi guda na jama'a : ra'ayi guda da jama'a ke gabatarwa. An samu girkuwar tsarin demokaraɗiya a albarkacin ra'ayi guda da jam'iyun siyasa suka yi ta gabatarwa.

Exprimer : Nunawa : gabatar da ra'ayinsa, bayyana ra'ayinsa. Ya yi wani dogon jawabi don nuna godiyarshi ga mutanen da suka kawo taimakonsu.

Expropriation : raba mutum da abunshi : halin da mutum ke bara wa gwamnati wata mallakarshi don amfanin jama'a bayan an ba shi diyya, ƙwace. Raba mutum da hilinshi.

Exproprier : Anshewa, ƙwacewa, Rabawa : raba mutum da wa mallakarshi dangance da ƙa'idodin doka, ƙwacewa. An raba shi da duk ƙadarorinshi don amfanin jama'a.

Expulsion : kora : tsigewa, hidda mutum daga wani wuri tare da amfani da ƙarhin damtse. Y'an sanda sun kore ɗalibai daga cikin tsangayarsu.

. **Expulsion des étrangers : korar baƙi** : tilasawa waɗanda ba y'an ƙasa ba da su fita daga ƙasar idan zaman su yakan iya kansancewa aibu ga jama'a.

Extension : ƙari : yaɗuwa, ƙara girman wani abu. K'ara shinfiɗa hukumancinsa.

Extermination : Kishin kya-she : koshi na rishin imani; halakawa ; yi wa jama'a kishin kyashe dangance da launin fatarsu.

Extrader : Mayar da ; Mikawa: sanyà mutunen da ake tuhuma hannun hukumomi. Mika d'an ta'adda cikin hannun hukumar kasarsu.

Extradiction : Mikawa, damkawa,maidawa : hanyoyin da wata kasa ke d'auka don sad'un domar a sanya cikin hannunta mutunen da ake tuhuma. Mika wanda aka yanke wa hukuncin kishi.

Extrait : Gutsure : guntu, tsame.1/ wani sashe da ake gutsorowa daga cikin wani littafi, ko wani jawabi, ko wani filim. D'an jarida ya nuno gutsiran jawabin shugaban kasa a gidan radiyo-mai-hoto.

2/ Batagwainiyar wata takarda.

. Extrait de naissance : takardar haifuwa.

Extraordinaire : Na musamman : wanda ba a saba gani ba. Kwamitin zatarwa na jam'iyar ya kirawo taro na musamman.

Extrémité : lungu : karshen wani abu. Masu goyon bayan jam'iyyar, sun fito daga lunguna daban-daban na cikin kasa.

Exubérance : kuwa da tsalle-tsalle : Nuna jin dad'insa matuka y'an kallo sun nuna jin dad'insu ta hanyar yin kuwa da tsalle-tsalle.

F

Facteur : shisshike : abin da ke taimakawa wajen cim ma wani guri. Abin da yake shisshike ne wajen samun ci-gaba

. **Facteur clé : Ginshiki** : babban shisshike, abu wanda komi ke rataye kanshi.

. **Facteur de développement : shisshiken ci-gaba** : abu mai taimaikawa wajen samun ci-gaba.

Faire autorité : Tilasawa ; tsare gida : kama jiki ta fuskar girkar da hukunci, zama abin koyi. Tsare gida gaban y'an gidansa.

Falsification : Kirar karya, sake kama ta karua: jirkitar da wani abu, ba shi wad'ansu alamu na karya. Y'an sanda sun kama mutanen da ake zargi da laifin kera kud'in karya.

Falsifier : sauyar da kama : bayar da wata kama ta sata. Sauyar da kamar wad'ansu takardu.

Famille : Iyali : 1/ dukan mutanen da ke da y'an-uwanci, dangi . Y'an iyali guda suna shawara.

2/ **Gungun y'an Adam**, ko na wad'ansu abubuwa masu kama guda, masu ra'ayi gida. Dukan masu ra'ayin siyasa guda sun halarci taron gangamin.

. **Famille humaine : y'an Adam** : dukan mutanen da ke zaune a bayan doron kasa.

Fanatique : Mai tsattsauran ra'ayi : mai kukewa kan wani abu : mai son wani abu hiye da mizani, mai mutuwa kanshi. Mai tsattsauran ra'ayin siyasa.

Fatalité : kadara : abin da ke faruwa kwatsom, wani abu mai haddasa masifa. Ba a iya kaucewa kadara.

Fausse déclaration : Sanarwar banza : Sanarwar karya, wadda ba ta da hujja. Gabatar da sanarwar banza.

Fausse nouvelle : labarin banza : labari maras hujja, na karya. Kawo labarin banza.

Faveur : Goyon baya : Son rai : nuna fifiko. Aikata son rai ; nuna goyon baya.

Favorable : Amintacce : 1/ Wanda yake d'auke da amintattun matakai. Dukan y'an siyasa sun amince da a yi wa kundin zabe gyaren fuska.

2/ Datacce : Wanda ya dace da wani abu, mai kawo alheri ga abin. Kwamitin na cikin nazarin datattun matakai don samun zaman lafiya.

Favoritisme : Halin son rai : fifiko, gatanci nuna bambanci, rishin bin gaskiya. Tashi tsaye kan masu nuna halin son rai.

Fédéralisme : Mulkin Tarraya: tsarin mulki wanda a cikinshi gwamnati ke saka wa hukumo-

min jahohi cikakken iko. Wadansu jam'iyun sayasa sun yi tsaye kan sai an kafa mulkin tarraya.

Fédération : kungiya : Tarayya, hukuma ; hadin gwiwar jam'iyun siyasa, ko yan kwadago, ko wadansu masu wadansu harakoki. Kungiyar ta yan gudun kafa kasar Nijar.

Félicitation : Barka : Taya mutum murna dangance da wani farin ciki da yake cikinshi. Shugaban jamhuriya ya samu sakon barka a dalilin zagayowar sallar samun yancin kan kasa.

Fer de lance : kusar ci-gaba: mutumen da ke karfafa wani tsari, masu sanya wani abu ya ci-gaba. Zama kusar ci-gaba cikin wata kungiya.

Fermeté : Tsauri : nuna tsauri wajen tafiyar da wani abu, tsanani ; aikata wani abu da zucciya guda. Nuna tsauri.

Festival : Biki : fastibal : shirya sabgagin wasanni iri-iri a wani kayyadadden wuri. Biki (Festibal) na duniya kan al'adun Afirka.

Festival de la jeunesse : Biki (fastibal) na samari da yan mata : haduwar samari da yan mata wuri guda don gudanar da wasanni da sada zumunci.

Février : faburari : wata na biyu cikin shekarar nasara mai mutuwa bayan kwanaki ishirin da takwas ko ishirin da tara. An gudanar da zaben kananan hukumomi a ranar bakwai (7) ga faburari na alif dari tara da tasa'in da tara (1999).

Fidélité : Amana, imani : bin wasu abu kan gaskiya, adalci. Rike amana kan alkawalin da aka dauka.

Finalisation : halin cika wani abu : kare wani abu, hauda shi kan hanyar da ake bukata. Cika wani guri.

Finalité : guri : cim ma fata, cika niyyarsa. Matakan cin ma guri.

Financement : biya : tallafa wa wani kampani, ko wata ma'aikatar gwamnati ta hanyar kudi. Yan kasar Nijar sun dauki nauyin biyan kudin shirya zaben neman amincewa ko na rishin amincewa.

Finances : kudi : dukan abin da ya shafi kudin da ke shiga da masu fita daga cikin asusun kasa, tafiyar da harakokin kudi a cikin hukumomi. Ministan kudi.

Finances publiques : kudin kasa : dukan kudin da kasa ta mallaka.

Flagrant : na kiri-kiri : abin da ke wuce mizani, wanda ba ya da tambaba, wanda ba ya boyiwa. Aikata wani abu kiri-kiri.

Flagrand délit : Laifin kiri-kiri : laifi a gaban idon mutane.

Fléau : Bala'i ; Alloba : wata babbar matsala mai shafar

jama'a, wani abin tashin hankali. Yunwa bala'i ce ga jama'a.

Fluctuation : hawa da sauka: canje-canje. Hawa da saukar wad'ansu kud'i.

Foi : **Imani** : 1) ban gaskiya kan wata ibada, kan wani addini. Fad'ad'a imani.

2) Amincewa da mutum , ko da wani abu. Amincewa da makomarsa.

Fonction : aiki : Harakokin aiki, tafiyar da wani aiki. Aikin koyarwa.

Fonction publique : ma'aikatan gwamnati : dukan ma'aikatan gwamnati, masu aiki cikin ma'aikatun gwamnati.

Fondamental : Mahimmi : Ginshiki : wanda ake dogara kanshi, mai cikakkar ma'ana wajen tafiyar da wani abu. Mahimman dokoki.

Fondement juridique : hujja kan doka : wanda ke kan hanyar shari'a, wanda bai kauce wa doka ba. Kawo hujja kan tsarin shari'a.

Fonds : Lamani : jari, kud'in da ake bai wa wani. Masu bayar da lamani na duniya sun kawo wa kasar Nijar tallafin magud'an kud'i.

Fonds de solidarité : asusun tamaikon juna : tarbacen kud'in da ake yi don agaza wa masu karamin hali.

Fonds monétaire international : Asusun bada lamani na duniya : kungiya mai bai wa kasashen duniya bashi.

Fonds limité : karamin jari : ragaggin kud'i wand'anda ba su da yawa sosai kampanin yana cikin tashe, amma sai dai karamin jari gare shi.

Force : karfi : sanya kuzari wajen aikata wani abu aikata wani abu da karfi.

Forces sociales : kungiyoyi : dukan kungiyoyin jama'a masu tofa albarkacin bakinsu cikin jan ragamar harakokin kasa, kungiyoyi masu kare yancin yan kasa. Kungiyoyi suna korahin cewa matakan da gwamnati ya d'auka suna kuntata wa jama'a.

Forces armées : Sojoji : runduna -daban-daban ta dakarun kasa masu nauyin tsaron lafiyar kasa. Sojoji sun fara juyin mulki na farko a ranar sha biyar ga apirilu na alif d'ari tara da saba'in da hud'u (1974).

Fortune : dukiya : mallakar mutum, ko mallakar kasa. Dukiyar mutum.

Forum : Babban taro : had'uwa, mafawara, zaman canza miyau, shirya zaman taro na samun had'in kan kasa.

Forum national : Babban taro na kasa : Babban taro mai had'a wakillan yan kasa don tattaunawa kan matsalolin kasa.

Fraude : fasa-ƙwabri : sarande, satar hanya. Tashi tsaye kan fasa-ƙwabri.

Fraude électorale : magudi kan zaɓe : yin sata cikin gudanar da zaɓe, manaƙisa.

Fréquence : yawaita : yawan faruwa, yawaitar wani abu. Yawaitar juyin mulki cikin ƙasashen Afirka.

Fréquenter : Yawan ganawa : yawan gani, saduwa. Saduwa da aboki.

Frontière : iyaka : mararraba tsakanin ƙasashe biyu, ko waɗansu jahohi. An kafa ofishin yan sanda da ofishin duwan bakin iyaka.

Frontière linguistique : iyakar yankunan harshe : iyaka wadda ke raba yankin wani harshe da na wani a cikin ƙasa ko jaha.

Fructification : halin jujjuya-wa : samun damar yawantar da wani abu, cin riba. Jujjuya jari.

Frustration : ɓacin rai ; takai-ci: burkutar ran mutum, rishin jin daɗi cikin ran mutum. Samun ɓacin rai, jin takaici.

Fugitif : Maguji : wanda ya gudu : wanda ya tsere, wanda ya arce. Y'an sanda sun shiga neman mutanen da suka gudu.

Fulgurant : mai sauri : abu mai aukuwa da gaugawa. Da sauri ya samu zama cikin manya-manyan sojoji.

Fumiste : Sakakke ; mai sakaci : mutunen da ba ya yin komi a hankali kwance, maras lura. Inda ya rage sakaci, da ya ci babbar nasara.

Funèbre : zana'iza : halin ɓacin rai dangance da mutuwar wani, zaman makoki. Zaman zana'iza.

Fureur : tsanani : hasala : muguwar zuciyar, halin wani tsananin faɗa . Ana gobza faɗa mai tsanani a hilin daga.

Fusion : haɗin gwawa : gamuwa. Haɗin gwiwar jam'iyun siyasa biyu.

Futur : zuwa gaba : lokaci mai zuwa. Zaɓuɓɓukan da za a yi zuwa gaba suna da babban mahimmanci ga ƙasa.

G

Gachis : ɓarna : amfani da wani abu ba kan gado, pacaka, shagalin tsatsa. Gudun yin ɓarna.

Gager : jinginawa : jingina wani abu, ɗaukar alƙawali. Jinginar da wani abu.

Gajeure : fariya : shirme tarkar abin da mutum ba ya iyawa. Gurin da ya sanya gaba ya kasance tamkar fariya.

Gagner : samu : abin da ƙarfin mutum ya ba shi, ci . Samun amincewar wani.

Gain : samu : sauƙi, riba. Neman samu babu wahala.

Garant : Mai haida : mai wakilta, mai bayar da tabbaci. Shugaban jamhuriya shi ne shaidar haɗin kan ɣan ƙasa.

Garantie : tabbaci : alkawalin tafiyar da wani abu. Ya bayar muna da cikakken tabbaci.

Garantie fondamentale : ɣancin ɣan ƙasa : dukan hakki da ɣancin da tsari mulki ya tanada wa ɣan ƙasa.

Garantir : tabbatar da : ɗaukar nauyi, kulawa. Shugaban jamhuriya ke tabbatar da daratta dokoki da ƙa'idodin ƙasa.

Garde : Mai gadi ; mai tsaro: mai kula da tsaron wani abu, da kiyaye lafiyar wani abu. Yin gadin dare.

Garde à vue : tsarewa a ofishin ɣan sanda : tsare mutum na ƙayyadadden lokaci da ake yi wa mutum a ofishin ɣan sanda kahin a gabatar da shi a gaban koti.

Garde des sceaux : mai adanan tambarin ƙasa : ministan da ake aza wa nauyin adanon tambarin ƙasa.

Garder le sécret des délibérations : Ruhe asirin shawarwari : rike abin siri cikin zucciyarsa.

Gardien : Mai gadi : mai tsaron wani abu, mai kare shi. Tsarin mulki shi ke kare ɣancin ɣan ƙasa.

Garnison : rundunar sojoji : Kampanyin sojawa.

Gaspillage : ɓarna : kashin kuɗi ba lissafi. Ɓarnar kuɗi.

Gel : halin sokewa : halin dakatar da wata haraka, tsayar da ita daskare ta. Soke bashi.

Geler : sokewa, daskarewa : tsayar da wata haraka, dakatar da zirga-zirgar kuɗi. Gwamnati na da niyyar daskarar da albashin ma'aikata.

Général : Na kowa : na ƙaruwar kowa da kowa, wanda ya shafi yawancin jama'a. Aikata abin da za ya amfanin kowa.

Généralisation : halin abun da ke shafar yawancin mutane : Cabewar da tashin hankalin ya yi, shi ya kawo jama'a barin garin.

Généralité : Galibi : yawanci: wanda ya shafi yawanci. Bayar da ra'ayinsa kan yawancin abubuwa.

Génération : tsara ; sa'a : dukan yan shekaru guda, waɗanda aka haifa kusan lokaci guda. Rikicin tsareku daban-daban.

Générosité : sakin hannu : wanda ba ya da taurin hannu, kyauta. Sakin hannu ƙwarai.

Génie : waibuwa : samun fusa'ar ƙirƙira abubuwa masu ƙayatarwa. Yin waibuwa kan waɗansu harakoki.

Génie propre : wanda mutum ya ƙirƙira da kanshi : abin da mutum ya ƙirƙiro cikin kanshi ba tare da ya kwaikwayi wani ba.

Gérance : haya : ɗaukar hannun jari a masana'anta, ko kuma tafiyar da harakokin masana'anta da sunan haya. Sanya wata masana'anta haya.

Gestion : Tsarin tafiyar da : tsarin gudanar da waɗansu harakoki. Tsarin Tafiyar da lissafin kuɗi.

Gestion des terroirs : tsare-tsaren cikin ƙasa : kula da awaitar da waɗansu tsare-tsare cikin ƙasa.

Gestion occulte : Tsarin tafiyar da harakoki cikin duhu : rishin haske cikin tafiyar da harakoki..

Gestion des affaires publiques : tsarin tafiyar da harakokin ƙasa : jan ragamar harakokin ƙasa.

Gestion du gouvernement : tsarin rafiyar da harakoki daga gwamnati : jan ragamar harakokin ƙasa daga gwamnati.

Gestionnaire : Mai tafiyar da : mutunen da ke da nauyin jan ragamar waɗansu harakoki, ko wata ma'aikata. Mai tafiyar da harakokin banki.

Globalisation : halin haɗewa : halin mayar da harakokin duniya bai ɗaya. Haɗewar harakokin kasuwancin duniya.

Globaliser : haɗewa : mayar da dukan harakoki bai ɗaya. Haɗa duniya.

Gloire : suna ; girma : kawo ban girma ga mutunen da ya yi suna saboda ƙoƙarin da ya yi wa jama'a. Girmama mutanen da suka rasa rayukansu dangance da neman wani yancin, ko haƙƙinsu.

Goulot d'étranglement cikas: mai hana ruwa gudu : mai hana ci-gaban wani abu. Zama cikas cikin wata haraka.

Gouvernants : mahukunta : masu gabata, masu shugabanci. Tayar wa mahukunta ƙayar baya.

Gouvernement : gwamnati : masu shugabanci, dukan ministoci. Kawo goyon baya ga ayyukan gwamnati.

Gouvernement autocratique : Gwamnatin kama karya : mulkin son rai, mai muzgunawa talakkawa.

Gouvernement corrompu : gwamnatin cin hanci : gwamnati wanda a cikinshi cin hanci ya zama ruwan dare game duniya.

Gouvernement d'union nationale : gwamnatin hadin kan kasa : gwamnati mai kumshe da ministoci da suka fito daga jam'iyu daban-daban.

Gouvernement de large ouverture : gwamnatin hadin kai : gwamnati mai kumshe da ministoci da suka fito daga jam'iyu daban-daban da wakillan kasa.

Gouvernement de transition : gwamnatin wucin gadi : gwamnatin rikon korya, mai girka hukumomin jamhuriya.

Gouvernement monolithique : gwamnati da ke kumshe da ministoci y'an jam'iya guda.

Gouvernement restreint : takaitaccen gwamnati : gwamnati mai kumshe da ministoci bakin gwargwado (kadan).

Gouvernemental : Na gwamnati : wanda ya shafi gwamnati, masu hukunci. Mambobin gwamnati.

Gouvernés : talakkawa : jama'ar da ake shugabanta. Mahukunta da talakkawa.

Gouverneur : Gwamna : mai hakuncin jaha, ko wata banki gwamnan banki.

Grâce : afuwa : yahewa, sakin mutunen da ke d'aure, ko sassauta mishi d'auri. Shugaban jamhuriya ya yi afuwa ga y'an kaso a albarkacin sallar samun mulkin kai.

Grâcier : yin afuwa : yahewa, sassauta d'auri. Shugaban jamhuriya na da y'ancin yin afuwa ga mutunen da aka yanke wa hukuncin kisa.

Grand : babba : mutunen da ke da babban mukami, mai martaba. Manyan mutane suke yin abin tarihi.

Grand chancellier des ordres nationaux : Waziri ; babban shansela : mai adanon tambarirrikan kasa.

Grandeur : Mahimmanci : girma, amfani, mai ma'ana kan wani fannin siyasa ko zamentakewa. Mahimmancin wani abin karuwar jama'a.

Gratification : kyauta ; tukwici : karin da ake yi wa ma'aikaci bisa ga albashinshi. An yi wa dukan ma'aikatan kyauta a karshen shekara.

Gratitude : Godiya : nuna jin daɗi a game da wani abin alheri. Gabatar da sahihiyar godiyarsa ga wani.

Gratuit : maras hujja : wanda ba ya da kan gado, na rishin gaskiya. Zargi maras hujja.

Grave : tsananta : Mai kuskure, abin da ke iya haddasa tashin hankali, mai ban tsoro. Tsanantar wani hali.

Gravir : cim ma : hawa, kaiwa. Ya cin ma dukan matsayi daban-daban na babbar mahakunta.

Gravir les échellons : cin ma matsayi daban-daban : samun cin ma waɗansu muƙamai daban-daban, sannu-sannu.

Gré : niyya ; yarda, ganin dama. Aikata wani abu da niyyar ƙashin kansa.

Gré à gré : hannu da hannu : yin wani abu tsakaninsa da wani kawai.

Greffier : Mataimakin juju : mai bai wa juju hannu cikin tafiyar da aikinshi. Mataimakin malamin shiri'a.

Grève : yajin aiki : halin dakatar da aiki, tsayar da aiki. Gabatar da sanarsuwa ta shiga yajin aiki.

Grève de la faim : yajin cin abinci : ƙin cin abinci da niyyar nuna baƙin cikin da ake fuskanta.

Grille : tsari : shire-shiren da ake iya wallafawa kan wani allo don jama'a su karanta. Tsarin lokutta.

Grille salariale : tsarin jimillar albashi : albashin da ake bayarwa a cikin ma'aikatu.

Groupe : Rukuni : gungun jama'a daban-daban da ke zaune wuri guda, ko masu ra'ayi guda kan wani abu. Rukunin yan majalisa.

Groupe cible : gungun da wani abu ya shafa : gungun da wani abu ke shafa. **Groupe socio-professionnel : gungun ma'aikata** : gungun masu sana'a iri guda.

Groupe parlementaire : rukunin yan majalisa : gungun yan majalasa a cikin majalasar dokoki dangance da yawan mutanen da aka tsayar don cika rukunin.

Groupement : Haɗin gwiwa : haɗuwar mutane da yawa wuri guda don cin ma wani guri da suka sanya gaba, ƙawance. Bangaren yan adawa yana ƙumshe da jam'iyun siyasa masu haɗin gwiwa.

Groupement mutualiste : haɗin gwiwar ƙungiyoyin taimako: haɗin gwiwar ƙungiyoyi masu kawo tamaiko.

Guéguerre : faɗace-faɗacen banza : Tsegumi : riginginmu na banza da ba su ƙarewa. Yin tsegungumma.

Guêpier : haƙo : yin tarko don kama wani, gina ramen mugunta. Haƙon wani.

Guérisseur : mai magani : Mai bayar da maganin waɗansu cututtuka ba tare da ya yi karatun likita ba. Mai maganin gargajiya.

Guerre : yaƙi : faɗa da makamai tsakanin ƙasashe, tashin hankali. Yaƙin Tekun Pasha.

Guet-apens : tarko : yi wa mutum rame don shi faɗa. Jawo maƙiyi shi faɗa cikin tarko.

Guide : Jagora ; shugaba : mutumen da yake jagorar wani abu, mai nuna hanyoyin da za a ɗauka. Mai shugabantar neman sauye-sauye.

Guide suprême : Babban shugaba : babban jagora a fannin siyasa ko kan fannin addini, abin koyi.

Guise : yarda : amincewa, yin abin da mutum ya baƙata. Yin abin da mutum ya yarda da shi.

H

Habilitation : Samun yanci : dacewa, tabbacin ƙarhin mutum na aikata wani abu, iya cika wani aiki. Samun yancin aikata wani abu.

Habileté : yanci : samun damar aikata wani abu. Shugaban jamhuriya na da yancin rushe majalisar dokoki.

Habitat : muhalli : halayen zaman jama'a. Kyautata muhalli

Habitude : sabo : abin da mutum ya saba da shi. Haramta mugun sabo.

Haine : ƙiyayya : nuna rishin sa, ko ƙauna ga wani. Tunzura ƙiyayya tsakanin ƙabilu.

Handicap : cikas : mai hana ruwa gudu, wani abin da ke dabaibaice tafiyar da waɗansu harakoki. Handamar kuɗin ƙasa na kawo cikas cikin tafiyar da harakokin tattalin arzikin ƙasa.

Harmonie : haɗin-kai : zama tare da fahimtar juna tsakanin jama'a, zaman lumana. Samun cikakken haɗin-kai.

Harmonisation : halin daidaitawa : tsarin wani abu, daidaitawa. Daidaitar da halin siyasar ƙasa.

Harmonisation de la politique économique : tsarin siyasar tattalin arziki : yin shinfiɗar kyaukyawar siyasar tattalin arziki, daidaitar da ita.

Harmonisation des plans développement : yin daidaitattun fasullan ayyukan ci-gaba : kawo tsari a game da fasalin ci-gaba.

Hasard : katari : sa'a abin da ke faruwa kwatsam, wanda ba a tsammani. Yin gamen katari da wani.

Haut : mai daraja : mai babban muƙami, mai faɗi a ji. Masu daraja cikin ƙasa.

Haut niveau de vie : kyaukyawan halin rayuwa : halayen rayuwa na ƙwarai masu kawo jin daɗin jama'a.

Haute cour de justice : koti na musamman : kotin da ke da nauyin yanke wa magabata shari'a idan sun aikata laifin cin amanar ƙasa cikin tafiyar da ayyukansu.

Haute trahison : cin amana : mugun aikin da ke sanadiyar zargin shugaban jamhuriya a gaban koti ta musamman.

Hégémonie : Nunin ƙarhi : gwadin girma da ƙarfi na wata ƙasa kan waɗansu ƙasashe. Nuhin ƙarfi daga wata al'umma.

Hérésie : ra'ayin da ke saɓawa ƙayadadun matakai na kancewa wata mazahada, ko mai saɓawa waɗansu al'adu.

Hanya : abin da ya faɗi ya kasance tamkar kancewa hanya.

Héritier : Magaji : wanda ke cin gadon wani. Tabbataccen magaji.

Hiérarchie : tsarin biyayya : tsarin jama'a mai kawo ladabi da biyayya tsakanin mutanen da ke cikin tsarin, ƙa'ida. Tsarin biyayyar sojoji.

Hiérarchie sociale : tsarin biyayyar jama'a : hawa-hawa cikin jama'a dangance da matsayin kowa.

Histoire : tahiri : ilimin sanarsar da jama'a kan abubuwan da suka abku a dauri, ilimi mai nazari kan ci-gaban duniya. Irin wannan abu bai taba faruwa ba a cikin tarihin jamhuriya ta biyu.

Historien : masanin tarihi : wanda ya shahara kan ilimin tarihi. Zama cikakken masanin tarihi.

Historique : na tarihi : wanda ke da alaka da tarihi. An yi bikin cikon shekara na wadansu abubuwa na tarihi da suka faru a karni na biyu.

Hommage : Ban girma ; yabo : kawo ban girma. Yaba wani kan kyakkyawan abin alherin da ya yi.

Homme : ɗan adam ; mutum: dukan ilahirin mutamen da ke zaune doron kasa. Ɗan siyasa.

Homme de médiation : Mai shiga tsakani : mutumen da ke sasanta mutame ko bangarori daban-daban masu gaba da juna.

Homme d'influence : Ɗan (mai) shige-shige : wanda ya yi suna cikin mutane, wanda yake da huldar da mutane da yawa.

Honnêteté : gaskiya : tsare gaskiya, rishin munahuci. gaskiya ta fi komi.

Honneur : Mutunci : darajar kansa martaba. Mutunta mutum.

Horizon : wajeje : guri. Zuwa gaba. yana sanya ran yin aure wajejen shekara ta dubu biyu (2000).

Hospitalité : yin maraba da bako : karbar baki da hannu biyu. Kasa mai maraba da baki.

Huis-clos : na sirri : yin wata shawara cikin sirri. Yin wata haɗuwa ta sirri.

Humanité : yan Adam ; Bil Adama : dukan mutanen da ke zaune a bayan doron kasa. Mulkin wariyar launin fata babban abin kunya ne ga yan Adam.

Humiliation : Cin mutunci : halin kunyatar da mutum, kaskantar da shi. Cin mutuncin wani.

Humilier : wulakantar da : kunyatar da : bai wa mutum kunya, cin zarahin mutum kunyatar da abokin kiyayya.

Hygiène : tsabta : tanadin kansa, ko wani wuri da kyau don kyautata lafiyarsa da ta sauran ta jama'a. Tsabtar jikinsa.

Hymne : take : waƙar da ake yi wa wani zarumi ko wata ƙasa. Kera take.

Hymne national : taken ƙasa : waƙar da ke da matsayin taken ƙasa, wadda ake rare wa ƙasa.

Hypothèse : Hasashe : d'auka kamar, azawa kamar... ; Yin hasashe kan wani abu.

I

Idéal : Manufa : gurin da ake son cin ma, fatan da ake son cin ma. Samun manufa cikin zaman duniya.

Identification : ƙwanƙwancewa : ƙididdigewa, gano wani abu. Samun saurin ƙwanƙwance waɗansu abubuwa.

Identique : Iri ɗaya : alamu guda, kama da juna. Samun alamu iri ɗaya.

Identité : Ainahi, shaida : matsiri, abin da ke bambanta mutum. Tabbatar da ainahinsa.

Idéologie : ra'ayi : dukan ra'ayin da wata ƙungiya ko wani mutum ya sanya gaba, kuma yana kare shi . Y'an siyasa ba su gajiya da baza ra'ayin kansu.

Ignorance : jahilci : rishin iya koyon karatu da rubutu, rishin fahimtar abubuwan duniya. Girka cikakkar siyasa ta kawar da jahilci.

Illégal : Haramtacce : mai saɓa wa doka ; wanda ba ya kan gaskiya, wanda ya kauce wa hanyar doka. Aikata fasa-ƙwabri. Haramtaccen abu ne wanda ya saɓa wa doka.

Illégitime : wanda bai cancanta ba : wanda ba ya kan ƙa'ida, maras hujja. Minista ya ƙi amincewa da ya karɓi y'an ƙwadago saboda ya nuna cewa koke-kokensu ba su cancanta ba.

Illetré : Mai baƙin kai ; wanda bai koyi karatu da rubutu ba : mutunen da bai je makarantar boko ba, kuma bai yi yaƙi da jahilci ba. Rishin iya karatu da rubutu abin cizon hannu ne.

Illicite : haram : wanda aƙida ko doka ta haranta. Ya tara dukiya ta haram.

Illimité : maras iyaka : maras maƙura, maras wa'adi. Y'an ƙwadago sun shiga yajin aiki maras iyaka.

Illusion : shucin gizo ; zato : yin lissafe-lissafe na banza, ɗaukar alamu tamkar abin gaskiya. Shucin gizo ya ɓadda shi.

Image : alama : kamannu, halayen (alamun) wata al'umma.

Image de marque : mutunci : darajar mutum, ko ta ƙasa.

Imagination : halin ƙirƙiro wani abu : ƙaga wani abu, ƙirƙiro wani abu ƙirƙiro wani abu.

Imbrication : Alaƙa : gami tsakarin, abubuwa. Alaƙa tsakanin waɗansu abubuwa.

Immatriculation : Lamba : yi wa wani abu shaida. Sanya wa soji lamba.

Immigration : baƙunta : shiga wata ƙasa tare da shirya zama na din-din-din. Baƙin haure.

Immixtion : shigas-higula : tsoma baki cikin harakokin da ba su shafi mutum ba. Babu ƙasar da za ta amince a yi mata shiga-shigula cikin harakokinta.

Immobilier : ƙadarori : abin da ya ƙumshi kayayyaki, ka dukiya. Wurin baje ƙadarori.

Immunité : kariya gaban shari'a : tanadin da doka ke yi wa waɗansu mutane. Bayan an ɗage kariyar da ke gare shi a gaban shari'a, an samu damar gabatar da shi a gaban koti.

Immunité diplomatique : kariyar shari'a da ke ga jakada : rishin damar gabatar da jakada a gaban koti cikin ƙasar da yake jakadanci.

Immunité parlementaire : kariyar shari'a da ke ga ɗan majalisa : tanadin da doka ta yi na babu damar gabatar da ɗan majalisar dokoki a gaban koti idan ba da amincewar buron majalasar dokoki ba.

Impact : Tasiri ; aibu : kawo cikas cikin tafiyar da waɗansu harakoki, sharaɗi. Aibun da yajin aiki ke hadasawa kan fannin tattalin arziki.

Impartialité : rishin nuna son rai : rishin son rai cikin wani abu, aikata wani abu kan gaskiya. Ya gabatar da shari'a ba tare da nuna son rai ba.

Impératif : wajibi, tilas, na doli : Abin da ya ƙasance doli dangance da waɗansu halaye. Abun da ya ƙasance doli (wajibi, tilas)saboda lokaci.

Impérialisme : muƙin mallaka : danne wata ƙasa kan fannin siyasa da kan fannin arziki. Har zuwa yau ƙasashen Afirka ba su fita daga ƙarƙashin mallakar ƙasashen turai ba kan fannin tattalin arziki.

Implantation : halin kafuwa : girkuwa, yin sayu. Kafuwar jam'iyar siyasa cikin wani yanki.

Implication : tsoma baki, shafa kashin kaji, ma'ana : sanya hannu, shiga cikin wani abu. Ma'anar matakin shari'ar da aka ɗauka a fuskar siyasa.

Implicite : Na ɓoye : abin da ba a bayyana ba cikin magana. Sanar da wani abu a ɓoye.

Impliquer : laƙawa : zana sunan mutum da yana da hannu cikin wata haraka. Laƙawa mutum da yana da hannu cikin kuɗin banza.

Impopulaire : Mai baƙin jini : Maras farni jini ; wanda jama'a ba su amince da shi ba ; wanda bai samu goyon bayan talakkawa ba, wanda talakkawa suka yi Allawadai da shi. Dokar da jama'ar ƙasa ba su amince da taba. Doka mai baƙin jini.

Import : fatauci na shigowa da kaya: shigowa da kayay-

yakin kasuwanci daga ƙasashen waje. Yin fatauci.

Import-export : shigowa da fita da kaya : kasuwancin ɗauko kayayyaki daga ƙasar waje, da kuma fitar da kayayyaki.

Importation : Shigowa da kaya : shigowa da kayayyaki daga ƙasar waje. Shigowa de pitaro.

Imposable : wanda biyan karo ya hau kanshi : wanda ake iya tilasta wa biyan karo. Bakin daidai karon da ake yankawa.

Imposition : Lanho, haraji, halin tilastawa : wanda ake aza wa mutum, matsi. An tilasta wa ƙasashen afirka da su matse aljifan gwamnati.

Impôt : lanho : kuɗin da gwamnati ke amsa gun jama'a don aikata abubuwan gyaran ƙasa. Ya wajabta ga kowane ɗan ƙasa da ya biya lanho.

Impôt direct : lanho na kowa da kowa : lanho da ya hau kan mutane da masana'antu.

Impression : alama : tabi'a ta gari ko mugunya dangance da tarbi'ar mutum. Nuna kyak-kyawan alamu.

Imprévoyance : Rishin tsin-kaye ; sake : rishin hasashen gaba, rishin kulawa ; yin sake kan wani abu.

Improviser : Ƙagowa take-yanke : yin wani abu ba shiri cikin gaugawa. Y'a ƙago wani jawabi take-yanke.

Impulsion : Halin haɓakar da, bunƙasa : karfafa wani abu, ba shi daraja. Bunƙasar yawan buɗa ido cikin jaha.

Imputation : 1) ƙaƙe : zargin mutum ba tare da hujja ba. Ƙaƙen da aka yi mishi ya jawo mishi ƙaurin suna.

2) **keɓewar waɗansu kuɗi**. keɓe waɗansu kuɗi kan wani fannin jin daɗin rayuwar jama'a.

Inaliénable : wanda baya ƙwatuwa : abin da babu damar dawowa kanshi. Y'ancin da ba ya ƙwatuwa.

Inapte : kasasshe : wanda bai dace ba. Wanda ba ya iyawa. Ƙasasshen mutum.

Inauguration : Bikin buɗe wani abu : sabgogin da ake shiryawa a albarkacin buɗe wani taro, ko buɗe wata ma'aikata. Ministan kiyaye lafiyar jama'a ya shugabanci bikin buɗe wani gidan haihuwa a cikin wata unguwa.

Incapacité : halin kasawa : halin wanda ya kasa aikata abin da ya rataya a wuyanshi. An tsige daraktan dangance da kasawarshi a game da aiki.

Incarnation : Tabbaci : shaida : mai tabbatar da wani abu. Shugaban jamhuriya shi ne tabbacin (shaidar) haɗin kan ƙasa.

Incarner : Tabbatar da : zama shaida : tabbatar da tafiyar da wani abu. Malamin shari'a shi ke tabbatar da shari'a.

Incitation à la rebellion : tunzurawa ga shiga tawaye : iza wadansu da su dauki makamai don tayar wa hukumomi kayar baya. Kin daratta hukumomi. An kare shi daga cikin kasarshi saboda yana tunzura mutane da su shiga tawaye.

Incohérence : rishin kan gado : rishin tsari, maras digi. Kishin kan gadon wani jawabi.

Incompatibilité : rishin gamuwa : rishin damar rike mukami da yawa gaba daya. Rishin gamuwar wadansu mukamai.

Inconditionnel : cikakke : maras ragi, wanda ba ya dauke da sharadi ko guda. Magoya bayan yan siyasa sun dauki niyyar kawo cikakken goyon baya ga shugabannin jam'iyarsu.

Inconscience : Rishin sanin ciwon kai : halin aikata wadansu abubuwa ba tare da yin nazari ba, aikata abubuwan da ba su dace da doka, da kuma al'adu ba, rishin sanin ciwon kai daga magabaci.

Inconstitutionnalité : rishin dacewa da doka : halin abun da bai dace da tsarin mulki ba. Jam'iyun siyasa na bangaren adawa suna nuna rishin dacewar kudirin da majalasar dokoki ta dauka da doka.

Incontestable : maras tambaba : wanda ba ya da shakku cikinshi ko guda, wanda babu damar kin amincewa da shi. Ya lashe zaben babu wata tambaba.

Inculpabilité : Halin tabbatar da laifi : tabbatar da zargin da ake yiwa mutum. An tsayar da shi saboda an tabbatar da laifin da ya aikata na sata.

Inculpation pénale : darmi : tsarin da ake yi wa mutum dangance da laifin da ya aikata.

Inculpé : wanda ake tuhuma : mutunen da ake zargi da aikata laifi. Yi wa wanda ake tuhuma tambayoyi.

Inculper : tabbatar da laifi : mutunen da aka kama da laifi bayan an yi mishi shari'a. An tabbatar da kashin kan da barawo ya aikata.

Indemnisation : Diyya : Bai wa mutum wadansu yan kudi don shafe mishi hawaye, ranko, ramuwa. Gwamnati ya bayar da diyya ga mutanen da yan makaranta suka jawo wa hasara.

Indemniser : bayar da diyya : yi wa mutum ranko, ramuwa. Bayar wa jama'a diyya.

Indépendance : yanci : cin gashin kai kan fannin siyasa, ko kan fannin tattalin arziki, yancin

ƙasa. Y'ancin kafofin watsa labaru.

Indépendance des tribunaux : y'ancin koti : cikakken y'anci daga mashari'anta daban-daban na gudunar da ayyukansu ba tare da gwamnati ya yi masu shisshigi ba.

Indépendance économique : cin gashin kai kan fannin tattalin arziki : samun damar biyan buƙatunsa kan fannin tattalin arziki ba tare da an nemo gudummuwa ba a ƙetare.

Indépendance nationale : y'ancin kan ƙasa : ƙasar da ke cin gashin kanta kan fannin siyasa, mulkin kai.

Indépendant : mai y'ancin kai : wanda ba ya rakuɓa ga wani, mai cikakken y'anci. Ya kyautu da ƙungiya mai shirya zaɓe ta zama mai cikakken y'anci.

Indicateur économique : alamun tattalin arziki : abubuwa da ke nuna halin da tattalin arziki yake ciki a cikin ƙasa, a cikin wani lokaci. Alamun tattalin arzikin ƙasar Nijar baƙi ƙirin suke a game da kwantawar harakokin tattalin arziki.

Indice : shaida : alama mai nuna zaman wani abu. Shaidar halin jin dad'in rayuwar al'umma..

Indignation : ɓacin rai : halin zama cikin baɓin ciki bayan da aka nuna wa mutum rishin adalci. Musulmi sun shiga cikin wani halin ɓacin rai bayan da aka tsayar da shugabansu.

Indispensable : Mai mahimmanci : wanda ya dace, abin ƙwarai. Kawar da son rai ga shugaban jamhuriya abu ne mai mahimmanci ƙwarai cikin tafiyar da harakokin shire-shiren zaɓe cikin ƙasa.

Indûment : A ƙauce : aikata abin da ba ya kan ƙa'ida, wanda bai dace ba. A ƙauce ya samu shugabancin jam'iyar.

Industrialisation : Halin **girka masana'antu** : kafa masana'-antu na sarrafa abubuwa don haɓakar da tattalin arziki. Girka masana'antun cikin ƙasa.

Industrie : masana'anta : masana'antu masu sarrafa abubuwan amfanin jama'a. Masana'antun ƙasa.

Inégalité : Rishin adalci : nuna son rai, raba d'ayan biyu, bambanci. Tashi tsaye kan masu nuna rishin adalci.

Inégalité sociale : bambance-bambance tsakanin jama'a : bambancin da ake samu cikin jama'a dangance da hali da matsayin mutane.

Inéligibilité : rishin cika sharud'd'an zaɓe : mutunen da bai cika sharud'd'an shiga takara ba. Rishin cika sharud'd'an zama d'an takarar majalisar dokoki.

Inéligible : wanda ba ya iya shiga taƙara : d'an takarar da bai

cika sharuɗɗan zaɓe ba. Wanda ba ya shiga takarar zaɓe.

Inflation : tashin kuɗi : hawan kuɗin kayayyaki a kasuwa, tsada karya darajar sefa ya kawo tashin kuɗin cimaka.

Infliger : hakuntawa : yi wa mutum hakunci, cin tara. Hakunta ma'aikaci.

Influence : Faɗi-a-ji, hanya : halin mutumen da ake ɗaukar zancenshi a cikin wuri, wanda ra'ayinshi ke da ma'ana. Yana faɗi a ji ƙwarai cikin jam'iyarshi.

Influencer : Izawa : juyar da ra'ayin mutum, canza mishi ra'ayi ba da son shi ba. Bai cancanta ba sarakan gargajiya su riƙa iza masu zaɓe a cikin yankunansu.

Information : Labari : labarun da kafofin watsa labaru ke gabatarwa. Bayar da labaru.

Infraction : taka doka : aikata laifi, rishin bin ƙa'ida. Kowa ya taka doka tana taka shi.

Infrastructure : kayan aiki : dukan kayan yakin da ake amfani da su don tafiyar da wani aiki. Kayan aikin yan makaranta.

Ingénieur : Injiniya : mai ilimin ƙirƙirowa, mai kuma nazari kan abubuwa. Kasar Nijar na buƙatar injiniya kan fannin noma don zamanintar da aikin noma.

Ingérence : shigunshigula : tsoma baki cikin abin da bai shafi mutum ba. Yin shigunshigula cikin harakokin wata ƙasa.

Non ingérence : Rishin yin shugunshugula : rishin tsoma baki cikin sha'anin da bai shafi mutum ba ; rishin shiga cikin abin da bai shafi mutum ba.

Ingratitude : Butulci ; rishin godiya : halin wanda ba ya ganin ƙoƙarin da ake yi mishi, mai renuwa.

Inhospitalier : wanda ba ya son baƙi : wanda ba ya karɓar baɓi da hannu biyu, maras kirki. Al'ummar da ba ta karɓar baƙi.

Inhumain : rishin imani : maras imani, maras tausai. Ana yi wa masu kason ra'ayin siyasa duka ta rishin imani.

Initiation : koyo : nuna wa mutum hanyoyin iya wani abu. Koyon aikin hannu.

Initiative : tsirawa : aikin ƙirƙiro wani abu, tarkar wani abu. Ya ɗauki niyyar tsira gidan wallafa litattafai.

Initiative privée : niyyar girka abin kansa : girka wata ma'aikata mai zaman kanta.

Initier : fitar da : ɓullo da wani abu, ɗaukar wata niyya ya fitar da wata sabuwar niyya.

Injustice : rishin adalci : abin da babu gaskiya cikinshi, zalumci. Rishin adalci cikin ƙasa.

Inné : Na baiwa : wani abin da ake halittar mutum dashi, ko kuma wani abin da ke tare da

mutum tun haihuwarshi. Samun baiwa daga Allah.

Innocence : rishin laifi : matsayin wanda ba ya da hannu cikin aikata wani laifi.

Innocent : maras laifi : wanda ba ya da laifi. A yi mishi dukar tsiya duk da ba ya da laifin komi.

Innocenter : wanke laifi : bayyana rishin hannun wani cikin wata haraka. Wanke hannun mutum cikin wata haraka.

Innovation : sauyi : kirkirowa, sabin canje-canje. Kawo sauyi.

Innover : fitar da sabon abu : fitar da wani sabon abu, kawo sauye-sauye. Gwamnatin kasar Nijar ya fitar da wani sabon tsari kan horo da bayar da ilimi.

Inquiéter : tayar da hankali : razana halin rayuwar jama'a. Tayar da hankalin jama'a cikin kasa.

Inquiétude : Damuwa, rishin kwanciyar hankali : rishin jin dad'i dangance da jin wani tsoro, ko a game da lissafin duniya zama cikin rishin kwanciyar hankali.

Inscription : rubutu : d'aukar sunan mutum, rubuta sunan mutum kan wani kirgam. Duk d'an takara sai ya zuba diyya don a rubuta sunanshi kan jerin mutane masu neman takara.

Inscrire : rubutawa : d'aukar sunan mutum kan wata takarda, ko cikin wani kundi. Ya rubuta sunanshi kan jerin y'an takara masu neman zama y'an majalisar dokoki.

Inspecter : Dubawa, yin larwai : gudanar da bincike, yin kididdigi kan wad'ansu abubuwa. An gudanar da larwai a cikin wad'ansu ma'aikatan gwamnati.

Inspecteur : "Speto ": mai kula da kiyaye wani abu, ko mai kula da gudanar da larwai da bincike cikin tafiyar da harakokin kasa.

Inspection : Larwai : halin kiyaye wani abu, ko tafiyar da bincike. Larwai kan wad'ansu abubuwa.

Inspiration : kwaikwayo ; bud'i: bin shawarar wani, d'aukar hanyar da ya bi. Ya kwaikwayi malaminshi wajen wallafa littafinshi.

Inspirer : kwaikwaya : yin amfani da shawarar wani, d'aukar hanyar da wani ya bi. Kwaikwayar malaminsa.

Instabilité : rishin girkuwa : halin abun da ke tangal-tangal, wanda ba tsayayye ba. Rishin girkuwar mulkin demokarad'iya a kasashen Afirika.

instabilité politique : rishin kwanciyar hankali kan fannin siyasa : yawan tsegungumma dangance da siyasa cikin kasa.

Instabilité sociale : rishin kwanciyar hankalin jama'a : tashe-tashen hankali cikin kasa.

Instabilité économique : rishin girkuwar tattalin arziki : rishin daidaituwar harakokin tattalin arziki cikin ƙasa.

Instable : wanda bai girku ba : wanda bai daidaitu ba, wanda ba tsayayye ba. Mulkin da bai girku ba.

Installation : girkawa : shinfiɗawa, azawa. Girkawar majalisar dokoki.

Instance : Ma'aikata.

Instance dirigeante : shugabani. Magabatan jam'iya.

2) shire-shiren gabatar da shari'a. Shigar da ƙara.

Instance suprême : mahukunta na ƙoli : masu tafiyar da hukunci cikin ƙasa.

Instance de concertation : ƙungiyar bayar da shawara : ƙungiya mai bayar da ra'ayinta kan waɗansu abubuwa.

Instance de décision : Hukumar yanke shawara : hukumomi masu tafiyar da hukumanci.

Instauration : shinfiɗawa : girkawa, kafawa. Shinfiɗa mulkin demokaraɗiya.

Instigation : Tunzurawa : halin iza mutane ga yin waɗansu abubuwa, masu hasa wuta. Doka na hukunta masu tunzura mutane ga ƙin bin ƙa'idodi da oda.

Instituer : kafawa : fitar da, shinfiɗawa. An kafa dokar ta ɓaci.

Institut : tsangaya : wuraren karatu na ilimi mai zurhi. Tsangayar karatun ilimin siyasa.

Institution : Ƙungiya, ma'aikata : dukan tsare-tasare da ƙa'idodin da ake shinfiɗawa don jin daɗin rayuwar jama'a. Ƙungiyoyin ƙasa.

Institution de développement : ƙungiyoyin ci-gaba : ƙungiyoyin da ake kafawa don ci-gaban ƙasa.

Institution non étatique : ƙungiyoyi masu zaman kansu : ƙungiyoyin da ba na gwamnati ba.

Institutions bancaires internationales : ƙungiyoyin harakokin kuɗi na duniya : ƙungiyoyin bankuna masu bayar da lamani.

Institutionnel : wanda ya shafi tsarin ma'aikatun gwamnati: dukan abubuwan da suka shafi tsarin ma'aikatu. Dokokin da suka dace da tsarin ma'aikatu.

Instruction : 1) Bincike : hanyoyin gabatar da shari'a. Bincike don gabatar da shari'a.

2) **Umurni** : halin bai wa wani oda don aikata wani abu. Diktar ya bai wa sakatarinshi umurni kahin ya tafi.

Instruire : bayar da ilimi : bayar da horo da ilimi, ƙarfafa

sanin mutum. Wajibi ne a bai wa dukan y'an ƙasa horo da ilimi.

Instruire un dossier : shire-shiren gudanar da shari'a.

Instrument : abin aiki : wani abin da ake amfani da shi wajen tafiyar da wani aiki. Kayan aiki.

Instrument juridique : abun da ya shafi ilimin shari'a : dokoki, da ƙa'idodi.

Insubordination : rishin ladabi da biyayya : ƙin daratta na gaba, ƙin bin umurninsa. An sallami waɗansu ma'aikata don rishin ladabi da biyayya daga gare su.

Insuffisance : ƙaranci : rishin isasshen wani abu, ƙwabro. K'arancin abinci.

Insunier : Nunawa a faƙaice: yin gugar zana ; faɗin wani abu cikin karin magana (cikin habaici). Fadin abu a faƙaice.

Insurrection : tarzoma ; tawaye : tashin hankali, hargitsi. Shirya gagarumar tarzoma.

Intégralité : sarai ; gaba-ɗaya: halin avun da ba ya da ragi, cikakke. Ya biya bashinshi gaba-ɗaya (sarai).

Intégration : sanyawa ; shiga: sanya mutum cikin wani wuri, yi wa mutum wuri. Sanya tsaffin y'an tawaye cikin ma'aikatun gwamnati.

Intégration sociale : shiga cikin al'umma : nema wa mutane gidin zama cikin jama'a ; nema wa mutane aikin yi domin su samu damar tafiyar da rayuwarsu cikin jin daɗi.

Intégration économique : ƙarfafa danƙon kasuwanci : ƙara ƙarfin kasuwanci tsakanin ƙasashe.

Intègre : mai adalci : mai riƙe amana, wanda ba ya zalumci. Shugaban ƙasa mai adalci.

Intégrer : shigar da : sanyawa. Ya yi murabus daga jam'iyarshi don ya shiga cikin wata jam'iya.

Intégrité : cikakken hankali : mutunen da ke da ƙoshin lafiya. Tayar da kwanciyar hankalin mutum.

Intégrité physique : cikakkar lafiyar jiki : halin mutumen da ba ya da massakanta ko guda.

Intégrité morale : cikakken hankali : halin mutumen da hankalinshi bai taɓu ba ko kaɗan.

Intellectuel : ɗan takarda, mai ilimi : mutumen da ya yi karatun boko. Y'an takardar ƙasashen Afirka.

Intelligibilité : Fahinta : halin abu wanda ke ganuwa ; abin da ake fahimta da sauƙi, maras ɗarmin kai. Faɗin maganar da ake ganewa.

Intelligible : Mai sauƙin fahintuwa : mai haske, wanda ake ganewa. Ya yi wa jama'a jawabi mai haske.

Intention : niyya : sanya ran aikata wani abu. Shugaban ƙasa na da niyyar rushe majalasar dokoki.

Inter-gouvernementaux : na tsakanin ƙasashe : wanda ya shafi gwamnatocin ƙasashe da yawa. Haɗuwa ta tsakanin ƙasashe.

Inter-régional : na tsakanin jaha da jaha : wanda ya shafi jahohi daban-daban. Yarjejeniya tsakanin jahohi.

Inter-dépendance : cuɗayyar juna : game ƙarhi don tafiyar da wani abu. Akwai cuɗayyar juna tsakanin ƙasar Nijar da ƙasar Nijeriya kan fannin harakokin kasuwance.

Interdiction : haram, hani : abin da dokar ƙasa ko aƙida ba su amince da shi ba. An haramta shigowa da miyagun ƙwayoyi a ƙasar Nijar.

Intérêt : Amfani : (cin) riba, (cin) moriyar wani abu, (cin) amfanin wani abu.

Intérêt national : amfanin ƙasa : abin da ya kasance alheri cikin ƙasa.

Intérêt fondamentaux de la société : Muhimman amfanin jama'a : abin da ya fi zama alheri ga jama'a.

Intérêt moraux et matériels : yancin jama'a : abin da yake da amfani ga mutumci da mallakar jama'a.

Intérêt corporatiste : yancin yan ƙungiya guda : abin da yake yanci ga waɗanda suke cikin ƙungiya guda.

Intérieur : na cikin gida : wanda ya shafi harakokin cikin gida. Siyasar cikin gida.

Intérim : Na wucin gadi ; muƙaddashi : mutumen da yake riƙe wani muƙami idan ya kasance mai wurin ya yi balaguro, ko ba shi da dama.

Interlocuteur : Abokin tattaunawa : mutumen da ake zaman sasantawa da shi. Samun cikakken abokin tattaunawa.

Intermédiaire : mai shiga tsakanin : mutunen da ke shiga tsakani wajen sasanta mutane, ko ɓangarori daban-daban. An naɗa shi a matsayin mai shiga tsakani.

Interministériel : Na tsakanin ministoci : wanda ya ƙumshi ministoci da yawa. An kafa wani kwamiti wanda ya ƙumshi ministoci da yawa.

Internat : gidan kwanan yan makaranta : ɗakunan da ke bakuntar. Yan makaranta. Ya kyautu a riƙa tsabtata gidajen kwanan yan makaranta.

International : Na ƙasashe : abun da ya shafi ƙasashe da dama ; abun da ke gudana tsakanin ƙasashe. Huldodi ko dangantaka tsakanin ƙasashe.

Interne : Na daga ciki : abun da ke daga ciki. Jam'iyyar na huskantar matsaloli daga cikinta.

Interpellation : 1.) Kira : gayyatar da y'an majalisar dokoki ke yi wa wani minista don ya zo ya bada bayyani kan wani al'amari. Ministan harakokin noma ya amsa kiran y'an majalisar dokoki inda ya bayar da amsoshin tambayoyinsu a game da rikice-rikice tsakanin manoma da makiyaya.

2.) Tambayoyin da y'an sanda ke yi wa mutum a lokacin da suke yin wani bincike. Y'an sanda sun yi wa mutane da yawa tambayoyi a lokacin zanga-zangar y'an adawa.

Interpeller : Tsayar da : cilasa wa mutum da ya bayar da amsa ; tambayar shi bayyani. Y'an sanda sun tsayar da shugaban wata jam'iyyar adawa.

Interprétation : Ma'ana : halin bayar da nufi, da bayyani. Ma'anar wata ayar doka ta cikin tsarin mulki.

Interprétation juridique : Ma'ana ta huskar shari'a : bayyani a fannin shari'a.

Interprête : Mai fasara : mai yin fasara daga wani harshe zuwa wani. neman gudunmuwar mai fasara.

Interpréter : Bayar da ma'ana : bayar da bayyani ; ganar da. Kahohin labaru masu zaman kansu sun bayar da ma'anar jawabin shugaban kasa.

Intervenant : Mai magana : wanda ya d'auki magana cikin mutane. An yi wa mai magana tabi.

Intervenir : 1.) Daukar magana : magantawa don bayar da ra'ayinsa. Magantawa cikin radiyo.

Sanya hannu : aikatawa kai hari. Y'an sanda sun sanya hannu don tarwatsa masu zanga-zanga.

Intervention : Sanya hannu/ shiga : sa baki cikin wani al'amari ko wata shari'a ko wani rikici. Shigar y'an sanda cikin jami'ar Yamai.

Interventionnisme : Sanya hannu : tsarin da ke bai wa gwamnati damar sanya hannunta cikin harakokin tattalin arziki. Sanya hannu da gwamnati ke yawan yi, shi ya haddasa karewar kampanoni.

Interview : Hira : ganawa da wani tare da yi mashi tambayoyi a game da wasu ra'ayoyinshi ko wasu tsare-tsarenshi don bayyana su, ko kuma yin wani amfani da su. Hira ta radiyo da radiyo-mai-hoto.

Intimidation : Ban tsoro : turji, burga - Y'an adawa ba su ja da baya ba duk da ban tsoro da ma'ikanta suka yi.

Intimider : Bayar da tsoro : turzawa, hirgitawa. Ya bai wa abokin hamayyarshi tsoro.

Intitulé : Suna : Laƙani kan bayyani, kan littafi ko na babi, ko na wata doka ... Sunan littafi.

Intolérance : Rishin girmamawa ; ƙyama : rishin haƙuri, tsana a game da duk wanda ba a da ra'ayi guda da shi, ko addini guda.

Intolérance idéologique : ƙyamar ra'ayi : rishin haƙuri da duk wanda ba a da ra'ayi guda da shi.

Intolérance réligieuse : Kyamar addini : rishin haƙuri da dukan wadanda da a da addini guda da su.

Intoxication : Sharri : Karyace-karyace : Y'an adawa suna ƙulla wa gwamnati sharri.

Intransigeance : Tsageranci : Halin wanda ba a sasantawa da shi, wanda ba ya tanƙwasuwa. Gwamnati ta ki ja da baya duk da tsagerancin ma'aikata

Intrigue : Makirci : zambar da ake shiryawa don samun wani abu ko don yi wa wani lahani. Makircin siyasa

Introduction : Shigowa : sanyowa, kawowa. Shigowar ƙwaya cikin ƙasar Nijar na faruwa ta hanyar fasa-ƙwabri.

Introduire : Shigar da : gabatar da, amincewa, yin na'am. Shigar da wata ayar doka cikin tsarin doka. introduire un recours : shigar da ƙara : kai ƙara, neman hakki.

Intronisation : Nadin sarauta : wankan sarauta. Jama'a da dama sun halarci nadin sarauta.

Introniser : Nada sarauta : nada (rawanin) sarkin gargajiya. An nada sabon sarki bayan rasuwar sarki.

Intrusion : Katsalandan : shiga ba tare da samun gayyata ba. Katsalandan din yan gudun hijira a cikin wata ƙasa.

Intuition : Ji-ga-jiki : ilhani, gano wata gaskiya ba tare da yin wani nazari ba. Ya ji zuwan bala'in ga jikinshi.

Invalidation : Sokewa : ƙin aiki da ... Sokewar sakamakon zaɓe.

Invalide : 1.) **Nakasasshe :** masaki, wanda ya rasa wani abu daga cikin sassan jikinshi, da ba ya iya yin aikace-aikace.

2.) **Wanda bai dace ba :** wanda bai karɓuwa a dokance. Matakin da bai dace ba.

Invalider : Sokar da : bayyana, rishin karɓuwa. Sokar da zaɓe cikin wasu yankunan zaɓe.

Invariable : Wanda bai sauyawa.

Invasion : Mamaya : mamayewar ƙasa da ƙarhin soja. Mamayar da Iraki ta yi wa Koweti, ita ce makasudin yakin taikun pasha a shekarar 1991.

Inventaire : Kidaya : lissahi dalla-dalla. Y'in Kidaya

Inventer : Ɓullo da : Kirkira, ƙaga samowa, ƙera wani sabon

abu. Kungiyar ma'aikata ta ɓullo da wani salo na kokowar kare hakkin ma'aikatan.

Invention : Ɓullowa : Kirkirawa, ƙagawa, ƙerawar sabon abu, ganowa. Ɓullowar (ƙagowar) Kamfas ta bai wa turawa damar bincike (mallake) nahiyar Afirika.

Investigation : Bincike : nema a hankali kwance, bin diddigi. An gudanar da bincike don gano dalillan hatsarin.

Investir : Haudawa kan mulki : miƙa wa wani sandar iko, aza wa wani nauyin wani aiki. Hauda shugaban jamhuriya kan kujerar mulki.

Investissement : Zubin jari : zubin kuɗi don kyautata amfanin wani abu, don ƙara riba. Zubin jari daga wajen ƴan kwangila cikin masana'antun ƙasa na iya farfaɗo ayyukan tattalin arziki.

Investissement humain : halin bayar da isassun mutane.

Investisseur : Ɗan zuba jari : wanda ke saka kuɗi. Ɗan zuba jari mai zaman kanshi.

Investiture : Naɗi: haudawa kan mulki : miƙa wa wani sandar mulki a bainar jama'a. Manyan mutane da dama sun halarta wurin naɗin shugaban jamhuriya kan mulki.

Inviolabilité : Rishin takuwa : halin abun da ba a iya take shi. Dokar da ba ta takuwa.

Invité : Baƙo : Wanda ake gayyata ga wata sabga. Kulawa da baki.

Invité d'honneur : baƙon daraja, babban bako.

Involontaire : Ba na gangam ba : abun da ake aikatawa ba tare da niyyar aikata shi ba. Abun da ya kubce wa mutum. Aikin da ba na gangam ba.

Irrécevabilité : Rishin karɓuwa : halin abun da ba a iya na'am da shi. Rishin karɓuwar wani ƙara (kuka)

Irréfutable : Na gaskiya : abun da babu shakka cikin shi, babu gardama kan shi. Hujjojin da ɗan shaidar ya bayar na gaskiya ne.

Irrégularité : Maguɗi : rishin bin ka'ida (gaskiya), rishin haske ga abu. Ɗan adawa sun bayyana maguɗɗan da aka tabka ga zaɓen da aka gudanar.

Irrégularités graves : Manyan maguɗɗai : maguɗɗan da ke iya sawa a soke sakamakon zaɓe.

Irrégularités mineures ƙanƙanan maguɗɗai : maguɗɗan da ba su iya sawa a soke sakamakon zaɓe.

Irréprochable : Maras laifin komi : wanda ba a iya wa suka ko zargi. Ba ya da laifin komi cikin zamanshi da magabatanshi.

Irresponsable : Maras sanin ciwon kanshi : wanda ba ya kama girmanshi ; wanda ke aikata abubuwa ba tare da lissafi ba.

Irrévocable : abun da ba ya taduwa : abun da ba ya sauyuwa, da ba a dawowa kan shi. A lokacin mulkin kama-karya, matakan da gwamnati ta ɗauka ba su taduwa.

Itinéraire : Hanyar bi : hanyar da za a ɗauka. Hukuma ta ƙayyade wa masu zanga-zanga hanyar bi don kiyaye dabanci.

J

Jachère : Sabra (saura) : shaya, sankara, hutawar wurin noma a tsawon shekara 1 ko 2. Ya bar gonarshi sabra.

Jalon : Hanya : abun da ke nunawa, abun kwatanci. Aza ƙasa bisa hanyoyin zamani.

Jalonner : Nuna hanya : Ƙayyade hanya. Nuna hanyar da za a bi

Janvier : Janairu : wata na farfo na kalendiren kirista. Cikin watan Janairu ne ɗ'ari ke farawa a Nijar.

Jeunesse : Ƴ'arinta/Ƙurciya/ matasa : lokacin rayuwa daga farkon yarinta zuwa dattako. Kowace ƙasa na aza gurinta kan matasa.

Joueur : Ɗan wasa : mai yin wani wasa. Ɗan wasan ƙwallon ƙafa

Joug : Danniya : mallaka, matsatsi. Kahin su samu ƴancin kansu, ƙasashen Afirika sun zama ƙalƙashin mulkin danniyar turawa.

Jouir : Amfana : yin amfani, cin moriya. Masu amfana da cikakken ƴancinsu na ƴan ƙasa, su ke iya aje takararsu ga zaɓen ƴan majalisar dokoki ko na shugaban ƙasa.

Jouissance : Jin daɗi : nishaɗi. Jin daɗin wani abu.

Journal : 1.) **Jarida** : takarda inda ake bayyana labarun rana-rana a rubuce. Jaridar mako-mako, mujalla, ko sati-sati.

2.) **Hilin labarun** da ƴan jarida ke gabatarwa cikin radiyo ko radiyo-mai-hoto. An bayar da cikakkun labaru cikin hilin labaru.

Journal officiel : Mujallar gwamnati : jaridar hukuma mai bayyana labarun hukuma. Mujallar gwamnati ba ta bayyana labarun ƙarya.

Journaliste : Ɗan jarida : mai aikin rubutu labara cikin jaridu ko bayar da labaru cikin radiyo ko radiyo-mai-hoto.

Judiciaire : Na shari'a : abun da ya shafi shari'a, da ya danganta da shari'a. An ɗ'auki matakai na shari'a don tuhumar masu yin kuɗ'in ganye.

Juge : Juju : mai yin shari'a, alƙali, mahukunci. Jujun sasantawa.

Jugement : Shari'a : hukuncin da koti ya yanke. Yanke shari'a

Jugement de valeur : shari'a, yabo : ra'ayoyin da ake bayar don nuna mahimmancin wani abu.

Jugement équitable : shari'ar adalci : hukunci na gaskiya.

Juger : 1.) Bayar da ra'ayi : faɗar yadda mutum ya gani. Ga nashi ra'ayi, gamin bai yi daidai ba.

2.) **Yanke shari'a :** yanke hukunci. An yanke wa wani shari'a bisa laifin handamar dukiyar jama'a.

Juillet : Yuli : wata na bakwai cikin kalandiren kirista.

Jumelage : Tagwaitawa : haɗa dangantaka. Al'ada ta haɗa dangantakar tagwaici tsakanin garuruwa biyu na ƙasashe biyu daban-daban don kafa huldɗa tsakanin su. Tagwaitawar birnin tasawa na ƙasar Nijar da birnin KOT DARMOR na ƙasar Faransa.

Junte : Mulkin soja : gwamnatin da ke bisa iko ta hanyar juyin mulki. Mulkin soja na Nijar ya kafa wani gwamnatin farar hula.

Juré : Mamban masu shari'a : wanda ke cikin rukunin masu gudanar da shari'a. Ya amince da zama mamban masu shari'a.

Jurer : Rantsewa : ɗaukar alƙawalin yin wani abu a bainar jama'a. Ɗan shaidu ya rantse da ƙura'ani.

Jurer solonnellement : Rantsewa a bainar jama'a : ɗaukar niyya (alƙawali) a gaban jama'a

Jurisconsulte : Mai ilimin shari'a : Kwararren masanin dokoki, mai bayar da ya shawara kan duk abun da shafi shari'a. Wani ma'aikaci ya buƙaci shawarar malami mai ilimin shari'a kahin ya kai ƙaran maigidanshi.

Juridiction : Hurimi : ikon gudanar da shari'a ; ikon yanke shari'a ; dukan illahirin koti-koti masu matsayi ɗaya.

Juridiction d'exception : Hurimi na masamman : shari'ar da babu ruwanta da aiki da doka, sai abun da hukuma ta ce.

Juridiction provisoire : Hurimin ƙaramin lokaci : shari'ar da ake gabatar kahin wani lokaci.

Juridictionnel : Na hurimi : wanda ya shafi ikon gabatar da shari'a. Ikon yanke shari'a.

Juridique : Na shari'a : abun da ake yi kuma a gabatar da shi ta hanyar shari'a gaban koti. Bi ta hanyar shari'a.

Fait juridique : Abu na shari'a: abun da ya danganta da shari'a.

Vide juridique : rishin matakan shari'a : rishin dokoki game da wani hali ko wani al'amari.

Jurisprudence : Fiƙihu : dukan ƙa'idodi ko matakan shari'a game da wani fanni, ko na wata ƙasa ; hanyar da wani koti ke ɗauka don gabatar da shari'a kan wani al'amari, dukan ƙa'idodin shari'a da ake amfani da su a game da al'amarin. Dokokin da suka saɓa wa al'adu da haƙiƙannan abubuwa na

ƙasar Nijar, ya kamata a sake su daga fikihin ƙasar.

Juriste : Mai ilimin shari'a : wanda ke da sani kan harakokin shari'a, shahararre kan harakokin shari'a. Ya cancanta malamai masu ilimin shari'a su sa hannu sosai wajen wallafa dokokin ƙasa.

Jury : Zaɓaɓɓun alƙalai : kwamiti da aka keɓe don nazari kan wani zance ko wani mai jarrabawa. Rukunin masu shari'a da aka keɓe masamman don gudanar da wata shari'a. Shugaban zaɓaɓɓun alƙalai ya bayyana sakamakon jarrabawa.

Justice : Adalci : kyakkyawar aƙida ta shari'ar gaskiya, bin gaskiya. Ya kyautu ma'ikanta su riƙa adalci.

Justice sociale : Adalci wajen al'umma : tabbatar wa kowane ɗan ƙasa yancinshi da darrata yancin

Justiciable : Na koti : abun da ya shafi koti, da koti ke iya yanke wa shari'a.

Justification : Hujja : dalili, bayyani. Kawo hujjoji.

Justifier : Bayar da hujja : gaskantar da, bayar da mafari, da bayyani, karewa, ɗebe zargi. An tambaye shi ya bayar da hujja a game da fashin da ya yi.

Juvénile : Na matasa : abun da ya shafi matasa (yara). Shashanci na matasa a Nijar, ya kai wurin bada tsoro.

L

La Nigérienne : Taken Nijar : taken (waƙa) da ake yi wa ƙasar Nijar. An kaɗa taken Nijar.

Laboratoire : Ɗakin gwaji : wurin da aka gyara don aikata gwaje-gwaje, da binciken kimiyya.

Laborieuse : Mai son aiki : mai aiki da yawa, mai ƙwazo ga aiki. Al'ummar Nijar mai son aiki ce.

Lacune : Ƙaranci : Kaɗanci, abun da ke son ƙari, halin ragaggen abu, giɓi, rishin isa. Magance ƙaranci.

Laicité : Rishin alaƙa da addini : rishin bambancin addini

Laïque : Na rishin bambancin addini : abun da ba ya da alaƙa da addini. Nijar ƙasar rishin bambancin addini ce.

Laissé-pour compte : Wararre: mutunen da al'umma ta ware, wanda ba ruwan kowa da shi.

Laisser : Bari : sakawa, yardawa, ƙin ɗauka (karɓa). Ya bari wata cikakkar sa'a ta wuce shi.

Laisser-aller : Rishin kula : rishin lura, rishin tsari, sakaci, hali inda kowa ke yin abun da ya so.

Langage : Magana : baiwar da mutane ke da ita ta su faɗi abun da suke tunani, ta baka ko a rubuce.

Langue : Harshe : Hanyar sadarwa (yin magana) da ke ga kowace al'umma. Harsunan ƙasa.

Langue officielle : Harshen hukuma : harshen da ake amfani da shi cikin ma'aikatu, da makarantun boko, da huldɗa da ƙetare.

Latitude : Dama : walwala, iko, hali. Bai wa mutun damar aikata wani abu.

Lauréat : Wanda ya ci lambar gasa : wanda ya ci wata nasara. Ministan matasa, da wasanni, da haɗin kan ɗan ƙasa, shi ya miƙa wa waɗanda suka ci lambar gasa tukwicinsu.

Leader : Shugaba / Madugu : mutumen da ke jagorancin wata jam'iyar siyasa, ko wata ƙungiya. Madugun ɗan adawa.

Leadership : Shugabanci : jagoranci. Shugabancin wata ƙungiya, wani tsari.

Légal : Na gaskiya/Na halal : abun da ke bisa hanyar doka. Aikata abu na gaskiya

Légalisation : Gaskantawa : sawa bisa hanyar doka ; halalantawa, dimantawa ta hanyar doka. Gaskantawar wata sabuwar jam'iyyar siyasa.

Légaliser : Gaskantar da : dimantar da, halalantar da,

dacewa da doka. Ba za a amincewa da duk takardar da ba a gaskantar da ita ba.

Légalité : Gaskiya : matsayin abun da ke kan gaskiya. An yi rabon kan gaskiya.

Législateur : Mai kafa dokoki : mai ikon fitar da dokoki. A cikin tsarin demokaraɗiya, majalisar dokoki ce ke da nauyin kafa dokoki.

Législation : Ka'idodin shari'a: dukan ƙa'idodin shari'a na ƙasa, ko da suka shafi masamman wani fanni. Ka'idodin shari'a na Nijar.

Législature : Wa'adin majalisar dokoki : Tsawon lokacin da majalisar dokoki ke tahiyar da aikinta (da ikonta). Wa'adin majalisar dokokin jamhuriya ta ukku.

Légiste : Mai ilimin shari'a : shahararren masannin dokoki. Ya nemi gudunmuwar mai ilimin shari'a don wallafa ƙa'idodin jam'iyyarshi.

Légitime : Halattacce/na kan gaskiya : abun da ya dace da doka, na halal. Yana matsawa ƙwarai ga kare ra'ayinshi don ganin cewa na kan gaskiya ne.

Legs : Gado : bara wa wani kyautar dukiya ta rubutacciyar shaida. Bara wa wani gado.

Leitmotiv : Shaida/hali : fasali, zane, shaidar wata al'umma/ halayen wata al'umma.

Lenteur : Nawa : sanyin jiki/sanyin hali, rishin sauri ko hanzari. Nawa cikin tafiyar da wani aiki.

Lenteur administrative : Nawar aikin hukumomi : rishin sauri, sanyin hali cikin tafiyar da aikin hukumomi.

Levier : Matokari : abun da ke bada ƙarhi.

Lexique : Kamus : tsarin kalmomin da harshe ya ƙumsa. Kamus wanda ya shafi wani fanni. Ya sayi ƙamus na kalmomin fannin shari'a don samun sani kaɗan daga shari'a.

Liaison : 1.) **Haɗi :** huldɗa da wani ko tsakanin ƙasashe biyu.

2.) **Sadarwa :** sadarwa ta wayar talho.

Libéral : Na sassauci : na sakin ragama, mai sarari, mai son demokaraɗiya. Jam'iyya mai ra'ayin sassauci.

Libéralisation : Sassauci : Sakin ragama. Sassauci da aka yi wa kahohin labaru ya ba su damar watsa su sosai.

Libéralisation du commerce : Sassauci wajen kasuwanci : sakin ragamar kasuwanci.

Libéralisation du régime : Sassaucin mulki : kawo mulkin demokaraɗiya.

Libéralisme : Darattawa : daratta yancin wani. Daratta yancin yin siyasa.

Libéralisme économique : ra'ayi na daratta yancin kowa na yin kasuwancin da yake so, sakin ragamar kasuwanci.

Libéralité : Taimako : Sadaka, kirki, halin kyauta. Kawo taimako ga waɗanda ke cikin mawuyancin hali.

Libération : Neman yancin kai : Saki, kwatar yancin, samun walwala. Kungiya mai neman yancin kan wata al'umma.

Libérer : Sakawa : bai wa wani yancin walawa. An ji wahala ga tattaunawar neman saka yan kaso.

Liberté : Yancin : halin mutunen da ba ya kalkashin kowa, halin aikata abu ba tare da shakkar komi ba. Aikata abu cikin cikakken yancin.

Liberté d'association : Yancin kafa kungiya : damar da tsarin mulki ya bai wa yan kasa na kafa kungiya.

Liberté d'entreprise : yancin yin sana'a : damar da tsarin mulki ya bai wa yan kasa na ɗaukar niyyar gudanar da ayyukan kansu.

Liberté d'opinion et de pensée : yancin bayar da ra'ayi : damar da tsarin mulki ya bai wa yan kasa na bayar da ra'ayinsu da tunani ba tare da tambaba ba.

Liberté de circulation : Yancin zirga-zirga : damar da tsarin mulki ya bai wa yan kasa na yin kai-da-kawo cikin kasa da ketare ba tare da shakkun komi ba.

Liberté de conscience : yancin yin lura : damar da tsarin mulki ya bai wa yan kasa na yin nazari kan al'amurran kasa.

Liberté de correspondance et de communication : yancin sadarwa : damar da tsarin mulki ya bai wa yan kasa na su sada tsakanin su a cikin kasa ko a kasashen waje.

Liberté de culte : yancin yin addini : damar da tsarin mulki ya bai wa yan kasa na yin addinin da ransu ke so ba tare da an tayar masu da hankali ba.

Liberté d'expression : yancin magantawa : damar da tsarin mulki ya bai wa yan kasa na tofa albarcin bakinsu ba tare da shakkun komi ba.

Liberté de presse : yancin kahohin labaru : damar da tsarin mulki ya bai wa yan jarida na watsa labaru a kowane fanni na kasa ba tare da shakkun komi ba.

Liberté de presse, de publication et de publicité : yancin kahohin labaru, na ɗab'i da na yin talla : damar da tsarin mulki ya bai wa yan kasa na buga jaridu, bayyana su da sayar da su.

Liberté de publication : yancin ɗab'i : damar da yan kasa ke da ita na buga jaridu,

litattafai da ƙasidu.

Liberté de publicité : yancin talla : damar da tsarin mulki ya bai wa yan ƙasa na taɗa kayansu wajen jama'a.

Liberté de résidence : Yancin zaben mazauni : damar da y an ƙasa ke da ita na su zauna garin da suke so.

Liberté de réunion : Yancin yin shawara : damar da yan ƙasa ke da ita na shirya taron shawara.

Liberté de choix : yancin zaɓe : damar da yan ƙasa ke da ita na zaben abun da ransu ke so.

Libre : Mai yancin kai : wanda ba ya ƙalƙashin ikon wasu, mai mulkin kanshi, mai cin gishin kanshi, mai zaman kanshi. Nijar ƙasa ce mai yancin kanta. -

Libre administration : ma'aikata (hukuma) mai y ancin kanta : ma'aikatar da ba ta ƙalƙashin jagorancin gwamnati.

Libre échange : Yanci cikin kasuwanci : tsarin kasuwanci mai sassauci tsakanin ƙasashe biyu.

Licence : «Lisensi» : takardar shaidar kammala karatun shekara 3 a jami'a.

Licite : Amintacce : abun doka ba ta hana ba, ta yarde ma. Amintaccen abu.

Lien : Huldɗa : abun da ya haɗa mutum biyu ko abu biyu, dangantaka. Karfafa huldɗar amintakanci

Ligne de mire : Hanyar bi : Kayyadaddar hanyar da za a bi. Zaben hanyar bi.

Ligue : Kungiya : Kungiyar kare hakki a fannin siyasa, ko na addini.. Kungiyar kare hakkin ɗan Adam.

Limites de pouvoir : Iyakar iko : maƙura, bakin iyakar da ba a iya zarcewa ga iko. Tsarin mulki na ranar 18 ga watan yuli 1999, ya ƙayyade dalla-dalla iyakar iko na gwamnati da na majalisar dokoki.

Limogeage : Tsigewa : Saukewa, hiddawa. An buƙaci tsigewar wani ɗan siyasa daga muƙaminshi.

Limoger : Tsigar da : saukar da, hitar da. Wani ya tsigar da ma'aikatanshi a dalilin yajin aikin da suka yi.

Liquidation : 1.) **Aikin karyar da** : saida kaya da araha kacal a dalilin barin kasuwancin ko don shigar da kayan da sauri. Aikin karyar da kampani.

2.) **Baddawa** : kashewa, raba kai da wani. Baddar da abokin hamayyar siyasa.

Liste : Jerin sunaye : sunayyen mutane ko wasu abubuwa ɗaya bayan ɗaya a kan wata takarda. Lissafi, ƙidaya. Fitar da jerin sunayen yan takara ga zaben yan majalisar dokoki.

Liste électorale : Jerin sunayen masu zaɓe.

Litige : Rikici : Jayayya, rishin jituwa, gardandami waɗanda ke iya kawo shiga tsakani. Warware (magance) wani rikici.

Lobby : Y'an ƙumbiya-ƙumbiya : y'an fadanci, y'an kamun ƙafa. Ya tara y'an ƙumbiya-ƙumbiya don su goyi bayan takararshi ta zama sakatarin jam'iyyarshi.

Local : Na ƙaramar hukuma: na jaha : abun da ya shafi wani wuri. Zaɓe na ƙananan hukumomi.

Localité : Gari : ƙaramin birni, wani sanannen wuri, ƙauye. Ya yi kiran taron gangami cikin wani gari kusa da babban birni.

Location : Haya : ɗaukar wani gida ko wani inji, ko bada gida na biya. Hayar gidan tana zo mashi da tsada.

Locuteur : Mai jin wani harshe : mutanen da ke magana cikin wani harshe. A Nijar, masu yin hausa da sunan harshensu na haihuwa sun zarce ƙashi 50 cikin ɗari.

Logistique : Kayan aiki : dukan dubaru, husa'o'i da kayayyakin gudanar da wani tsari, wata sabga. K'asar Faranshi ta kawo wa Nijar gudunmuwar kayan aiki don gudanar da zaɓe cikin sauƙi.

Loi : Doka : matakin da hukuma ke ɗauka wanda ba ya takuwa, wanda ya shafi dukan y'an ƙasa kuma yana ƙayyade hakkin kowanne da abun da ya wajaba kanshi. Dokar ƙasa.

Loi cadre : Dokar babban tsari : doka mai manyan matakai da ake dogara da su don ɗaukar hanyoyin zantarwa ; dokar Houpheit Boigny wadda ta soke aikin badala cikin mallakakkun ƙasashe, kuma ta ƙayyade hanyar da y'an Afirika ya kamata su ɗauka don cin ma mulkin kai.

Loi des finances : Dokar fasalin kuɗi : matakan da gwamnati ke ɗauka a game da tsarin kuɗin da za ta kashewa da kuma za ta samu a cikin shekara.

" Loi organique : Dokar tsarin ma'aikatu.

Long terme : Dogon lokaci : wa'adi mai tsawo. Asusun bada lamani (FMI) da bankin duniya sun bai wa ƙasashen da ke cikin tsarin tada komaɗar tattalin arziki basussuka na biya cikin dogon lokaci.

Lotissement : Tsarin hilaye : yankan hilaye don gina gidaje. Ma'aikatar magajin gari ta gusa mazauna unguwar don yin tsarin hilayen gini.

Loyalisme : Imani : riƙon amana, biyayya. Ya yi imani ga jam'iyyar siyasarshi.

Loyauté : Riƙon amana : gaskiya, biyayya. Magoya bayan jam'iyyarshi suna da riƙon amana.

Lucide : Mai hankali : mai duba abubuwa kan hankali, kan gaskiya mai kwanciyar hankali.

Lucratif : Na neman kuɗi : abun da ke kawo kuɗi, mai haifar da riba ƙungiyar da aka kafa don neman kuɗi.

Lutte : Yaƙi : kokowa (ƙokari) don shawo kan wata matsala ko cin ma wani guri. Ƙungiyar ma'aikata na matuƙar ƙokari don kare hakkin magoya bayanta.

Lutte de libération : yaƙin neman ɣancin : yaƙi don ɣanto wani ko wata al'umma daga mulkin mallaka.

Lutte de libération nationale : yaƙin neman ɣancin kan ƙasa : kokowa don kubuto ƙasa daga mulkin mallaka.

Luxe : Cikakken jin daɗi : rayuwa mai ɗauke da kashe-kashen maguɗan kuɗi don kyautata jin daɗi matuƙa. Rayuwa cikin cikakken jin daɗi.

Lycée : Lise.

M

Machiavélisme : Minahuci : halin mutunen da ke amfani da dulanci, da wayo, da yaudara, da zurhin ciki don biyan buƙatunshi. Nuna minahici.

Machine : Babban tsari : cikakken shiri mai sassa da yawa. Gudanar da babban tsarin ƙasa.

Magazine : Hili : shirin gidan radiyo ko na radiyo-mai-hoto bisa wani fanni. Hilin al'adu.

Magistrat : Juju : mai shari'a, mahukunci, ma'aikaci mai y'ancin yanke shari'a. Shugaban ƙasa ne babban juju na farko a cikin ƙasa.

Magistrat de siège : rukunin manyan jiyojin da ke tafiyar da shari'a.

Magistrat suprême : Babban jujun ƙasa : babban mahukunci na ƙasa.

Magistrats de parquet : rukunin jujoji masu neman aiki da doka da kare hakkin al'umma.

Mai : Mayu : wata na biyar cikin kalandiren kirista. Ma'aikata na duniya baki-ɗaya na gudanar da shagulgullan sallar ranar ɗaya ga watan mayu na kowace shekara.

Main d'oeuvre : Y'an ƙwadago, y'an aiki : dukan masu aikin ƙarfi cikin wata ma'aikata, wata masana'anta, wata jaha ko wata ƙasa. Iebarorin da suka ƙware.

Main-mise : Sanya hannu. Ya sanya hannunshi cikin harakar.

Maintenance : Gyara/Adani : tattali, dukan ayyukan kula da wani abu (inji, na'ura...) don ya ci gaba da aiki sosai. Sai da ya yi kiran masu gyara don injinan su tashi.

Maintien : Tabbaci : haƙiƙanci. Duk da matsalolin da ke akwai wajen shirye-shirye, gwamnati ta bayar da tabbacin gudanar da zaɓe a ranar 18 ga watan Juli 1999.

Maintien de l'ordre : aikin kwantar da tarzoma.

Maire : Magajin gari : mahukunci na farko na gari ko kwamin ; mai zartar da ayyukan kwamin. Magajin gari ya umurci masu shinfiɗa kaya bakin hanya da su tashi daga nan.

Maîtrise : Naƙalta : y'in ma, ƙwarewa, cin ƙarfi, gwaninta. Naƙaltar wani fanni.

Maîtrise de l'économie : Naƙaltar fannin tattalin arziki : Y'in ma fannin tattalin.

Maîtrise des charges : Naƙaltar harakokin kuɗi : ƙwarewa wajen duba shiga da fitar kuɗi.

Maîtriser : Cin ƙarhi : Cin ƙarfin wani abun da ba a iya tarewa,

ciwo kai, tsayar da. Sojojin kashe gobara sun ci ƙarhin gobarar.

Majeur : Mafi yawa : mahimmi, gagarumi, mafi daraja. Mafi yawan yan ƙasar Nijar jahilai ne.

Majoration : Ƙari : daɗi, hawa, habaka. Ƙarin kuɗi.

Majorité : 1.) Rinjaye : mafi yawan ƙuri'u. Samun rinjaye

2.) **Ɓangaren masu rinjaye :** jam'iyya ko haɗin kan jam'iyyun siyasa mafi yawan kujeru a majalisar dokoki. Ga mulki mai ruwa biyu, paraministan na ɓangaren masu rinjaye ne.

Majorité absolue : Cikakken rinjaye : rinjaye na hiye da rabin ƙuri'un da aka lissafa.

Majorité des deux tiers : Rinjayen kashi biyu cikin ukku : rinjaye mai ƙarfi ; rinjayen da doka ta so da dole sai ya zarce cikakken rinjaye wajen ƙuri'u.

Majorité requise : Dataccen rinjaye : daidai rinjayen da ake buƙata.

Majorité simple : Sahihin rinjaye : rinjaye kawai, rinjaye ko na ƙaƙa.

Mal : Lahani : abun da ke kawo jin ciwo, jin zafi, na baƙin ciki, da ba ya da kyau. Yin lahani.

Malaise : Rishin jin daɗi : rishin kwanciyar hankali, tashin hankali. Rishin jin daɗin jama'a.

Malentendu : Rishin fahimtar juna : rishin gane wa juna ; saɓani tsakanin mutanen da suka yi dubin sun gane wa juna. Wasu ayoyin doka na tsarin mulki sun kawo rishin fahimtar juna tsakanin yan siyasa.

Malversation : Handama : babban laifin cin kuɗi cikin gudanar da wani aiki. Handamar kuɗi.

Mandat : Wakilci : umurni, izini. Bai wa wani wakilci.

Mandat de détention : Umurnin tsayarwa : umurni na a ɗakatar da wani, a gabatar da shi gaban shari'a.

Mandat parlementaire : wakilci a majalisar dokoki : muƙamin ɗan majalisar dokoki.

Mandat impératif : wakilcin cika alkawali : wakilci wanda a cikin tafiyar da shi, tilas ne ga wanda aka zaɓa ya gabatar da tsarin da ya yi dalilin zaɓen nashi.

Mandat de dépôt : Umurnin ɗauri : umurnin ruhe wanda ake tuhuma.

Mandat d'arrêt : Umurnin kamu : umurnin da ake bai wa yan sanda na izo ƙeyar wani da ya gudu kuma su ɗaure shi a kurkuku.

Mandat d'amener : Umurnin durƙusar da : umurni na a gabatar da wani gaban juju.

Mandat de comparution : Umurnin amsa kira : umurnin

da juju ke bai wa wanda ake tuhuma na kawo kanshi gaban jujun a lokacin da aka kayyade cikin umurnin.

Mandataire : Wakili/wakiltacce : wanda aka bai wa wani izini. A lokacin zaman shawarwari tsakanin yan adawa da gwamnati, wakilin bangaren adawa ya yi watsi gaba d'aya da dukan shawarwarin bangaren gwamnati.

Manifestation : Zanga-zanga/Tarzoma : Taron jama'a ga hili don bayyana ra'ayinta ko neman wani hakkinta. Halartar zanga-zangar tuna wani abu.

Manifestation pacifique : Zanga-zanga/Tarzoma cikin lumana : zanga-zanga cikin kwanciyar hankali, ba tare da aika-aika ba.

Manifeste : Kundin tsare-tsare : sanarwa a rubuce inda gwamnati, ko wani babban mutum, ko wata jam'iyyar siyasa ke bayyana tsare- tsarenshi, ko hujjar matakan da ya d'auka. Wallafa kundin tsare-tsare.

Manoeuvre : Dubaru : hanyoyi, dukan husa'o'in da ake amfani da su don cin ma wani guri, galibi a munahuce. Dubarun gwamnati na kawo sabani tsakanin yan adawa.

Manquement : Sabani : halin saba wa doka ko wata ka'ida. Babban sabani.

Manufacturer : Sarrafawa, Kerawa : aikin da ake yi wa wani abu a masana'anta. Kayan da aka sarrafa.

Marginal : Na ware : na kauye guda, bare, wanda ba ya cikin jama'a sosai kuma ba ya kalkashin ka'idodinta. Mutunen ware.

Marginalisation : Wariya : Kauyacewa, maidawa kauye. Albarkacin kebabbiyar ranar mata ta duniya baki d'aya, mata sun nuna rishin jin dad'insu a game da wariyar da suke huskanta.

Mars : Maris : Wata na uku ga karandiren kirista. An haihe shi cikin watan Maris.

Marxisme : Ra'ayin gurguzu : ra'ayi ne da karl MARKIS ya yad'a a fannin falsafa, da zaman al'umma da tattalin arziki. Dan ra'ayin gurguzu.

Marxiste : Dan ra'ayin gurguzu : mai goyon bayan (mai bin) ra'ayin Markis. Rikakken d'an ra'ayin gurguzu.

Mass-média : Kahohin watsa labaru : hanyoyin bayar da labaru, na yad'a labaru. (radiyo, radiyo-mai-hoto, jaridu d.s) kuma hanyoyin ne na bayar da ra'ayi da isar da wani sako wajen jama'a. Kahohin watsa labaru suna taimakawa wajen bunkasa al'adu.

Masse : Al'umma : mutanen da ke yin rukuni (gungu) guda,

rukunin wasu mutane. Al'ummar talakkawa.

Masse populaire : Al'umma : jama'a. Masse rurale : Al'ummar yan karkara : dukan mazauna karkara.

Match : Gasa : Kombala tsakanin mutum biyu ko hiye. Gasar kwallon kafa.

Matérialiser : Tabbatar da : aikatawa, cika wani nufi. Tabbatar da wata niyya

Matérialisme : Son abun duniya : neman jin dadi da kadara. Yau kowa dan son abun duniya ne.

Matériel : Kayan aiki : dukan abubuwa da ake amfani da su a ma'aikata. An hana yin amfani da kayan aiki na gwamnati in ba lokacin aiki ba ne.

Matériel didactique : kayan karantarwa : littattafan.

Maternité : Gidan haihuwa : matsayin uwa. Gidan likita inda mata ke haihuwa. Haihuwa ba tare da matsala ba.

Matière pénale : Fannin hukunce-hukunce : abun da ya shafi laififfika da hukuncinsu. A fannin hukunce-hukunce, laifin fasa-kwabri yana da hukunci mai tsanani.

Matriarcat : Mulkin mata : tsari a fannin shari'a ko na zaman rayuwar wata al'umma inda mace ke iko, ke da matsayin maigida, inda mace ke rinjayar komi. Zama a kalkashin mulkin mata.

Matricule : Girgam : Kundi inda ake jera sunayen mutane na wata al'umma ko na cikin wata ma'aikata tare da sa wa kowane suna limaro bi-da-bi. Samun limaron girgam na ma'aikatan gwamnati.

Matrimonial : Na fannin aure : mai alaka da aure, da ya shafi aure, da ya danganta da aure. Danganta daga aure.

Régime matrimonial : tsari inda ake kayyade mallaka da tattalin dukiya tsakanin ma'aurata.

Matrône : Ungozuma : tsofuwar (lattijuwar) mace mai taimaka wa mata wajen haihuwa, mafi yawa a cikin kauyuka. Ungazuma ta hana ta cin gishiri.

Maturité : Isasshen hankali : Halin wanda ya kai mutumen kansa, da ya cin ma dattako.

Maturité politique : Isasshen hankali na siyasa : rikakken dan siyasa, wanda ke da cikakken tsinkaye a siyasa.

Mauvais : Mummuna : maras kyau, mugu. Mummunan hali. Mugun hali

Maximum : Matuka : iyaka, baki. Ya yi matukar kasada.

Mécanisme : Hanyoyin tafiyar da : yadda abu ke aiki. Hanyoyin tafiyar da aikin ma'aikata.

Méconnaissance : Rishin sani : jahilci, rishin fahinta. Rishin sanin wani hakki

Mécontentement : Ɓacin rai : rishin jin daɗi, kuka. Kawo ɓacin ran kowa da kowa.

Médaille : Gala : lambar cin nasara, lambar girma. Wani ya ci gala.

Médecine : Ilimin aikin likita : ilimin kiyaye lafiya. Shekara bakwai ne ɗalibai ke yi a jami'a don koyon ilimin aikin likita

Médiateur : Mai shiga tsakani : mutunen da ke kawo ƙokarinshi don sasanta mutum biyu ko hiye, ko wasu ɓangarori. Mai shiga tsakanin ƙasashe.

Médiation : Shiga tsakani : kawo sulhu, sassauci, yarjejeniya tsakanin mutane ko wasu ɓangarori. Gwamnatin Nijar ta sa hannu kan wata yarjejeniyar zaman lafiya da ɣan tawaye bayan shiga tsakanin wasu ƙasashen ƙetare.

Médiatique : Sananne ta kahohin labaru : abun da kahohin labaru suka yaɗa sosai, suka sa aka sani sosai. Sanannen wasa ta kahohin labaru.

Médiatiser : Yaɗawa / sanarwa ta kahohin labaru : watsawa ta kahohin labaru. Kahohin labaru sun yaɗa yaƙin taikun pasha sosai.

Médiocre : Ba wadatacce ba : abun da ba isasshe ba, ƙarantacce ƙanƙane. Ya samu sakamakon da ba wadatacce ba ga jarabawa.

Médisance : Muzantawa : Ɓata suna, tsegumi, cin nama, gulma. Muzanta wani abokin hamayyar siyasa.

Meeting : Taron gangami : haɗuwar da ake shiryawa a hili don tantaunawa kan wasu abubuwa da suka shafi jama'a ko kan wani al'amarin siyasa.

Meeting populaire : Babban taron gangami : haɗuwar mahawara a hili inda ake gayyatar dukan ɣan jam'iyyar siyasa, ko na wata ƙungiya.

Méfait : laifi : mugunta, cuta, mai kawo wa wani ko ƙasa matsala. Ya kamata a waye wa matasa kai a game da laifin shan ƙwaya.

Méfiance : Kin yarda : Kin amincewa, zargi. Akwai ƙin yarda tsakanin magoya bayan shugaban ƙasa da ɣan adawa.

Mégarde : Ba da gangan ba : ba da sani ba, ba da so ba. Aikata laifi ba da gangan ba.

Membre : Mamba : mutumen da ke cikin wata ƙungiya ko wani tsari. mamba na buron wata jam'iyyar siyasa.

Membres du gouvernement : Mambobin gwamnati : dukan manyan mutanen da gwamnati ta ƙumsa.

Mémoire : 1.) Rubuce-rubucen da ake yi don a bayyana, don a tallafa wa wani. gabatar da rubuce-rubuce.

2.) **Tunani** : waiwayowa da abun da ya shuɗe, rishin mance abu ; riƙe abu cikin ƙwaƙwalwa. Har yanzu ɗalibai suna tunanin hatsarin da ya faru a ranar 9 ga watan Faburari 1990 a jami'arsu.

Mémorable : Wanda ba ya mantuwa : abun tunawa, na tarihi. Ranar juyin mulki ta 15 ga watan Apirilu, rana ce wadda ba ta mantuwa a Nijar.

Mémorandum : Kundin "koke-koke" : takkardar da ake gabatar wa hukuma ko wata ma'aikata da ita wanda ta ƙumshi shawarwari dangane da wani zance da ake tantaunawa a kai. A albarkar sallar ranar 1 ga watan Mayu, ƙungiyar ma'aikata ta gabatar wa Ministan ma'aikata da kundin "koke-kokenta".

Mémoriale : Kundin abun tunawa : Kundin abubuwan da ba su mantuwa. Abun tarihi. Ya je ya binciki kundin abubuwan tunawa na siyasa a ƙasar Nijar a gidan adanon mahujjatai.

Menace : 1.) **Ban tsoro** : maganganu ko zabure-zabure masu nuna niyyar yin mugunta, masu nuna ɓacin ran wani.

2.) **Alamar haɗari** : abun da ke nuna abkuwar wani haɗari ; y'an makaranta suna cikin bakin ciki don ganin alamar ɓadda shekarar wajen karatu.

Ménacer : Bayar da tsoro : yi ikirari : yi wa barazana, yi wa burga, razanawa. Ƙungiyoyin ƙwadago na barazanar tsunduma cikin yajin aiki.

Ménager : Yi tsimi : amfana da wani abu tare da tattala shi. Gwamnati ba ta yi tsimin komi ba wajen kawo taimako ga iyallan da ke cikin matsaloli.

Mendicité : Bara : neman taimako, tara hannu. Bara ta ƙasaita a birnin yamai.

Meneur : Shugaba : jagora, madugu, mutanen da ke shiga gaban wani tsari ko wata zanga-zanga. Y'an sanda suna neman shugabannin y'an yajin aiki.

Mentalité : Hali : dukan abubuwan da ke shaidar wata al'umma (tabi'u, addini, aƙida...) Sauya hali.

Mercenaire : Sojin haya : wanda ake biya don ya aikata wani abu. Ɗaukar sojawan haya.

Mérite : Yabo : abun girmama mutum, abun da ya kamaci mutum. Samun ci gaba don yabon da aka samu.

Mésentente : Sabani : rishin jittuwa, rishin fahimta, taƙaddama kauce wa sabani.

Message : 1.) **Saƙo** : sanarwa,

labari da ake kai wa wani. Aika saƙon barka.

2.) **Jawabi** : sanarwa, kalami a bayyane zuwa ga wata majalisa, wani taro. Sauraren jawabin shugaban ƙasa.

Mesure : Mataki : hanyar cin ma wani sakamako. Ɗaukar matakai masu baƙin jini. (masu ƙuntata wa jama'a)

Mesure exceptionnelle : Mataki na masamman.

Mesure économique : Matakin tattalin arziki : matakin da ke sa a rage ɓannar kuɗi.

Mesure d'accompagnement : Matakin sanyayawa : matakin da ke biyo bayan wani don sauƙaƙa wani abu.

Mesure de grâce : Matakin alfurma : matakin da gwamnati ke ɗauka don yi wa wanda aka ɗaure ahuwa (gafara).

Méthode : Dubara : dukan hanyoyin da ake ɗauka don cin ma wani guri, hanya, husa'a. Sake dubara.

Métier : Aiki : sana'a ; abun da mutum yake yi mai ciyar da shi. Yin aikin jarida.

Mettre : Sanyawa : bayarwa, ajewa, kaiwa cikin wani hali, ga wani matsayi. Bai wa mutum hakkinshi.

Mettre fin : Sanya aya : dakatar da, tsayar da.

Mettre sur pieds : kafawa : girkawa, ƙirƙirawa.

Meurtre rituel : Kishin kan tsafi : fitar da ran mutum don tsafi. Kowace shekara, ana yawan kishi kan tsafi cikin wasu al'ummomi na ƙasashen Afirika.

Mieux être : Jin daɗin rayuwa : Kyautatacciyar (ingantacciyar) rayuwar mutum ko al'umma baki ɗaya. Ya kyautu gwamnati ta mayar da hankali wajen tabbatar da jin daɗin rayuwar al'umma.

Migration : Ƙaura : gushi, tashin al'ummar wata ƙasa zuwa wata ƙasa a dalilin matsalar tattalin arziki ko ta siyasa. Yunwa ta kawo ƙaurar ɗimbin mutanen karkara zuwa manyan birane.

Milice : Ƴan banga : Sojojin gida da ba na kan ƙa'ida ba waɗanda wata al'umma ko wata jam'iyyar siyasa ke ɗauka don tsaronta.

Militant : Magoyin baya : mutunen da ke cikin wata jam'iyyar siyasa, ko wata ƙungiyar ƙwadago kuma yana kawo ƙokarinshi don rayuwarta. magoyin bayan wata jam'iyyar siyasa.

Militants de droits de l'homme : Magoyin bayan hakkin ɗan Adam : wanda ke cikin wani tsari mai kokowar samar wa kowa ɣ ancinshi.

Militer : Goya baya : shiga cikin wata jam'iyyar siyasa, ko wata

ƙungiyar ƙwadago, ko wani tsari tare da kawo ƙoƙari don ci-gabansu. Goya baya ga wata jam'iyyar siyasa.

Mine : 1.) **Huska** : alama, kama. huskar jin dadi. Sakin huska.

2.) **Nakiya** : abun da ke ƙashewa, da ke tashi tare da walwatsewa da ƙara kamar bam, a bilbishi ko ƙalƙashin ƙasa ko cikin ruwa. Nakiya ta tashi da wani mutum.

Minerai : **Arzikin ƙalƙashin ƙasa** : ma'adinai inda ake iya haƙar wasu albarkatun ƙasa. Arzikin lu'ulu'u.

Minimum : **Mafi kaɗanci** : a ƙalla, kima. Samun abun rayuwa mafi kaɗanci.

Ministère : **Ma'aikatar minista**: dukan sassan hukumar da minista ke shugabanci.

Ministère de l'éducation nationale : **Ma'aikatar ministan ilimi da horo** : duka sassan ma'aikatar masu kula da tsari, da tattali, da lura, da gudanar da ayyukan makarantun boko na gwamnati da masu zaman kansu.

Ministre : **Minista** : mamba na gwamnati mai shugabancin ma'aikatar minista. Ministan noma ya tafi rangadin ganin halin damana a cikin faɗin ƙasar.

Minorité : **Maras yawa tsirarre**: Karamin gungun mutane masu bambanta da saura a majalisa, ko wata jam'iyya. kare yancin tsirarrar ƙabila (kare yancin ƙabila maras yawa).

Mirage : **Kawalneniya** : kamannu masu sa kuskure, masu bidawa, shucin gizo. Kawalneniya ta ɗauke shi.

Mise en examen : **Tsaro don bincike** : tsare mutum don bincikar gaskiya a kanshi. Wa'adin tsaron bincike ba ya wuce kwana biyu.

Mise en oeuvre : **Tabbatawa**: haƙiƙantawa, aikatawa. Tabbatar da wani guri.

Misère : **Tsananin rishi** : tsiya, tsananin talauci. Ma'aikata sun ɗauki niyyar dakatar da aiki saboda tsananin rishin da suke huskanta.

Mission : **Aiki** : nauyin da aka ɗora wa wani na aikata wani abu. Cika aiki.

Mixte : **Mai garwaye** : abun da ya haɗa abubuwan da ba iri ɗaya ba. makaranta mai garwayen y an maza da y an mata.

Mobilisation : **Tashi tsaye** : tattara, yunƙurin mutane ga yin wani aikin taro. Kungiyar ma'aikata ta yi kira ga magoya bayanta da su tashi tsaye don kare hakkinsu.

Mobilisation de financement : **Tattarar kuɗi** ; neman kuɗin aikata wani abun amfani.

Mobilisation des ressources internes : **Tattarar arzikin ƙasa** : gangamo kuɗin da ƙasa ke samu.

Modalité : Ka'ida : hanya, yadda wani abu yake ciki, yake gudana. A taron gangami an bayyana wa mutane ƙa'idodin zaɓe.

Modalités de recouvrement : ƙa'idodin gangamo kuɗi : hanyoyin tattaro kuɗin da ake bi bashi.

Mode de désignation : Hanyar zaɓe : irin yadda ake zaɓen mutum a wani muƙami

Modèle : Abun koyi : abun kwaikwayo, abun da ake ɗauƙar samfurinshi. An yi koyi da tsarin mulkin Faranshi wajen wallafa tsarin mulkin Nijar.

Modèle endogène : Abun koyi na ainahi : abun kwaikwayo wanda bai ɗauko wani samfuri ba.

Modération : Kima : rishin zaƙewa, sassauci. Gwamnati ta yi kira ga ƙungiyoyin ƙwadago da su sa kima cikin koke-koken da suke gabatar.

Moderne : Na zamani : sabon fitowa, na yayi, na yau. Rawar zamani.

Modernisation : Mayarwa na zamani : sauyawa, mayarwa na yayi, na yau. mayar da kayan aiki na zamani, shi ya bunƙasa noma a Amerika.

Modeste : Maras zaƙewa : mai dama-dama, madaidaici. Mutum maras zaƙewa

Modification : kwaskwarima ; gyare-gyare : gyare-gyaren da aka kawo wa doka.

Modification radicale : Cikakken sauyi : sauyi na gaba-ɗaya.

Moeurs : Aƙida : halayya, ɗabi'u na wata al'umma ko na wani mutum. Aƙidar ƙwarai.

Monarchie : Mulukiya : tsarin mulki inda mai sarautar (sarki) shi ne shugaban ƙasa. Mulukiya ta ƙin ƙarawa.

Monde : Duniya : dukan ababuwan da ke bisa doron ƙasa da na samaniya da ake gani ; muhallin halittu. Rayuwa cikin duniya mai kwanciyar hankali.

Monopole : Babakere : Cikakken gatanci da doka ko wani hali ke damƙa wa wani mutum, ko wani kampani ko wata ƙungiya. Kampani SONIDEP ne ya yi babakeren shigowar man petir a Nijar.

Monopoliser : Yin babakere: kankanewa, kakkacewa. Yin babakere ga magana.

Moralité : Aƙida : halayya, ɗabi'a. Samun aƙidar ƙwarai.

Morbidité : Yawan maras lahiya : mizanin adadin maras lahiya dangane da yawan al'umma. Mizanta yawan waɗanda wata cuta ta kama.

Mortalité : Yawan mace-mace : mizani na adadin waɗanda suka mutu a wani wuri kuma cikin ƙayyadadden lokaci dangane da yawan al'umma.

Mizanin yawan mace-mace ya hambare sosai.

Motif : Dalili : mafari, sanadi, hujja. Babu wani dalili sai ya fita daga wurin tataunawar da gaggawa.

Motion : Shawara : ra'ayin da wani ɗan wata majalisa ke gabatarwa. An kawo shawarar isar da godiya ga dukan mahalarta taron.

Motion d'information : Shawarar kawo labari : maganar da mutum ke tambaya a wani taro don ya kawo wani labari sabo.

Motion d'ordre. Shawarar kawo tsari : maganar da mutum ke tambaya don ya ce wa shugaban taron da ya yi la'akari da wasu fannoni kuma ya sanya tsari cikin tafiyar da ayyukan.

Motion de censure : shawarar saukar da : ikon da tsarin mulki ya bai wa majalisar dokoki wanda ke ba ta damar tsige (sauke) gwamnati.

Saukewar gwamnati ta biyo bayan shawarar saukar da ita da majalisar dokoki ta yanke.

Motion de procédure : shawarar sa hanya : maganar da mutum ke tambaya don shawarta yadda ayyukan majalisa za su gudana.

Motivation : Dalili : mafari, dukan hujjojin aikata abu. Kwararren dalili

Mouvement : Kungiya/tsari : Haɗin kai don neman wani sauyin ra'ayi, don cin ma wani guri.

Mouvement révolutionnaire : Kungiyar neman sauyi, ta juya-hali.

Mouvement coopératif : Kungiyar haɗin gwiwa : kungiya inda duk wanda ke cikin ta yake kawo irin nashi ƙoƙari ga ayyukan.

Mouvement national pour la société de développement : Babban tsarin ci-gaban ƙasa: haɗin kan dukan y'an ƙasa cikin tsari guda don ci-gaban al'umma.

Mouvement politique : Tsari na siyasa : Kungiyar (jam'iyyar) siyasa mai gurin samun mulki (iko).

Mouvement syndical : Kungiyar ƙwadago : Kungiyar ma'aikata mai gurin kare hakkin magoya bayanta.

Moyen : Hali : Hanyar cin ma wani guri, dama. Samun isasshen hali.

Moyen terme : Madaidaicin wa'adi : wa'adi mai dama-dama, matsakaicin wa'adin.

Multipartisme : Siyasa mai tay rin jam'iyyu : tsarin siyasa wanda ya haɗa jam'iyyu da yawa.

Municipalité : Hukumar birni: Cibiyar hukumar birni. Hukumar

birni ke da nauyin karɓar asangam.

Mutation : Tashi (tashe-tashe) : tadawa, sauyi, canji. Kungiyar malaman makaranta ta yi ƙorahi a game da tashe-tashe na ba mafari da aka yi wa magoya bayanta.

Mutation sociale : canje-canje cikin rayuwar al'umma.

Mutilation : Nakasa : lahanta, raunanawa, fitar da wani sashe na jiki. Kungiyoyin kare hakkin ɗan Adam sun yi watsi da muguwar tabi'ar nan ta nakasar da halittar ɗan mata wajen yin kungulum.

Mutualiste : Na taimakon juna : abun da ya shafi cuɗayyar juna. tsarin da ke buɗe wa mambobinshi hanyoyin tanadi da cuɗayyar juna. Kungiyar taimakon juna.

Mutualité : Tanadi na taimakon juna : ajiya da wasu mutane ke yi wuri guda don taimakon juna a game da wasu haɗarorin da ke iya aukuwa. Ɗan ƙasashen waje da ke zaune a Nijar sun yi tsarin kanadin taimakon juna.

Mutualité autoritaire : Tanadin dole na taimakon juna : tsarin ajiya da aka tilasa wa wata al'umma da ta kafa shi.

Mutuelle : Asusun taimakon juna : asusu na cuɗayyar juna tsakanin wasu mutane. Asusun bada bashi.

Mutuellement : Tare da taimakon juna : tare da masanya tsakanin juna, zuwa da zauwa.

N

Natalité : Yawan haihuwa : adadin haihuwar da ake samu cikin wani ƙayyadadden lokaci dangane da yawan wata al'umma. Mizanin yawan haihuwa ya hamɓare sosai a Nijar.

Nation : Ƙasa : Al'umma da ke zaune a ƙayyadadden wuri kuma masu zaman kansu. Ƙasar Nijar.

Nation équilibrée : Ƙasar kwanciyar hankali : ƙasar da ba ta huskantar matsaloli, ko a fannin siyasa, ko na tattalin arziki, ko ma na zaman al'umma.

Nation solidaire : ƙasar haɗin kai : ƙasa inda ke da zumunta sosai tsakanin y'an ƙasar.

National : Na ƙasa : mallakar ƙasa, wanda ya shafi ƙasa baki-ɗaya. Dipite na ƙasa.

Nationaliser : Mayarwa na ƙasa : sawa a hannun gwamnatin ƙasa, a misali wasu masana'antu ko kampani masu zaman kansu. mayar da wani kampani na ƙasa.

Nationalisme : Kishin ƙasa : fifita amfanin ƙasa bisan duk wani amfanin da mutum shi kaɗai ko gungum mutane kan iya samu. Nuna kishin ƙasa.

Nationaliste : Mai kishin ƙasa : mutumen da ke ƙaunar ƙasarshi ƙwarai da gaske. Shugaba mai kishin ƙasa.

Nations unies : Majalisar ɗinkin duniya : tsari wanda ya haɗa ƙasashen duniya ƙasar Nijar tana cikin mambobin majalisar ɗinkin duniya.

Nature : Halaye : dukan abubuwan (alamomin) da suka zame wa wata halitta jiki, ko wani abu, da ke rataye da su ; ainahi ; takamaimai.

La nature humaine : Mutuntaka.

Nature des droits : abubuwan da dokoki ke ɗauke (tahe) da su, sharuɗɗan da ke ƙayyade dokoki.

Nature des libertés : sharuɗɗan da ke ƙayyade y'anci.

Néfaste/nocif : Gaibu : mugu, mai lahani, mai kawo cikas, mai kawo matsala. Y'ajin aiki gaibu ne ga tattalin arzikin ƙasa.

Négoce : Sari : babban kasuwanci, ta'ammala. Y'in sari

Négociant : Ɗan sari : mutunen da ke yin sari.

Négociation : Tattaunawa : shawarwari tsakanin wasu mutane ko ɓangarori masu huldɗa da juna don cin ma yarjejeniya kan wasu matsaloli. Samun tattaunawa.

Négocier : Tattaunawa : gudanar ta shawarwari don cin ma wata yarjejeniya. Tattaunawar cin ma yarjejeniyar zaman haliya.

Néocolonialisme : sabon salo na mulkin mallaka : sabin dubarun da ƙasashe masu arziki ke amfani da su don sake mallakar ƙasashe masu tasowa ta wata hanya bayan sun samu ƴancin kansu. Tashi tsaye don yin kakkau da sabon salon mulkin mallaka.

Népotisme : Halin daga-ni-sai-na-gida : amfani da mutum ke yi da ikon da ke gare shi don cin moriyar tare da ƴan uwanshi da aminnanshi kawai. Doka ta haramta halin daga-ni-sai-na-gida a Nijar.

Neutralité : Tsaka-tsakanci : rishin son rai, halin ba-ruwana, ƙauracewa. Nuna tsaka-tsakanci a fannin siyasa.

Niger nouveau : Nijar sabuwa : Nijar ta haɗin kai, Nijar mai ci gaba. Ya kamata dukan ƴan ƙasa su kawo ƙokarinsu don gina Nijar sabuwa.

Niveau : Matsayi : hali, hawa, aji, tsawo. Ajin makaranta.

Niveau de vie : Halin rayuwar : gwalgwadon irin abubuwan tafiyar da rayuwa, sakamakon aikin mutum, ko na wata ƙasa.

Noeud : Cibiya : inda mahimmancin wani zance yake, inda matsalar take. Sannin cibiyar wata matsala.

Nomade : Makiyayi : wanda ba ya da mazauni ɗaya, kuma kiwo ne aikinshi. Rayuwar makiyayi.

Nomadisme : Zaman kiwo : fita daga wuri zuwa wuri, irin rayuwar makiyayi, rishin zama wuri ɗaya, yawan gushe-gushe. A Nijar, rayuwar wasu ta zaman kiwo ce.

Nomadisme parlementaire : Halin da ɗan majalisa ke fita daga gungun siyasarshi zuwa wani a majalisar dokoki.

Nombre : Yawa : adadi, jimilla (mutane ko wasu abubuwa). Ƴan kallo masu yawa sosai sun shigo hilin wasan ƙwallon ƙafa

Nomination : Naɗi : miƙa wa mutum wani aiki, ɗorawa kan wani matsayi. Naɗin wani darakta.

Nommer : Naɗawa : tsayar da. An naɗa shi (tsayar da) shugaban ma'aikata.

Non-alignement : Halin ba-ruwanmu : ra'ayin ƙasashe masu tasowa na ƙin goyon bayan ɓangare ko guda tsakanin ƙasashen yankin gabas da na yamma a lokacin da suke ja-in-ja da juna. Halin ba-ruwanmu na ƙasashen Afirika.

Nord-sud : Arewa da kudu : hulɗa tsakanin ƙasashe masu arzikin masana'antu da ƙasashe masu tasowa. Hulɗa tsakanin arewa da kudu

Normalisation : Daidaitawa : gyara, mayarwa yadda ya kamata. Daidaitawar hulɗar jakadanci tsakanin ƙasashe biyu.

Normes internationales : Ka'idodi na ƙasashe da ƙasashe : matakan da suka shafi ƙasashe. Wajibi ne kowace ƙasa ta girmama ƙa'idodi na ƙasashe da ƙasashe.

Notable : Mai faɗi a ji : babban mutum, mai daraja. Ɗan wani mai faɗi a ji.

Notification : Sanarwa : faɗi (gayi), faɗakarwa. An ba shi sanarwar yanke yarjejeniyar.

Notifier : Sanar da : shaida wa mutum ta hanyar ƙa'ida. An sanar da mai laifin hukuncin da koti ya yanke.

Nouvelle : Sabon labari : labarin da ya zo da ɗumi-ɗuminshi. Bayar da sabon labari.

Novateur : Wanda ya fara : wanda ya ƙirƙiro, da ya kafa, ya fito da sabon abu. Shi ne ya kafa wurin koyon kaɗe-kaɗen zamani.

Novembre : Nobamba : Wata ma goma sha ɗaya na kalandiren kirista.

O

O.N.U. : Majalisar ɗinkin duniya : Kungiya ta duniya wadda aka kafa a shekarar 1945, kuma ƙasashen da suka rattaba hannun sun ɗauki niyyar tabbatar da zaman lahiya da kwanciyar hankali cikin duniya, kuma haɗa hulɗa a fannin tattalin arziki, da zaman al'umma da al'adu tsakanin ƙasashe. Kwamitin sulhu na majalisar ne ke zartar da ayyukan. A birnin Nuyork ne cibiyar majalisar take.

O.U.A. : Kungiyar haɗin kan Afirika : Kungiyar da ƙasashen Afirika suka kafa (banda Afrika ta kudu da Zimbabuwe) a zaman taron babbar mahawara ta shekarar 1963 a babban birnin Adis-Ababa na ƙasar Habasha. Gurinta shi ne ƙarfafa dankon zumunci tsakanin ƙasashen Afirika ta hanyar hulɗar tattalin arziki da yaɗa al'adu.

Objectif : Guri : maƙasudi, manufa, abun da ake so a cin ma. Gurin duk wata jam'iyyar siyasa na ta samu iko ne.

Objection : Rishin amincewa : ra'ayin da bai goyi bayan wani ba, suka. Gabatar da rishin amincewa.

Obligation : Wajibi/nauyi : dole, alhaki, farilla, tilas. Ka'idodin zaɓe sun nuna cewa wajibi ne ga sarakunan gargajiya su kama bakinsu a lokacin zaɓe.

Obligation civile : Wajibi ga ɗan ƙasa : nauyin da ya rataya wuyan ɗan ƙasa.

Obligation civique : Wajibi daga doka : abun da doka ta tilasa wa ɗan ƙasa.

Obligation professionnelle : Wajibi daga aiki : nauyin da aikin mutum ya ɗora mashi.

Obligation de résultats : Nauyin samun sakamako : cin nasara dole, gabatar da sakamako dole.

Obliger : Wajaba wa : tilasta wa, sawa dole. Tilasta/wajaba wa wani da ya yi murabus daga aikinshi.

Observateur : Mai zura ido : wanda yake yin lura da abun da ke faruwa don yin rahoto

Obstacle : Cikas : abun da ke hana gudanar abu, da ke kare abu. An samu cikas iri-iri cikin tafiyar da harakokin.

Obstination : Himma : Naci, dagewa, daurewa, jimiri, taurin rai. Mayar da himma ga aiki.

Occasion : Albarkaci : dalilin wani abu. An shirya rawar zamani a albarkacin sallar sabuwar shekara.

Occasionner : Haddasa : jawowa, sawa, yi sanadi. Ambaliyar ruwa ta haddasa asarar dukiya mai yawa.

Occident : Yammaci : Kasashen yammacin turai.

Occidental : Na yammaci : abun da yake a yammaci,, da ya shafi yammanci. Akidar kasashen yammacin turai.

Occupation : Kasahi : shagala, abun yi. Bayan taro ya kare, kowa ya tafi kasahinshi.

Occuper : yi/samu/mama-yewa. Samun wani aiki na gabata.

Octroi : Taimako : gudunmuwa. Taimakon alawus

Octroyer : Taimakawa : bayar da gudunmuwa. Taimakawa da bashi.

Office : Ma'aikata : ma'aikata mai cin gashin kanta wajen harakar kud'i. Ma'aikatar tana huskantar matsalolin kud'i.

Officialisation : Tabbatawa : bayyanawa. Kotin koli na shari'a ke tabbata sakamakon zabe.

Officialiser : Tabbatar da : bayar da tabbaci, bayyana wa jama'a. Minista ya tabbatar da ranar jarrabawa ta karshen shekara

Officiel : Na hukuma/Na aiki : abun da ya fito daga hukuma kuma a bayyane. Faransanci ne harshen aiki a Nijar.

Officiers généraux : Manyan hafsoshin soja : hafsoshin sojan kasa da na sojan lema masu jan ragamar wata bataliya, ko wata runduna.

Officieux : Maras tabbaci : abun da ya fito daga wata hukuma, amma ba bayyananne ba. Sakamakon zabe maras tabbaci.

Oligarchie : Mulkin wariya : mulki inda duk wani iko yana hannun wani iyali ko wasu mutane kalilan.

Omettre : Mancewa : yi sakaci, ki kula. Ya mance da ya sa hannu.

Omission : Mantuwa : Shagala, sakaci, rishin kula. Mantuwar sunayen wasu bisa jeran sunayen yan zabe.

Onde : Radiyo : radiyo mai watsa labaru. Jam'iyyun siyasa suna neman a daidaita samun magana cikin radiyo.

Opérateur : Mai tafiyar da : mutunen da ke kula da sa wata mashin aiki, mai tafiyar da wani aiki. Mai sa radiyo aiki.

Opérateur économique : Dan kasuwa : d'an kwangila.

Opération : Aiki/hanya : dukan ayyukan da ake yi don kaiwa ga wani abu. An gudanar da ayyukan zabe cikin kwanciyar hankali.

Opérations de privatisation : Ayyukan yaye kampanoni : hanyoyin da gwamnati ke d'auka don sayar da kamapanoninta.

Opérations de dépouille-ment : Ayyukan kidaya : (ayyukan) kilgon kuri'u.

Opération de vote : opération électorale : ayyukan zaɓe : ayyukan gudanar da zaɓe.

Opérationnel : Mai aikatuwa : wanda ake iya amfani (aiki) da shi. Kayan zaɓen masu aikatuwa ne.

Opérer : Yi : aikatawa. Sun yi zaɓe na ƙwarai.

Opinion : Ra'ayi : yadda (abun da) mutum ya gani, yabon mutum bisa wani abu. Bayar da ra'ayinsa.

Opinion publique : Ra'ayin jama'a : yadda jama'a ta gani ko ta yaba wani abu.

Opinion internationale : Ra'ayin al'ummomin ƙasashe : dukan al'ummomi na duniya masu saurare.

Opinion politique : Ra'ayin siyasa : imanin da mutum ya yi a siyasa.

Opinion syndicale. Ra'ayin fannin sandika : imanin da mutum ya yi a sha'anin sandika.

Opportunité : Dama : hali. Samun dama.

Opposant : Ɗan adawa : wanda ke ƙin amincewa da wani mataki, wani hukunci, ko da hukuma. Mai hamayya. An tilasta wa yan adawa a cikin mulkin kama karya da su yi gudun hijira.

Opposer : Saɓawa : yi adawa, yi ƙiyayya, yi hamayya. Shawarar rage ma'aikata ta sa ƙungiyar ma'aikata saɓawa da gwamnati.

Opposition : Adawa/hamayya : Gungun adawa. Gungun (ɓangaren) adawa ya yi Allah waddai da wariyar da magoya bayanshi ke huskanta cikin ma'aikatu.

Opposition parlementaire : Dipitocin ɓangaren adawa : yan majalisar dokoki na jam'iyyun siyasa masu adawa da gwamnati.

Opposition armée : yan tawaye : gungun wasu mutane ko jam'iyyun siyasa masu adawa da gwamnati tare da yin amfani da makamai.

Opposition extra-parlementaire : gungun jam'iyyun siyasa masu adawa waɗanda ba su da dipitoci a majalisa.

Oppresser : Dannewa : taushewa, zalunta. Duƙar da al'umma ƙalƙashin iko mai tsanani, na rishin adalci kuma mai muggunawa. Mulkin kama-karya ya danne al'umma cikin shekara da shekaru.

Oppresion : Danniya : tausa, matsi, zalunci, muzgunawa. Danniyar da aka riƙa wa al'umma, ta kawo tawaye daga wajenta.

Opter : Zaɓa : Gwammacewa, yin zaɓe cikin abubuwa da yawa. Tsarin mulki mai ruwa biyu ne kwamitin shawara ya zaɓa.

Optimisation : Kyautatawar zato (hali) : ƙarfafawar halin samun abu. Kyautatawar zaton cin nasara

Optimitiser : **Kyautata (ƙara), zato (hali)** : ƙarfafa halin yi ko samun abu. Ƙara ƙarfi.

Optimisme : **Kyakkyawan fata** : rishin sarau, sa rai, fata na gari, zato mai kyau. Riƙe kyakkyawan fata game da wani abu.

Optimiste : **Mai kyakkyawan fata** (zato) : maras saura, mai fata na gari. kasancewa mai kyaukkyawan fata har kullum.

Option : **Zaɓi** (zaɓe)/**Ra'ayi** : Fitarshi daga jam'iyyarshi ta nuna sauya ra'ayinshi.

Orange : **Launin ruwan goro** : mai launin ɗorowa ma so ja. Yana ƙamnar launin ruwan goro.

Orateur : **Mai baki** : mutunen da ya iya magana gaban jama'a, mai kaudin bakin, mai fasaha a magana,

Ordonnance : **Kudiri** : dokokin da suka fito daga hukumar zartawa. Shugaban jamhuriya ya sa hannu kan wani ƙudiri na bai wa y'an ƙasashen waje da ke Nijar, matsayin y'an ƙasa.

Ordonnancement : 1.) **Shiri daki-daki** : tsari mai kyau, bi-da-bi. Shirin kaya daki-daki cikin kanti.

2.) **Wakilci** : uzini, bai wa wani wakilci (uzini)

Ordonnateur : **Matsari** (manaja) : mutunen da ke kula da kawo tsari, mai bayar da umurni. Matsarin wani kampani (Manajan kampani)

Ordre : **Tsari** : Shiri ,yadda aka shirya abubuwa, kawo tsari.

Ordre du jour : **Tsarin kanun mahawarar** : bi-da-bi na abubuwan da za a tattaunawa kansu a wani taro.

Ordre économique : **Tsarin tattalin arziki** : shirye-shiryen da suka shafi tattalin arziki.

Ordre judiciaire : Tsarin hurimai : dukan zaururrukan shari'a masu matsayi ɗaya.

Ordre public : kwanciyar hankalin al'umma

Organe : **Kungiya** : ma'aikata mai nauyin kula da tafiyar da ayyukan wasu ma'aikatun. Kungiyoyin (kafofin) Labaru iri-iri ne a Nijar.

Organe de contrôle : **Kungiya ta dubawa** : ma'aikata mai kula da dubawa da kuma bin ayyuka sau-da-ƙafa.

Organe exécutif : **Kungiyar** (hukumar) **zartarwa** : hukuma mai kula da zartar da dokoki.

Organe subsidiaire : **Hukumar idasawa** : ma'aikatar da ke ida cika aikin wata ma'aikatar.

Organigramme : **Jadawali** : Tsarin sassan ma'aikata da ayyukansu. Jadawalin wani kampani ka wata masana'anta.

Organisation 1.) **Tsari** : yadda aka shirya hukumomi da ayyukansu. An yi wani sabon tsarin hukumomi a Nijar.

2.) **Kungiya** : tsari mai neman cin ma wasu gurori. Kungiyar ma'aikata.

Organisation de l'état : Tsarin ƙasa : yadda aka tsara ayyukan ƙasa kuma ake tafiyar da su.

Organisation politique : Tsarin siyasa : yadda aka shinhiɗa wata siyasa.

Organisation sociale : Tsarin al'umma : yadda aka rarraba ayyuka cikin al'umma.

Organisation administrative : Tsarin ma'aikatu : yadda aka tsara ma'aikatu sassa-sassa.

Organisation communautaire : ƙungiyar haɗin kan al'umma.

Organisation de promotion mutuelle : ƙungiyar ci-gaban al'umma : tsarin tattalin rayuwa cikin al'umma.

Organisation des pouvoirs puyblics : Tsarin sassan mulki : yadda aka kalkasa iko : iko na gwamnati, na majalisar dokoki, da iko na fannin shari'a.

Organisation non gouvernementale : ƙungiya mai zaman kanta. Kungiya ce mai taimakon al'umma, mai samo kuɗin tafiyar da ayyukanta ta hanyar kyauta da taimako daga wasu mutane ko wani ƙasashe.

Organisation territoriale : Tsarin jahohi : yadda aka kalkasa ko rarraba hukumomin ƙasa.

Organisme : Kungiya/hukuma/kwamniti : wani reshe mai kula da wani aiki masamman. An kafa ƙungiyoyin majalisar ɗinkin duniya cikin kowace ƙasa da take mamba.

Organisme consultatif : kwamitin shawara : kwamitin da ake iya tuntuɓa don ya bayar da ra'ayinshi, da shawarshi kan wani al'amari.

Orientation : Manufa/hauda-wa kan hanya : zaɓe, nuna hanya. Sai bayan an binciki takardun ɗalibai ake hauda su hanyar ci-gaba da karatu.

Orientation politique : Manufar siyasa : nuna (zaɓar) hanya ta siyasa.

Loi d'orientation : Dokar nuna manufa : doka mai ƙayyade siyasar da za a zartar a wani fanni kuma cikin lokaci mai tsawo.

Orientation politique du gouvernement : Manufar siyasar gwamnatin : Hanyar da gwamnati ta ƙayyade don zartar da tsarin ayyukanta.

Originaire : Ɗan asilin : Wanda ya samo tushensi (ya fito) daga wata ƙasa ko wani wuri. Ɗan asilin wata ƙasa.

Original : Na ainahi : abun da bai fito daga wani abun ba, da ba a taɓa aikatawa ba a baya, sabo, wanda bai da kama. Ra'ayi na ainahi.

Origine : Asili : Tushe, matsiri, inda mutum ya ɗauko mafarinshi Asilinshi Afirika.

Origine nationale : ƙasar asili : ƙasar tushe.

Origine raciale : Iri : launin fatar tushe.

Origine sociale : Al'ummar asili : al'ummar da ke asilin mutum.

Orthodoxie financière : Ka'idodi na fannin kuɗi.

Otage : Garkuwa : kamuwa, mutunen da aka riƙe kuma da sakin shi ya danganta da samun biyan wata buƙata. Y'an fashin jirgin sama sun yi garkuwa da wani jirgin sama har sai an zuba musu wasu kuɗi masu tsoka.

Outil : Abun aiki : abun da ake amfani da shi wurin yin wani aiki. Kayan aiki. misali : kayan noma.

Outrage : Cin mutunci : Cin zarafi, rashin kunya, mugun zagi, laifin cin zarafin mutum cikin aikinshi. Cin mutuncin juju wurin shari'a.

Outrager : Yin cin mutunci : aikata laifin cin zarafin mutum cikin aikinshi. An gurƙusar da shi gaban shari'a saboda ya ci mutuncin juju.

Ouverture : Buɗi : farawa, somawa. An ɗage ranar buɗin yaƙin neman zaɓe.

Ouverture des vacances : Somawar hutu : lokacin hutun y'an majalisa ko y'an makaranta.

Ovation : Taɓi : Taɓi da jama'a ke yi wa wani babban mutum ko wani gwanin magana don girmama shi. An tarbi shugaban ƙasa da taɓi.

Ƥ

P.N.B : Jimillar dukiyar ƙasa.

Pacification : Kawo kwanciyar hankali : maido zaman lahiya, lumana ga wata ƙasa. Yarjejeniyar da aka sa hannu kanta tsakanin gwamnati da yan tawaye, ta kawo kwanciyar hankali cikin arewacin ƙasar Nijar.

Pacifiste : Mai son kwanciyar hankali : mai son lumana, mai neman zaman lahiya. Ministan cikin gida ya bi ta hanyoyi na lumana wajen warware rikice-rikice tsakanin manoma da makiyaya.

Pacte : Yarjejeniya : bayyanannen alƙawali tsakanin wasu ɓangarori. Shugaban ƙasa ya goyi bayan yarjejeniya ta ƙasa ɓaki ɗaya.

Pacte de non agression. Yarjejeniyar zaman lahiya : bayyanannen alƙawali da ƙasashe biyu ke ɗauka na kar su kai wa juna hari.

Pacte international : yarjejeniyar ƙasashen duniya : alƙawalin da dukan ƙasashe suka ɗauka.

Paix : Zaman lahiya : halin rayuwar da babu yaƙi, ko wani tashin hankali. Sanya hannu kan yarjejeniyar zaman lahiya.

Paix sociale : zaman lahiyar al'ummar : rayuwar al'umma cikin kwanciyar hankali da lumana.

Palabre : Surutu : hira mai tsawo ta rishin aiki, maras amfani. Gindin iccen surutu. Inwar surutu.

Panafricanisme : Kishin Afirika : ra'ayin fifita haɗin kan ƙasashen Afirika da ƙarfafa zumunta tsakaninsu. Ƙarfafa kishin Afirika.

Pancarte : Kahe : Karto mai wani rubutu wanda ake liƙawa ga katanga ko wani abu, don bayyana wa jama'a wani ra'ayi. kahen talla.

Paradoxal : Na saɓani : na shan bambam, na ƙaryatawa, ra'ayin da ya sha bambam da abun da aka amince ma. Halin saɓani.

Paragraphe : Sakin layi : Kowace gaba ta matani wadda ake farawa kan wani sabon layi. Sakin layi na wani matani.

Parajuriste : Mataimakin juju : mutunen da ba juju ba, yana bai wa juju hannu cikin tafiyar da aikinshi.

Parapher : Sa hannu : sa shaida. Sa hannu kan wata doka.

Parasite : Ci-ma-zaune : ɗan kwaraka (ɗan raraka), kaska, mutunen da ba ya komi, wanda ake ɗaukar nauyin rayuwarshi. Rayuwa cikin halin ci-ma-zaune.

Parasitisme : Halin ci-ma-zaune.

Parjure : Halin karya rantsu-wa : rantsuwar kafara, shaidar zur, halin saba wa alkawali. Doka ta buge ni idan na shiga halin karya rantsuwa.

Parjurer : Karya rantsuwa : yin rantsuwar kafar, saba wa alkawali. Dan shaidar ya karya rantsuwarshi.

Parlement : Majalisar dokoki : majalisa ko illahirin majalisoshi masu ikon kafa dokoki. An roshe majalisar dokoki.

Parlementaire : Dan majalisa dokoki : abun da ya shafi majalisa, mamba na majalisa, dipite. Y'an majalisar dokoki suna zaman taro na masamman.

Parquet : Lauyan jama'a : dukan rukunin alkalan da ke kokowar a yi aiki da doka (a zartar da doka, da gaskiya) don amfanin al'umma.

Parrainage : Tallafi : goyon baya ko gudunmuwar kud'i da ake yi wa wani mutum ko wani abu. An tafiyar da kasuwar baza kolin tare da tallafin minista mai kula da masana'antu da ayyukan hannu.

Partenaire : Abokin huld'a : abokin tarayya, kasa mai dangantaka (cud'ayya) da wata, ko wani a fannin siyasa, tattalin arziki ko a fannin al'adu... Abokan huld'ar neman ci-gaban kasashe.

Partenariat : Tarayya, huld'a: had'in gwiwar (game karfin) masana'antu ko wasu ma'aikatu don aikata wani abu. Rattaba hannu kan yarjejeniyar kafa tarayya (huld'a).

Parti : Jam'iyya : had'in kan mutane wad'anda ra'ayoyin da hanyoyinsu na siyasa suka zo d'aya. Y'an wata jam'iyyar siyasa (militan d'in wata jam'iyyar siyasa).

Participant : Mahalarci : wanda ya je wurin wani abu. Mahalarta taron gangamin y'an kad'an ne.

Participation : Halarta : zuwa wurin wani abu, sa baki. Zaben shugaban kasa bai samu halartar jama'a da dama ba.

Participation effective : Cikakkar halarta : Kawo kokarin kowa, tashi-tsaye na gaba d'aya (na kowa da kowa).

Participation massive : Gagarumar halarta : zuwan (tashi-tsayen) mutane masu d'imbin yawa.

Participation populaire : Halartar : al'umma tashi-tsayen al'umma.

Particularisme : Halin taka-maimai : hali na masamman, bambanci, hali inda a misali wata kabila ke bayyana abubuwanta na takamaimai (na masamman, bambance-bambancenta) ko tana neman a tabbatar mata da su kuma tana kokowar kare su. Halin takamaimai na siyasa.

Particulier : Na ƙashin kai : na masamman, takamaimai, na ainahi, na daban, mallakar mutum. Dukiyarshi ta ƙashin kanshi

Passage à tabac : Shan kashi : shan duka, yin dukar rishin imani. Kashin da y'an zanga-zangar da aka tsayar suka sha, ya kawo hayaniya wajen y'an siyasa.

Passeport : «Pazgo» : Kundi na shaidar zaman ɗ'an ƙasa da hukuma ke bai wa y'an ƙasarta don su samu damar yawatawa cikin wasu ƙasashe. Samun pazgo.

Pastoral : Na daji : abun da ya shafi karkara, da ya shafi kiwo.

Patente : Jula/Patanti : sunan da ake yi wa tara ko karo a can da. Biyan jula. Biyan patanti.

Patrie : Ƙasa : inda aka haihi mutum. Kishin ƙasa.

Patrimoine : Arziki (gado) : dukiya da albarkatun da wata al'umma ko wani gungun mutane suka tanada tamkar gado daga K a ƙ a n n i n - kakanni. Tattalin arzikin gado.

Patrimoine culturel : (arzikin) gado na al'adu : dukan tsare-tsare na gadin-gadin da ake da su har yanzu a huskar zaman al'umma da tabi'o'inta.

Patrimoine économique nationale. Arzikin ƙasa : dukiya da albarkatun da ƙasa ta gada daga kakannin-kakanni.

Patriote : Ɗan kishin ƙasa : Mai son ƙasarshi kuma yana nunawa. Zama cikakken ɗ'an kishin ƙasa.

Patriotique : Na kishin ƙasa : na mai son ƙasarshi, na nuna son ƙasarshi. Biyan lanho, ɗ'abi'a ce ta kishin ƙasa.

Patronage : Jagoranci : ƙarin daraja, ƙarin ɗ'aukaka ta hanyar wani babban mutum ko wata ƙungiya. Buɗe wani biki a ƙalƙashin jagorancin shugaban jamhuriya.

Pâturage : Makiyaya : wurin kiwo, inda bisashe ke kiwo. Wadatattar makiyaya (wadataccen wurin kiwo).

Pays : Ƙasa : Faɗin ƙasa. Kare ƙasarsa.

Pays en voie de développement : ƙasashe masu tasowa : dukan ƙasashe masu matsaikaicin hali, galibi ƙasashen Afirika ne.

Pays industrialisés : ƙasashe masu arzikin masana'antu : ƙasashen da suka bunƙasa, masu hannu da shuni.

Pays moins avancés : ƙasashe masu ƙaramin hali.

Paysan : Mutunen karkara : talakka, manomi, makiyayi.

Paysannerie : Al'ummar karkara : dukan mutanen karkara. Al'ummar karkara ta Nijar. Talakkawan Nijar.

Peine : Hukunci : shari'ar da ake wa mutum sakamakon laifinshi na taka doka. Yanke hukunci.

Peine de mort : Hukuncin kisa : hukuncin kashe mai laifin.

Pénalisation : Yanke hukunci: Misali : Hukuncin da aka yanke wa wani ɗan wasan ƙwallon ƙafa.

Pénaliser : Hukuntawa: Kuntatawa : Sabon matakin da aka ɗauka a game da jangali ya ƙuntata wa yan kasuwa.

Penchant politique : Ra'ayin siyasa : hanyar siyasar da mutum ya zaɓa. Yana da ra'ayinshi na siyasa.

Pénitentiaire : Na gidan kaso: abun da ya shafi gidan kaso. Ana yin bincike don gano dalillan zanga-zangar nan ta gidan kaso.

Pensée : Tunani : ra'ayi, nufi. Y'ancin yin tunanin da ake so.

Pension : Kuɗin ritaya : kuɗin antare. Kuɗin da wata ƙungiya ko gwamnati ke zuba wa mutum sakamakon aikin da ya yi a can da. Y'a zo amsar kuɗinshi na ritaya.

Pépinière : Hilin renon (tattalin) dashe : wurin da ake tanadin dashen da za a shuka. Ziyarta hilin (tattalin) dashe.

Pérennité : Ɗorewa : halin abun da bai ƙarewa da wuri, mai ɗaukar dogon lokaci. Ɗorewar zaman lahiya.

Perfectionnement : Inganta : gyaruwa, ƙaruwa, kyautata. Ingantar wata husa'a.

Performances créatrices : Gwanintar ƙage-ƙage : ƙoƙarin ƙere-ƙere. Allah ya ba shi gwanintar ƙage-ƙage.

Péril : Haɗari : babbar matsala. K'asar da ke fuskantar haɗari.

Période de crise : Lokaci na matsala : lokaci na hargitsi, na rikici, na rishi. Fuskantar wani lokaci na matsala.

Perquisition : Caji : Cikakken binciken da juju ko wani babban ɗan sanda ke yi a wani wurin da ake iya samo shaidodin masu nuna tabbacin laifin. Umurnin yin caji.

Persécuter : Tsananta : azabta, matsa lamba, tsananta wa al'umma.

Personnalité : Babban mutum: mutum mai muƙani, mai ƙwarjini

Personnalité éminente : Mashahurin babban mutum : shahararren babban mutum, mai ƙwarjini. Mashahurran manyan mutane sun haɗu wajen rasuwar sarki Hasan na biyu na Maroko.

Personnalité Juridique : Masanin shari'a : mutumen da ke da ilimi (wata masaniya) a fannin shari'a. Juju masanin shari'a ne.

Personne morale : Tsari mai ƙa'ida : K'ungiya, ma'aikata .. K'asa tsari ne mai ƙa'ida

Personne passive : Mutum shiru-shiru : mutum kurum, mutunen da bai bayar da ra'ayinshi.

Personne physique : Mutum da kanshi : mutum da cikakkar siffarshi. An ce sai mutum ya zo da kanshi .

Personne ressource : Mai shaidar ƙwarai : mashawarcin ƙwarai, wanda ra'ayinshi ke da mahimmanci, wanda ake bukatar ra'ayinshi. Y'in kiran wani mai shaidar ƙwarai.

Perspective : Zato : tsammani, fata, sa rai ga wani abu ko shakkun wani abu. Kyakkyawan zato.

Peuple : Al'umma : dukan mutanen da ke zaune a wani keɓaɓɓen wuri guda kuma suna ƙalƙashin hukumci guda, y'an ƙasa. Al'ummar Nijar, y'an ƙasar Nijar.

Peuplement : Cinkoson al'umma : taruwar al'umma wuri guda. Cinkoson al'umma cikin birni.

Phase : Taki/Hawa/Hali : kowanne daga sauye-sauyen da ke bin juna na wani abu ; hawa. Takin ƙarshe.

Phase de croisière : Makimancin hali : matsakaicin taki, hawa, gudu. Kasancewa cikin makimancin hali.

Philosophie : Ilimin falsafa : fannin tunani mai bukatar yin nazari kan halittu da mafarinsu, da yin hattara cikin rayuwa. Ilimin falsafar duniya.

Pilier : Ginshiki : shisshike : madogara, matokari, abun da ake dafawa don tsayar da wani abu. Noma da kiwo su ne shikashikan tattalin arziki a Nijar.

Pillage : Wasashe : wasoso : ɓannar da wasoson ya haddasa. Wasashe dukiyar.

Pilote : Matuki : mai tuka jirgin sama, motar gasar tsere, ko jirgin ruwa. Samun farmi (lasin) na zama matuki.

Pionnier : wanda ya fara.

Plaider : Goya baya : kare gaskiya, ko musantar da wani abu gaban shari'a. Ya goyi bayan rishin laifin.

Plainte : Ƙara : Kukan da mutum yake kaiwa gaban koti cewa da an yi mashi laifi. Ya kai ƙaran abokin fad'anshi.

Plan : Fasali : tsari : dukan matakan da aka tsayar don zartar da wasu ayyuka. Girka tsarin sakin ragamar mulki.

Plan régional : fasali, tsari jaha : matakan da aka tsayar don zartar da wasu ayyuka na wata jaha.

Planification : Yin fasali/tsari : fasaltawa, shiryawa. Yin fasali na ilimin harsuna yana bayar da damar koya harsunan ƙasa da kyau.

Planifier : Faltawa : tsarawa, shiryawa bisa kan wani fasalin ci-gaba. Fasalta tattalin arziki.

Planning : Fasali/tsari : tsarin aiki, tsarin fiddo amfani, daidaitawa. Yin tsarin haihuwa, daidaita haihuwa.

Plate-forme revendicative : : duk wata matashiyar ƙorahe-ƙorahe ; masomar "koke-koke"

Plébiscite : Kuri'ar neman ra'ayi : zaɓe, jefa ƙuri'ar al'umma ta amincewa ko rishin amincewarta da wani al'amari. Y'an adawa sun nemi a jefa kuri'ar neman ra'ayi a game da zancen rushe majalisar dokoki.

Plein-droit : Cikakken y'anci : Y'ancin da aka amince da shi gaba ɗ'ayanshi, samun damar wani abu. Y'an ƙasa suna da cikakken y'ancin tambayar gwamnati da ta yi masu abubuwa na kyautata jin daɗin rayuwarsu.

Plein épanouissement des populations : Cikakken jin daɗin rayuwar al'umma : ci-gaban al'umma. Ya kamata gwamnati ta girka tsarin tattalin arziki don cikakken jin daɗin rayuwar al'umma.

Plein pouvoir : Cikakken iko : ikon kama-karya, duk iko a hannun mutum ɗ'aya. A lokacin mulkin kama-karya, shugaban ƙasa ke da cikakken iko.

Plénière : Taron majalisa : taro na kowa, mai gayyatar dukan mambobin. Kiran taron majalisa.

Plénitude : Cika : halin abun da yake isasshe, wadatacce. Yana da cikakken hankali.

Pluralisme : Tsarin yawaitawa : tsarin siyasa, ko na zaman al'umma, ko na tattalin arziki mai karɓar bambancin ra'ayi da yawa.

Pluralisme démocratique : Tsarin mulki mai yawaita jam'iyyun siyasa.

Plurilinguisme : Tarin harsuna : hali na yawan harsuna cikin wani yanki ko wata ƙasa. Tarin harsuna cikin ƙasashen Afirika.

Pluviométrie : Sakamakon ruwan sama : awon yawan ruwan saman da suka faɗi.

Pluviosité : Yawan ruwan sama : daidai ruwan saman da suka faɗi a faɗin wani ƙayyadadden wuri kuma cikin wani lokaci.

Pôle de compétence : Cibiyar yanke shawara : wurin ɗ'aukar matakai. Nufa wajen wata cibiyar yanke shawara.

Police : Y'an sanda : dukan jami'an tsaro, y'an doka masu kwantar da tarzoma.

Police municipale : y'an sandar kwamin : y'an sandar da aka keɓe wa kwamin.

Politesse : Ladabi : biyayya, dukan halaye na iya zama da mutane. Nuna ladabi.

Politique : Siyasa : tsari, fasaha da hanyoyin tafiyar da ikon (shugabancin), al'umma. Siyasar hulɗar ƙasa de ƙasashen waje.

Politique culturelle : Siyasar yaɗa al'adu : hanyoyin da ƙasa ke ɗauka don bunƙasa al'adunta.

Politique d'hydraulique et de l'environnement : Siyar fannin ruwa da mahalli : tsarin kyautata harakokin ruwa da kare mahalli.

Politique d'urbanisme et de l'habitat : Siyasar gyaren birane da gina gidaje : tsarin mayar da birane na zamani da samar da gidajen kwanci.

Politique de l'emploi : siyasar fannin albashi : tsarin biyan albashi yadda ya kamata.

Politique de revalorisation du travail manuel : Siyasar inganta aikin hannu : tsari na kyautata ayyukan hannu.

Politique de santé et d'action sociale : Siyasar kiwon lafiya da agaji : tsarin kyautata kiwon lafiyar al'umma da kawo mata taimako.

Politique d'affaiblir et de diviser pour mieux régner : Siyasar kawo ɓaraka don ƙarfafa mulki : dubarun kawo sabarin tsakani mutane, raba kawunansu don cin moriyar (ribar) halin da suke ciki.

Politique de décentralisation : Siyasar sakin ragamar mulki : tsarin bai wa jahohi ko ƙananan hukumomi ikon (yancin) tafiyar da ayyukansu na tattalin arziki da ɗaukar wasu matakai.

Politique de développement : Tsarin ci-gaba : tsari na shinhiɗa ayyukan ci-gaba :

Politique judicieuse et audacieuse : ƙaƙƙafar siyasa ta adalci : daidaitacciyar siyasa, tsari na gaskiya tare da nuna kuzari.

Politique productiviste : Siyasar bunƙasa amfani : tsarin hiddo amfani daban-daban.

Pollution : Gurɓacewa : lalacewa, taɓarɓarewa, ƙazamcewa wuri ta hanyar shara mai guba. Gurɓacewar yanayi.

Ponctualité : Rishin makara : a lokaci. Rishin makarar ma'aikaci.

Populaire : Na al'umma : abun da yake na jama'a ne, da ya fito daga jama'a. Gwamnati ta samu goyon bayan al'umma.

Popularisation : Bayyanawa : yaɗawa, sanarwa, ruwaitawa, shaidawa. Bayyana tsarin mulki ga jama'a.

Populariser : Bayyanar da : yaɗa, sanar da. Bayyanar da doka.

Popularité : Farin jini : tashe, suna, mashahuranta, samin farin jini.

Population : Al'umma : dukan mutanen da ke zaune a wani kebabben wuri. Al'ummar Nijar ta kai miliyan 8 a shekarar 1988.

Porte-feuille ministériel : Mukamin minista : aikin minista, matsayin minista. Rike mukamin minista biyu.

Porte-parole : Kakaki : mutunen da ake wakilta don ya kai magana da sunan wani ko wata majalisa. Kakakin gwamnati.

Porter atteinte : Taka hakki : walakantar da, yin cin mutunci, cin zarafi. Taka hakkin yan kasa.

Portion : Bangare : tsayi, kashi, rabon da ake bai wa wani. Bangaren hili (kasa).

Positif : Na kwarai : mai amfani, mai kyau. Balas na kwarai.

Position : Ra'ayi : nufi. Ya rantse ba za ya sauya ra'ayinshi ba

Possibilité : Dama : hali, yiwuwa. Damar zaben wani abu.

Poste : Mukami (aiki) : wurin aiki : rike babban mukami.

Poste administratif : karamar hukumar gunduma. Yankin hukuma na kalkashin lardi a Nijar.

Poste de police : Ohushin yan sanda.

Poste budgétaire : sashe na kasahin kudi : sashen wani babi cikin kundin kasahin kudi.

Postérité : Baya : na tahe (mutane) a duniya. A yi aiki mai kyau saboda baya.

Pot-de-vin : Rashawa : toshiyar baki. Kudin da ake bai wa wani don gyaren wata haraka. Karbar rashawa.

Potentialité : Halin karhin kundu : halin abun da ke iya aiwatawa da kawo amfani.

Potentiel : Karhin kundu : dukan albarkatun da wata kasa ko wani gungun mutane ko wani mutum suka mallaka. Karhin kundun soja.

Pourcentage : Kashi cikin dari : yawa ko girman wani abu cikin kashi dari na wani abun. Ya lashe zabe da kashi 55 cikin 100 na kuri'u.

Pourparlers : Shawarwari : tattaunawa tsakanin kasashe ... don cin ma wata yarjejeniya. Fara shawarwani.

Poursuite : Yin shari'a : kara matakan shari'a da ake dauka ga wanda ya taka doka, ko wanda bai cika alkawali ba. Yana shawarar ya yi karan dan hayarshi.

Poursuivre : Kai kara : kai mutum gaban koti.

Pouvoir : Iko : hukuma, mulki gwamnatin kasa. Ga tsari na demokaradiya, iko na ga al'ummar kasa.

Pouvoir absolu : Cikakken iko/Ikon kama-karya : ikon da ba a raba shi da kowa.

Pouvoir exécutif : hukumar zartarwa : hukumar da ke zartar da dokoki da ayyukan ma'aikatun gwamnati ; gwamnati.

Pouvoir illimité : ikon da ba iyaka : ikon da ke bai wa ma'ikaci yancin yin abun da ya ga dama.

Pouvoir judiciaire : Hukumar shari'a : hukumar da ke gabatar da shari'a, malaman shari'a.

Pouvoir législatif : hukumar dokoki : hukumar da ke kula da kafa dokoki.

Pouvoir personnel : Karfin mutum : iko, ƙokarin mutum.

Pouvoirs exceptionnels : iko na masamman.

Pouvoir central : hukumar zartarwa.

Pouvoir décentralisé : Rarrababban iko.

Pragmatisme : Inganci : halin mutunen da ke iya tarar kowane hali ; mai son aikatawa, mai amfani sosai. Nuna inganci.

Pré-financement : Bashi (bada ƙafa) : bashin da ake bai wa wani mai masana'anta don sarrafa kayan da za ya sayarwa a ƙetare ; bada ƙafa. Ya tambayi gwamnati da ta ba shi bashi (ta ba shi ƙafa).

Préalable : Sharaɗi : abu ko abubuwan da ɓangare guda ke ƙayyadewa da sai an tabbatar da su kafin a fara duk wata tattaunawa. Sharaɗin da y'an tawaye suka ƙayyade kafin su halarci zaman shawarwarin kawo zaman lafiya, shi ne na a jaye sojoji daga yankin arewa na ƙasa.

Préambule : Gabatarwa : sashen farko na tsarin mulki, ko wata yarjejeniya mai bayyana mahimman kanun wasu dokoki.

Préavis : Kashedi : sanarwar da ake gabatar kafin a soke wata yarjejeniya ko kafin a tsunduma cikin yajin aiki. Kungiyar ma'aikata ta kai kashedinta na tsunduma cikin yajin aiki.

Prébende : Moriya/gajiya/ riba/amfani : kwaɗai, amfanin da ake samu daga wani hali. neman cin moriyar abu.

Prébendier : Mai cin moriya : mai cin gajiyar abu, mai cin ribar abu, mai cin amfanin abu, makwaɗaici.

Précolonial : Na kafin mulkin mallaka : yadda abu yake kafin shigowar mulkin mallaka. Afirika ta kafin mulkin mallaka

Préconiser : Shawartawa : bayar da goyon baya, bayar da gargaɗi. Shawarta wata hanyar warware wata matsala.

Prédateur : Mugu : mutum ko wani gungu mai azabta wa masu ƙaramin ƙarhi. Mugu ne sananne.

Prédécesseur : Wanda ya rigaya : mutunen da ya rigayi

wani kama wani mukami, wani aiki. Yaba aikin wanda ya rigaya

Préface : Mukaddama : gabatarwa. Mukaddamar littahi.

Préfecture : Hukumar jaha : kewaye ko yankin ikon hukumar jaha ; ma'aikatar gwamnan jaha.

Préfet : Gwamnan jaha : shugaban hukumar jaha. Gwamnonin jaha su ne shugabannin jahohi.

Préjudice : Lahani : laihin taka doka ko na yi wa wani ɓanna. Ya yi mashi lahani.

Préjudiciable : Mai kawo lahani : abun ke haddasa laifi, ɓanna, ko da ke iya haddasa su. Aikata wani abu mai kawo lahani.

Préjugé : Tsammani : ra'ayin farko na yabo ko na rishin yabon wani. Aza tsammani kan wani abu.

Préliminaire : Na share fage : na shirin farko, na farinfarawa, na shirya wani abu. Haɗuwar share fage.

Prématuré : Bakwaini/ gaggautacce : abun da ke faruwa kafin lokacin da ya kamata ; kwan gaba. Bakwainin yaro.

Prémédité : Tsararre : shiryayye. Abun da aka shirya, aka tsara da kyau kafin aikata shi (galibi abun assha ne). Aikata wani tsararren abu.

Première lecture : Nazarin farko : gabatar da doka a majalisar dokoki don neman amincewarta.

Prénatal : Na kafin haihuwa : abun da ake yi kafin mace ta haihu. Awo aiki ne na kafin haihuwa.

Prendre : Ɗauka : prendre en charge : Ɗaukar nauyi : kula da wani abu.

Prendre en considération : Lissafawa da : yin aiki da. prendre la relève : Ɗaukar wuri : wucewa da aikin da wani ya fara.

Prendre par ordonnance : Ɗaukar ƙudiri : yancin da tsarin mulki ya kebe wa shugaban ƙasa na ɗaukar wasu dokoki ba tare da shawarar majalisar dokoki ba.

Préoccupation : Lalura : abun ɗaukar hankali, damuwa, matsala. Ya samu lalura.

Prépondérance : Wadata : ɗaukaka, haɓaka, bunƙasa, ƙarfin arziki. ƙasa mai wadata.

Prépondérer : Wadatar da : ɗaukakawa, haɓakar da, bunƙasar da. Wadatar da kampani/ɗaukaka kampani/ bunƙasa kampani.

Prérogative : Yancin : damar da aiki ko mukamin mutum ke tanada mashi ; gatanci. Jagorancin taron majalisar ministoci, yancin shugaban ƙasa ne.

Présélection : Zaɓen fari : raurayar farko. Zaɓen fari na yan takara.

Préservation de l'environnement : Tattalin mahalli : kariyar mahalli. Ya kyautu a rika yin ayyuka na tattalin mahalli don a yaki hamada.

Présidence :1.) **Shugabancin kasa :** mukamin shugaban jamhuriya

2.) **Gida, fadar shugaban jamhuriya :** Jakada ya samu tattaunawa a fad'ar shugaban jamhuriya.

Président : 1.) **Shugaba jamhuriya :** Shugaban jamhuriya ke nad'a paraminista.

2.) Shugaban wata majalisa ko wata kungiya, ko jagoran wani taro. Jagoran zaman taro.

Président par-intérim : Shugaba na wucin gado : wanda ke zartar da ayyukan shugaban in ba ya nan.

Présidentiel : Na shugaba : Na shugabanci : abun da ya shafi shugaba. Zabe na shugaban kasa.

Présider : Shugabanta : jagoranta (na wani taro..) Shugaban jamhuriya ya shugabanci wani taron manyan ma'aikata.

Presse : Kahohin labaru : dukan abubuwan watsa labaru. Y'ancin watsa labaru.

Presse internationale : kahohin labaru na duniya : dukan hanyoyin watsa labaru na kasashen duniya.

Presse locale : kahohin labaru na gida : hanyoyin watsa labaru na wata kasa.

Pression : Matsi : damuwar da ake yi wa wani don a sa ya canza ra'ayinshi, tasiri. Matsin da al'umma ta yi wa gwamnati ta sa gwamnatin ta soke wasu miyagun matakai da ta d'auka.

Prestataire : Mai amfani da.... Mutumen da ke amfana da wani alawus.

Prestige : Martaba : daraja, kwarjini. Samun martaba kwarai cikin jama'a.

Prestigieux : Mai martaba : Mai daraja, mai kwarjini. Babban gari mai martaba.

Présumé : wanda ake zato : Yin tsammani, d'auka cewa. Wanda ake zaton ya aikata laifi ya tsare.

Prêter serment : Ɗaukar alkawali : rantsuwa, alwashi, d'aukar alkawalin cika wata niyya. Shugaban jamhuriya ya d'auki alkawali a bainar jama'a.

Preuve : Hujja : Abin da ke tabbatar da gaskiyar wani abu. Aza wa mutum laifi ba tare da hujja ba.

Prévenir : 1/ Shaidawa : Sanassar da, gayi. Shaida wa mutum wani abu.

2/ Gargad'i : fad'akar da, riga-kahi. Riga-kahi ya fi magani.

Préventif : Na riga-kahi : matakai masu hana aukuwar wani abu. Ɗaukar matakai na.

Prévention : Riga-kahi : tunkarar wani abu kafin ya auku yin riga-kahin wata cuta.

Prévision : tsammani : yin hasashe kan wani abu. Yan siyasa sun tura wakilansu a rumfunan zaɓe don suna tsammanin ko an shirya magudi.

Prévoir : yin hasahe : tsinkaya: hange, hango, yin hange. Kungiyar shirya zaɓe na hasashen shirya zaɓe a watan Oktoba.

Prévoyance : Tsinkaye : tsinkaye, hangen nesa. Yana da tsinkayen nesa ƙwarai.

Primordial : muhimmi : mai muhimmanci, abin ƙwarai. Gudunmuwar yan ƙasa abu ne mai muhimmanci cikin tafiyar da tattalin arzikin ƙasa.

Principe : Ka'ida : ƙa'idodi ko dokokin da ake dogara kansu wajen tafiyar da wani abu. Ka'idar demokaradiya ita ce na zaɓar abin da mutum ke so.

. Principe fondamental : muhimmiyar ƙa'ida : ƙa'idar da ke sahun gaba wajen tafiyar da wani abu.

. Principe intangible : ƙa'idar da ba ta takuwa.

Prioritaire : Na sahun gaba : muhimman kashe-kashen kudin ƙasa da ke sahun gaba.

Priorité : fifiko : muhimmi, na sahun gaba. Gwamnatocin ƙasashen Afirika suna fifita fannin kiyon lafiya, da kuma fannin horo da bayar da ilimi.

Prise de conscience : Sanin ciwom kai : nazari kan abubuwan duniya, kawo kimtsi cikin rayuwarsa ta duniya. Aikata abin rishin sanin ciwon kai.

Prise en charge : Ɗaukar nauyi : kula da, kiyayewa kan wani abu. Ɗaukar nauyin iyalansa.

Prisonnier d'opinion : Ɗan kason ra'ayin siyasa : mutanen da ke zaune gidan kaso a dalilin ra'ayinsa na siyasa. Nelson Mandela yana cikin yan kason ra'ayin siyasa wanda ya fi suna a duniya.

Privatisation : Halin sayar da : sanya masana'antun gwamnati kasuwa, mayar da su masana'antu masu zaman kansu. Sayar da masa na'anta.

Privatiser : Sayar da : Sanyawa kasuwa, sayar da gwamnati na zaman sassantawa da yan. Kwadago don shire-shiren sayar da waɗansu masana'antan gwamnati.

Privé : Mai zaman kansa : wanda ba na gwamnati ba.

Privilège : Gatanci : tattali da tanadi na musamman da ake yi wa mutum. Samun gatanci mai ƙarfi.

Prix Nobel : Tukwicin nobel : Kyauta da ake yi wa mutum

dangance da wani ƙokari da ya nuna kan fannin ilimin kimiyya, ko kan fannin nuna hakuri. Samun tukwicin nobel.

Problématique : Dubara : hanyoyin ake ɗauka don ciwo kan wata matsala. Shirya dubara.

Problème : matsala : abin damuwa, rigima. Shawo kan matsalolin rishin kwanciyar hankali cikin manya-manyan birane.

Procédure : Hanya : matakan da suka dace a ɗauka don cin ma wani guri. Bin hanyar shari'a.

. **Procédure pénale :** sashen shari'a mai nazari kan matakan doka.

Procès : Shari'a : Yanke hukunci tsakanin mutane, ko ɓangarori daban-daban

Procès-verbal : rahoto : takaici.

Proclamation : Bayyanawa : shela, yekuwa. Bayyana sakamakon zaɓe.

Procuration : Izinin wakilci : Izinin da wani ke bai wa wani don shi wakilce shi. Bai wa mutum izinin wakilci.

Procureur : Lauya.

Procureur de la République : lauyan gwamnati.

Producteur : Mai sarrafawa : kamfani, ko mutum mai sarrafa kayayyaki. ƙasashen turai na sarrafa kayayyaki da yawa.

Productif : Mai amfani : mai albarka, mai bayar da riba. Kasuwanci sana'a ce mai amfani ƙwarai.

Production : Amfani ; sakamako, kayayyaki sarofawa : kayayyakin da ake ƙerawa daga kampanoni daban-daban. Kasar Nijar na ɗauko kayayyakin sarrafawa da yawa.

. **Produit agricole : amfanin gona :** albarkar gona.

Production artistiques : ayyukan fasaha : ayyukan da suka danganta da ƙirkire-ƙirkire na fasaha.

. **Production littéraires : ayyukan adabi :** ayyuka masu nazari kan adabi.

Productions scientifiques : ayyukan kimiyya : ayyuka da suka shafi ilimin kimiyya.

Produit : Albarka : amfani, sakamako. Albarkar gona.

Profanation : rishin girma-mawa : rishin daratta wani abin da ya dace a daratta mai girma. Rishin girmama wani kabari.

Professer : Bayyanawa : Aikatawa : yin wata ibada, ko kariyar waɗansu kalamai. Aikata addinin kirista.

Profession : Sana'a : aikin da mutum ke yi don ciyar da kanshi. Sana'ar hannu.

Profession libérale : Sana'ar

kansa. Sana'a wadda mutum ke yi don kanshi.

Profit : Riba : amfanin da ake samu a game da wani abu. Cin riba

Programmation : (Takardar) sa rana ; shiri : Shiri, tsari. Gabatar da takardar shiri ; sa ranar haɗuwa.

Programme : Shirye-shirye : tsare-tsaren da ake gabatar da su don cim ma wani guri. Shirye-shiryen wata haɗuwa.

. Programme social : **tsarin ayyukan jin daɗin jama'a :** gabatar da tsara-tsare don kyautata rayuwar jama'a.

. **Programmation électoral : tsarin zaɓe :** tsare-tsaren gabatar da zaɓe sa ranaikun zaɓe.

Progression : ci-gaba : karuwa, ci-gaban yan tawaye wajen babban birni..

Prohiber : Haramta : hanawa daga doka ko addini. An haramta shigowa da miyagun ƙwayoyi a ƙasar Nijar.

Prohibitif : Mai tsananin tsada : Wanda ba ya sayuwa saboda kuɗinshi sun hamɓare. Kayayyaki masu tsananin tsada.

Projet : tsari : guri : Shirye-shiryen da ake yi da niyyar gabatar da yin nazari kan wani tsari.

. **Projet de société : tsarin jama'a :** tsarin kyautata rayuwar jama'a.

Prolifération : yaɗuwa : barbazuwa, ruɓanyawa, warwatsuwa da sauki. Yaɗuwar miyagun kayayyakin yaki.

Proliférer : yaɗawa : ruɓunyawa,barbazawa, watsawa da sauki. Yaɗawar miyagun ƙwayoyi Ruɓunya kuɗin ganyi.

Promotion : ƙarin girma : ci-gaba. Samun ƙarin girma.

. **Promotion de la femme :** ci-gaban mata, bai wa mata daraja, wayar masu da kai.

. **Promotion de la production et des échanges : bunƙasar (ci-gaban) saye da saidawa :** Samun ƙaruwa kan fannin saye da saidawa.

. **Promotion des langues nationales : Haɓakar harsunan gida :** bai wa harshunan gida daraja.

Promouvoir : haɓakar da , bunƙasawa : Kyautata wani abu, gyara shi haɓakar da fannin kiwon lafiya.

Promulgation d'une loi : halin tabbatar da doka : bayyanar da doka a hukunce. An tabbatar da doka kan sake tsarin horo da bayar da ilimi.

Promulguer : tabbatar da ; bayyanar da doka. majalasar dokoki ka tabbatar da dokoki cikin ƙasa.

Prôner : nema : yaba ga wani abu, yin fata. Neman zaman lafiya.

Pronostic : Hasashe : Kimantawa, tsammani. Yin hasashe kan wanda za ya cin galaba a game da wata kombala

Propagande : farfaganda : yakin neman zabe. Y'an siyasa sun shiga farfaganda

Prospos licencieux : Bakaken maganganu : maganganun da ke kumshe de zagi cikinsu. Ranshi ya bace saboda an gaya mishi bakar magana.

Proposition : shawara : tayi. Bai wa wani shawara.

Propriété : Mallaka : abin da yake na kashin kan mutum. mallakar kasa.

Proscrire : haramtawa : hani, yardawa, kawar da ; ya kyautu y'an kasa su haramta bambance-bambance tsakaninsu.

Prospecteur : mai bincike : mai nema samo wani abu. Mai neman gano kwancin zinariya.

Prospection : bincike : bincike don gano kwancin albarkatun kasa. Binciken neman man petir.

Prospérité : albarka : arziki, wadata cikin kasa

Protection : kariya : taimako, gudunmuwa, tsaro . Kare mata da kananan yara a game da kamuwa da cututtuka.

Protection de l'environnement : kariyar muhalli : kula don kiyaye tabarbarewar muhalli.

Protection des droits : kiyaye hakki : kariyar y'ancin jama'a.

Protestation : rishin yarda : kin amincewa, zanga-zanga. Jama'ar kasa sun nuna rishin yardar su da wani tsarin gwamnati ta hanyar shirya zanga-zanga.

Protocolaire : na tsari ; na fadanci : wanda ya shafi fadanci cikin wand'ansu tsare-tsare. Shagulgulan tsare-tsare na fadanci.

Protocole : tsari ; fadanci : dukan shire-shiren wad'ansu shagulgula, ko kuma wata dangantaka. Sanya hannu kan wani tsari.

Prototype : na asili : na ainahi, orijina, iri guda, gangariya. Sayen wani abu na asili.

Provenance : asali : tushe. Y'an asalin kasar Marad'i na mahawara.

Province : lardi : yankin kasa da ke karkashin hukuncin sarkin gargajiya. Lardin Marad'i.

Provisoire : Na wucin gadi : na karamin lokaci, na rikon kwarya. Matakan wucin gadi.

Provocation : Takula : jawowa, tunzurawa. Takulo fad'a.

Psycho-sociologie : ilimin halin d'an Adam da na

zamantakewa : ilimi mai nazari kan halin ɗan Adam, dangance da halin zamentakewarsa. Karatun ilimin halin ɗan Adam da na zamantakewa.

Pshychologie : Ilimin halin ɗan Adam : ilimi na sanin halin ɗan Adam ; yin nazari kan halin gungun jama'a.

Psychologique : Na halin ɗan Adam : wanda ya shafi sanin halin ɗan Adam. Dubarun gano halin ɗan Adam.

Public : jama'a : wanda ya shafi jama'a, na ƙasa, na mutane. Gayyatar jama'a.

Publication : Bayyana : halin tabbatar da ; bayyana doka.

Publicité : talla : taɗa darajar kayansa don jawo hankalin jama'a da su zo su saya. Yin tallar kayayyaki.

Publier : bayyanar da : wallafawa, gabatar wa jama'a.

Puissance : ikon aikatawa : Karfin aikata wani abu yana da babban ikon aikata da harakokin mulkin ƙasa.

Puissances étrangères : ƙasashe masu hannu da shuni : ƙasashe masu ƙarhin arziki.

Punir : hukuntawa : ɗaure mutum, ko cin tarar shi dangance da laifin da ya aikata. Doka na hukunta duk wanda ya aikata laifi.

Pure imagination : shucin gizo : lissafe-lissafen banza. Jawabin da ya gabatar shucin gizo kawai ne.

Pyramide des âges : dalar shekaru : ajin-ajin jama'a cikin ƙasa dangance da yawan shekarunsu. Dalar shekarun jama'a cikin ƙasa.

Q

Qualification : Halin ƙayyadewa : halin nuna irin laifi

Qualité : halin kyau : na ƙwarai, na gari. Samun kyakyawan tabi'u.

Quantité : yawa : abu mai tay rin yawa. An kawo mishi hatsi da yawa.

Quartier : unguwa : laska, waje. An shirya kombala tsakanin unguyoyi daban-daban na birnin yamai.

Querelle : faɗa : gardandami, hasuma. Neman faɗa da mutane.

Questeur : raɓaɓben ɗan buran majalisa : mutunen da aka zaɓacikin buran wata majalasa don tafiyar da harakokin kuɗi, ko kuma harakokin hukumanci. An saurari bayyanai kan harakokin kuɗi daga zaɓaɓben ɗan buran majalasa mai kula da wannan fannin.

Question : tambaya : Neman bayyanai don fahimtar wani abu. Yin tambiyoyi.

Question écrites : Rubutattun tambayoyi : tambayoyin da ɗan majalasa ke aika wa wani minista ta hanyar mujallar gwamnati a rubuce, kuma a mayar mishi da amsa ta wannan hanyar.

Questions orales : tambayoyin baki : tambayoyi da ɗan majalasa ke yi wa minista kai tsaye cikin majalasar dokoki.

Question de routine : tambayoyin yau-da-kullum : tambayoyin da aka saba da su.

Questionnaire : tsarin tambayoyi : shiryayyin tambayoyi da ake yi wa mutum da niyyar tafiyar da wani bincike ; gabatar wa mutum tsarin tambayoyin.

Quête : Biɗa : nema, tattarawa. Biɗar bayyanai.

Quiétude : kwanciyar hankali : zaman lafiya. Kwanciyar hankali cikin ƙasa.

Quittance : shaidar biya : takarda mai tabbatar da mutum ya biya kuɗin wani abu. Shaidar biyan lanho.

Quitus : shaidar tafiyar da harakoki da kyau : takardar da ke nuna mutum ya gudanar da harakoki yadda ta kamata. An bashi takardar shaidar tafiyar da harakoki da kyau.

Quorum : yawan isa shawara : gwargwadon mutane da ya kamata su halara don soma mafawara. An ɗaga ranar mafawarar saboda mutane ba su cika yawan isa shawara ba.

Quota : Mizani : Daidai bakin da aka kayyade, yawa mizanin yan makaranta.

Quotidien : mai bayyana kullum : na yau da kullum. Jarida mai bayyana kullum.

Quotient : Sakamakon rabo : adadin da ake samu daga rabon wani adadi da wani.

R

Race : Jinsi : ɗaya daga cikin abubuwan da ke bambanta jama'ar da ke zaune a bayan doron ƙasa ; jinsin baƙar fata.

Racine : saye : abin da ke girkar da wani abu, ko kuma mai asulantar da shi. Manyan jam'iyun siyasa sun yi sayu cikin ƙasarmu.

Racisme : bambancin launin fata : nuna bambanci dangance da launin fata. Tashi tsaye kan y'an nuna bambancin launin fata cikin duniya baki ɗaya.

Radical : masu tsauri : kawo cikakken sauyi cikin wani tsari. Yin canje-canje masu tsauri.

Radicaliser : tsaurarra : sanya kaifi cikin wani abu, sanya tsauri. Tsaurarra yajin aikin.

Radicalisme : tsaurin ra'ayi : nuna rishin amincewa kan dukan abubuwa. Mai tsaurin ra'ayi kan fannin siyasa.

Radio : Radiyo : kafar labaru da ake saurare.

Raid : Hari : kai farmaki ga abokan gaba. Rundunonin sojojin Amarika sun kai wa rundunar sojin Iraki hari.

Raison : hankali : abun da ke bai wa ɗan Adam damar yin nazari, da yin lissafi. Ya ɓatar da hankalinshi.

Raison d'être : mafari : dalilin wani abu.

Ralliement : Goyon baya : Amincewa da wani ra'ayi, yarda. Samun goyon baya.

Rapatrier : mayar da a ƙasar ainahi : turo mutum a ƙasarshi ta ainahi. Am mayar da y'an gudun hijira a ƙasarsu.

Rappel : kira : bai wa mutum umurnin shi dawo wani wuri. An kira jakadi.

Rappel à l'ordre : kashedi : jawo hankalin mutum na ya kawo kimtsi, a game da wani hargitsi da yake shirin shibkawa.

Rapport : Dangantaka (1) : ma'amula tsakanin jama'a ko ƙasashe, ƙasar Nijar na dangantaka da ƙasashen duniya da yawa.

(2) **Rahoto** : bayyanai a takaice, bincike ; yin rahoto kan wata haraka.

Rapporteur : mai rahoto : mai nauyin kammale bayyanan wata mafawara. Samun matsayin mai rahoto cikin wata ƙungiya.

Rapport périodique : rahoto lokaci-lokaci : rahoton da ake bayar da lokaci zuwa lokaci.

Rapprochement : kusanto-wa : matsowa kusa da kusa. Kusanto ra'ayiyuka da suka sha bamban.

Rassemblement : Taro : haɗuwa : yan ƙwadago na kiran magoyan bayansu ga wani taro.

Rassurer : Tabbatar da : kwantar da hankali, nuna aminci. Bai wa jama'a tabbaci kan wani abu.

Ratification : halin rattaba hannu : amincewa, tabbatawa. Rattaba hannu kan yarjeniyar zaman lahiya.

Ratifier : rattabawa : amincewa, tabbatawa. Ƙasar Nijar ta rattaba hannu kan wata yarjejeniya.

Ratio : rabo : wani abin da ake rarrabawa gida-gida. Rabon maza da na mata.

Ration : yawa : daidai bakin abin da ya isa, maras ƙaramci. Yawan abincin da mutum ke ci cikin rana.

Rationalisation : halin fasaltawa : tsarintawa, daidaitawa. Fasalta kashe-kashen kuɗin ƙasa.

Rationaliser : fasaltawa : tsarawa, daidaitawa. Fasalta harakoki daban-daban

Ravitaillement : Halin bayar da : rabon cimaka, ko wani abu, samu. Bayar da cimaka ga talakkawa.

Rayonnement : yaɗuwa : wadata, warwatsuwa, ci-gaba ;sanya hannunsa wajen yaɗuwar arziki cikin ƙasa.

Réaction : Halin Mayar da magana : Halin mayar da martani bayan an taƙuli mutum. mayar da magana take yanke.

Réaffirmation : ƙara, sake tabbatawa : nanata wani abu, halin bayar da tabbaci kansa. 1. Gwamnati ya sake tabbata ranar shirya zaɓe.

Réaffirmer : ƙara tabbatar da : nanatawa, bayar da tabbaci ; sake tabbata ƙiyayyarsa kan wani abu.

Réajustement : halin daidaitawa : tsarintawa. Daidaita kashe-kashen kuɗin.

Réalisme : Halin gaskiya : wanda ya dace da abin da ke gaskiya. Nuna halin gaskiya.

Réalité : haƙiƙa : Abin da yake na gaskiya, wanda babu ƙarya a cikinshi, halayen zaman duniya. Zancenshi haƙiƙan ne.

Réalité du terrain : wahalolin aikatawa : matsalolin da ake samu cikin tafiyar da waɗansu ayyuka, ko halayen zaman rayuwar duniya.

Réanimation : halin farfaɗar da : dukan dubarun da suka danganta da halayen farfaɗar da mutum idan ya suma. Ɗakin falfaɗar da mutane.

Rebelle : ɗan tawaye : wanda yake adawa da gwamnati ta hanyar ɗaukar makamai don yaƙin neman wani abu. Ɗan tawaye sun aje makamai a ƙasar Nijar.

Reboisement : dashen itatuwa : Aikin dasa itatuwa kan wani hili. Dashen itattuwa na kare hamada cikin ƙasa.

Récapituler : Maimaitawa : taƙaicewa, jimilcewa. Maimaita mahimman kanun wani jawabi.

Recel : ɗan hali : sata. An kama shi, saboda ya aikata ɗan hali.

Recensement : ƙidayar mutane : lissafin jama'a cikin ƙasa, ko lissafin wani abu can daban. A shekarar alif ɗari tara da tamanin da takwas an yi ƙidayar mutane a ƙasar Nijar.

Réception : karɓa : amsa. Karɓar wani taimako. **Liyafa** : haɗuwa ta cin abinci. An shirya liyafar cin abinci.

Recession : gurguncewar tattalin arziki: kwantawar harakokin kasuwanci, lafawar halin tattalin arziki :.An shiga cikin lokaci na gurguncewar halin tattalin arziki.

Recette : Cinaki : bakin kuɗin da aka samu, kuɗin da aka tattara. A albakacin ranar salla yan kasuwa sun yi cinaki da yawa.

Recevabilité : halin karɓuwa: halin wanda ke gaskiya. Ana binciken takardun yan takara daban-daban don gano masu karɓuwa.

Recherche : bincike : nema, don ci ma wani guri. Binciken ilimin kimiyya.

Recherche fondamentale : bincike na nazariyya : bincike na farko kahin a shiga bincike mai zurhi.

Récipiendaire : mai cin amfani wani abu : Mutumen da zai ci ribar wani taimako.

Récipissé : shaidar karɓa : takarda mai tabbatar da an karɓi wani abu. Takardar shaidar kuɗin lanho.

Réclamation : Neman hakki: tambaya, neman a cika masa wata buƙata. Gabatar da neman hakki..

Recommandation : Umurni : Goyon baya neman a yi wani abu ; shawara. Mahalarta taro sun gabatar da umurni daban-daban.

Recomposer : Sake tsarawa : sake shiri cikin wani abu. Sake tsara yan wasan ƙwallon ƙafa.

Recomposition : Sulhu halin sake tsarawa : Sake shirya wani abu, gyaran fuska. Sake tsara hukumomin ƙasar Nijar.

Reconcilisation : sulhu, Halin sasantawa : zaman kawo shiri, zaman kawo kwanciyar hankali. An yi zaman sasantawa tsakanin gwamnatin ƙasar Nijar da yan tawaye a ƙasar Aljeriya.

Reconnaissance : Shaidawa: gano wani abu, bincike. Kar mutum ya ƙarda abin da bai shaida ba.

Reconversion : Halin sauyawa : canzawa, kawo sauyi cikin wani

abu. Samun ci-gaban ƙasa na buƙatar sauya halaye ga al'umma.

Record : cin babbar nasara : cin irin nasarar da ba a taɓa ci ba. Cin babbar nasara ga zaɓe.

Recours : ɗaukaka ƙara : Halin ƙin amincewa da hukumancin da aka yanka wa mutum a koti. Ya ɗauki datattar hanya don ɗaukaka ƙara.

Recours effectif : datacciyar ɗaukaka ƙara : ƙauɗaka ƙara wanda ke kan ƙa'ida.

Recouvrement : tattara : karɓa, amso abubuwa daban-daban daga hannun mutane. An tattaro kuɗin lanho da mutane suka daɗe ba su biya ba.

Recrudescence : Kamari : abkuwar wani abu cikin tsanani. Sata ta yi ƙamari ƙwarai a shekarun baya-bayan ga cikin garin yamai.

Recrutement : ɗauka : rubuta suna, ɗaukar ma'aikata. An shirya jarrabawa don ɗaukar ma'aikata.

Recteur : Shugaban jami'a : Shugaba mai jan ragamar jami'a. Shugaban jami'ar birnin yamai ya ɗaukaka ranar soma karatu.

Rectification : Gyara : Halin gyara wani kuskure. Cin gyara.

Recyclage : Horo : horo na musamman da ake bai wa ma'aikata don su ƙara saninsu. Horon malamman makaranta.

Rédacteur : Mawallafi : mai rubuta matanai, ko mai rubuta jaridu. Mawallafan jaridu sun kafa ƙungiya.

Rédaction : Mawallafa : ɗakin rubuce-rubucen jarida. Shugaban mawallafa.

Redevance : Tara : waɗansu y'an kuɗi da ake karɓa gun mutane dangance da wani amfani da ake yi masu. Tarar y'an gidan radiyo-mai-hoto.

Redistribution : Halin rarrabawa : kalkasawa. Rarraba wa kowa aikinshi.

Redressement : Halin falfaɗar da : kawo tsari cikin wani abu, bunƙasawa. Falfaɗar da tattalin arzikin ƙasa.

Réduction : Ragi : afuwa, sassabtawa. Gwamnati ya yi ragin ma'aikata.

Réélection : Sake zaɓa : sake daukar mutum a muƙamin da ya taɓa riƙewa. Sake zaɓar shugaban ƙasa.

Référence : Madogara : abin da yake abin dafawa kanshi, na tushe. Wannan littafin ne madogarar aikin.

Référendum : Zaɓen amincewa, ko rishin amincewa : zaɓen cewa i, ko a'a, zaɓen raba gardama. An shirya zaɓen amincewa, ko na rishin amincewa da tsarin mulki a ƙasar Nijar.

Réflexion : Tunani : nazari. Yin tunani kan wani abu.

Réforme : Gyara : kawo canje-canje cikin wani abu, kyautata shi ; kawo gyara ga tsarin bayar da ilimi a ƙasar Nijar.

Réforme de l'administration : Sake tsarin hukumomi : kawo canje-canje (cikin hukumomin ƙasar Nijar).

Réfugié : Ɗan gudun hijira : mutumen da ya tserike daga ƙasarsu dangance da waɗansu dalilai don tsirar da ransa ; ƙasar Nijar na ƙumshe da y'an gudun hijira kimanin su ɗari uku.

Refugié politique : Ɗan gudun-hijira kan ra'ayin siyasa : mutumen da ya tserike, ko aka cilasa wa da ya bar ƙasarsu dangance da ra'ayinsa na siyasa.

Régénérer : Ruɓanya : yaɗuwa, rarrabuwa gida-gida. Gindin iccen kabewa na ruɓanya gida-gida.

Régie : Hukuma : wurin tafiyar da harakokin hukumanci cikin ma'aikata. Ya biya kuɗin sanarwa a wurin hukumancin gidan radiyo.

Régime : Mulki : tsarin tafiyar da hukumancin ƙasa.

Régime parlementaire : Tsarin mulki inda majalasar dokoki ke da cikakken iko.

Regime d'émission de monnaie : tsarin buga kuɗi : dubaru, hanyoyin da ake ɗauka wajan ƙera kuɗi.

Régime d'exception : mulkin kama karya : mulkin danniya.

Régime disciplinaire : mulki mai fifita ladabi : tsari wanda a cikinshi ke da kwai ladabi da biyayya.

Régime matrimonial : tsari mai bai wa ɗiya mata iko : tsarin mulki mai fifita mata.

Régime militaire : mulkin soji.

Régime pénitentiaire : tsarin gidan kaso : abin da ya danganta da tsare-tsare a gidan kaso.

Région : jaha : wani yanki da ke cikin ƙasa. Jahohin ƙasa.

Régional : Na jaha : wanda ya shafi jaha. Zaɓen jaha.

Régionalisation : Tsarin jahohi : saka wa jahohi ragamar hukumanci, cin gashin kai, da tafiyar da tsare-tsare.

Régionalisme : Bambancin jaha : nuna bambanci dangance da jahar da mutum ya fito, nuna son jaharsa hiye da ƙasa baki ɗaya. Mai ra'ayin bambancin jaha.

Régisseur : mai tafiyar da harakoki.

Régisseur d'une prison : mai tafiyar da harakokin gidan kaso.

Régistre : kirgam, kundi : babban littafi inda ake rubuta abubuwa na yau da kullum.

Rubuta sunansa cikin kirgam na kasuwanci.

Régistre des affaires : kudin harakoki : littafin da ake rubuta harakoki da aka yi cikinshi saboda halin mantuwa.

Règlement : (tsarin) : dokoki da ka'idodi na tafiyar da mulki, ko wata kungiya. Tsarin tafiyar da wani abu.

Règlement financier : ka'idodin tafiyar da harakokin kudi : matakan da suka dace cikin tafiyar da harakokin kudi.

Règlement intérieur : ka'idodin tafiyar da wani tsari : matakan da ke kayyade halin tafiyar da wani tsari.

Règlementaire : dattace : wanda ya dace da doka da ka'idodi. Dattatun matakai.

Réglementation : Tsari : dukan matakai da ka'idodi da wani tsari ya kumsa. Tsarin samun magana cikin kafofin watsa labarun kasa.

Régner : Jan ragamar mulki : tafiyar da hukumanci. Rarraba kawunan mutane don shinfida mulkinsa da kyau.

Régularisation : Kawo daidaita : danganto wani abu da doka, ko da ka'idodi.kawo daidaito ga matsayin makarantun boko masu zaman kansu.

Réhabilitation : sake ingantawa : sake bai wa mutum darajarshi, ko kuma wani hali. Sake inganta darajar mahukunta.

Réinsertion : agaji : samar wa mutum aikin yi. Tsarin agaji ga matasa.

Réintégration : Sake mayar da : sake mayar da mutum cikin aikinshi. Sake mayar da ma'aikaci cikin aikinshi.

Réjouissance : Farin ciki : murna, jin dadi. Farin cikin jama'a.

Relance de l'économie : farfadowar tattalin arzikin kasa : bin hanyoyi na farfado da tattalin arziki, ba shi karfi. Tayar da tattalin arzikin wata kasa.

Relation : Dangantaka : hulda tsakanin kasashe. Kasar Nijar na da kyaukyawar dangantaka da makwabtanta.

Relation amicale : amintaka : hulda tsakanin mutane, ko tsakanin kasashe.

Relations extérieures : dangantaka da kasashen waje : hulda da kasashen waje.

Relation bilatérale : hulda ta kasa da kasa : ma'amula tsakanin kasa da kasa.

Remaniement : kawo sauyi : yin gyaran fuska, sake tsarawa. An kawo sauyi cikin gwamnati,

Remaniement ministériel : sauyin ministoci : kawo canje-canje cikin gwamnati.

Remaniement législatif : kawo sauyi cikin dokoki : yi wa dokoki gyaran fuska.

Remarque : lura : la'akari, jawabi, gargaɗi. Yin lura.

Remettre : gabatar da : gabatar da, mikawa, gabatar da murabus kinsa.

Remettre en cause : musantawa : karyatar da. Musanta wani zance.

Remou : Tarzoma : zanga-zanga, halin tayar da zaune tsaye. Tarzomar y'an makaranta.

Remou social : tarzomar jama'a : zanga-zanga, tashin hankali cikin kasa.

Rendement : mizani, yawa : wani sakamakon da aka cim ma. Mizanin aikin y'an makaranta.

Rendement par travailleur : mizanin aikin kowane ma'aikaci : awon bakin kokarin kowane ma'aikaci.

Renforcer : karfafawa : kara wa wani abu karfi. Karfafa had'in kan y'an kasa.

Renommée : shahara : halin wanda ya yi suna kwarai. Shahararren sarki. Cin ma shahara.

Renovation : sabuntawa : zamanautar da wani abu, kawo sauyi. Sabuntawar da kayayyakin aiki.

Renseignement : bayyani : samun karin haske, neman labari. Neman bayyanai gun wani.

Renseignement généraux : ofishin y'an sanda mai kula da kiyaye lafiyar kasa.

Renversement : Juyi : kifewar, birkicewar wani tsari. Juyin mulkin, kama karya.

Renversement d'un regime : juyin mulki. Kifar da mulki.

Réorientation : sake tsari : yin gyaran fuska, sake wa wani abu manufa. Sake tsarin makarantu.

Répliquer : Mayar da martani : tarewa, mayar da martani ga duk wani farmaki.

Report : d'agawa : halin mayar da wani abu har zuwa gaba, d'aukakawa. Daga ranar zaman taron majalasa.

Repreneur : wanda ya d'auka: mutunen da ya d'auki wata masana'anta da ke shirin mutuwa. Mutunen da ya d'auki masana'antar ya fara sallamar wad'ansu daga cikin ma'aikatan.

Représaille : ramuwar gaya : shan fansa ; kai farmaki.

Réprésentant : wakili : mutunen da ke jagorantar wata tawaga, ko wata kasa. Dan majalasar dokoki, wakilin kasa ne.

Répresentation : Wakilci : halin wakiltar wata kasa a kasar waje, jakadanci ofishin wakilcin wata kasa.

Repression : Ɗuka : ban kashi, hakuntawa, tarwatsar da wata zanga-zanga. Kungiyoyi daban-daban sun yi allawadai da dukar da aka saka wa masu zanga-zanga.

République : Jamhuriya : ƙasa mai y'anci. Jamhuriyar Nijar

République laique : Kasar da ake girmama duk ibada : ƙasar da ba a hihita wani addini, ƙasar da dukan addinai ke da matsayi guda a gaban hukuma.

Requête : Nema ; tambaya : roƙo, gabatar wa wani hurumi takarda don neman wani abu. Isarwa juju takardar tambaya ko neman wani izini.

Requête : shahara : suna ya shahara ; ya yi suna sosai.

Requin : Mai wayo : ƙenƙerau, mai wuyar harakoki. Zama mai wayo.

Requisition : tambaya : buƙatar da malamin shari'a ke gabatarwa kai tsaya cikin tafiyar da shari'a don a kawo mishi wani mutum. Hanyoyin tambaya.

Réquisitionner : yin kamuwa : wajabawa, dattatar hanya ta tilasawa ma'aikaci da ya tsaya wurin aikinshi idan ma'aikata na cikin yajin aiki. Yin kamuwar ma'aikata.

Réquisitoire : jawabin yanke shari'a : jawabin da malamin shari'a ke gabatarwa don tabbatar da zargin da ake yi wa mutum. Malamin shari'a ya gabatar da muhimmin jawabi wajen yanke shari'a.

Réseau : ƙungiya : haɗuwar jama'a da yawa wuri guda don cin ma wani guri. Tarwatsar da ƙungiyar y'an ta'adda.

Résilier : sokewa : dakatar da wani abu tsayar da shi. Soke wata yarjejeniya.

Résistance : Jan (shan) daga : kariyar kai, jimiri, dauriya. Shan daga.

Résistance anti coloniale : shan daga da y'an mulkin mallaka : ƙin amincewa da wata danniya, kariyar kai da y'an ƙasashen Afirika suka yi wa y'an mulkin mallaka.

Résolution : tsaidaddar shawara : matakin da aka tsayar da, wanda ake fatan ganin an aikata. Tsaidaddar shawara dangance da wani abu.

Respect : Daraja : girma, ladabi ga wani, kowani abu. Ya bai wa na gabanshi daraja.

Respect strict : Cikakkar daraja, kan gaskiya : a game da abin da ba a saba wa ƙa'idodinshi ko kaɗan.

Responsabilité : Gabata : shugabanta, ɗaukar wani nauyin kansa. Shi ke da nauyin gabatar ayyukan.

Responsable : magabaci : shugaba, jagora. Y'an sanda sun

kame magabacin bangaren y'an adawa.

Ressort : wanda ya shafi : wanda ya danganta da wani abu. Gabatar da shari'a abu ne wanda ya shafi malamman shari'a.

Ressortissant : Dan asilin (gari) : mutumen da ya fito daga wani gari. Y'an asilin ƙasar Maraɗi.

Ressource : Albarka : dukiya, arziki, mallakar ƙasa. Albarkatun ƙasa.

Ressources humaines : masu ƙarfin tafiyar da wani aiki : dukan mutanen da ke iya yin wani aikin ƙarfi cikin ƙasa, matasa.

Restauration : Maidowa : daidaitawa, kawo gyara. Maidowar zaman lafiya cikin ƙasa.

Restreindre : Tauyewa : dannewa, ƙuntatawa. Tauyar da y'ancin jama'a.

Restriction : Tauyewa : danniya, halin ƙuntatawa. Tauyrwar y'ancin jama'a

Restructuration : sake tsarintawa : kawo gyare-gyare, shiri. Sake tsarinta masana'anta gwamnati.

Résultat : sakamako : abin da ke biyo bayan wani abu. Kotin ƙoli ta amince da sakamakon zaɓen birane.

Résultats définitifs : sakamako na dindindin : sakamakon da babu wata tankiya kanshi, wanda babu duk wani y'ancin dawowa kanshi.

Résultats globaux : sakamako a jimilce : sakamako daban daban da aka haɗa wuri guda.

Résultats provisoires : sakamakon da ba na dindindin ba : sakamakon da ake iya ƙin amincewa da shi, wanda ba na ƙarshe ba.

Résumé : takaitawa : halin gabatar da mahimman abubuwa kan wani abu, faɗin shi a gurguje, sauƙaƙawa. Taƙaita jawabi.

Rétablissement : Maidowa, sake rayawa : sake daidaita wani abu, gyara. mayar da hulɗa tsakanin ƙasashe kan fannin jakadanci.

Réticence : tsoda-tsoda : yin i'ina wajen tafiyar da wani abu, nuna rishin amincewa sosai. Aikata wani abu ba tare da tsoda-tsoda ba.

Retirer : jayewa : fasa wani abu, sauya ra'ayi. Jaye ƙara.

Retombées : riba : sakamako, wani alherin da akan iya samu, sakamako da ke biyo bayan wata kaɓɓa kan fannin siyasa.

Rétombées financières : riba kan fannin tattalin arziki : alherin da ke biyo bayan wata haraka ta kuɗi, kuɗin da ake ci.

Retraite : antare : ritaya, ƙayyadadden lokacin aikin ma'aikaci dangance da yawan shekarunshi. An sanya shi antare da ƙarhi.

Retransmission : watsawa nuni : halin gabatar da shire-shire a kafofin watsa labaru na radiyo da talbijin ; sanyawa, gwadi. Sanyo wasan ƙwallon ƙafa a gidan radiyo.

Rétro-actif : mai dawowa baya : Abin da ke da halin ya je ya dawo, mai yancin hakunta abin da ya wakana a baya. Doka mai halin dawowa baya.

Réunion : haɗuwa : haɗuwa, mahawara, shawara taro. Gayyatar wata haɗuwa.

Revalorisation : darajanta-wa : ɗaukaka darajar wani abu, ba shi girma, darattawa. Bai wa al'adun ƙasa daraja.

Revalorisation des langues nationales : halin bai wa harsunan ƙasa daraja : halin ingantar da harsunan ƙasa ba su daraja ƙwarai ta hanyar amfanin da su cikin harakokin yau da kullum cikin ƙasa.

Revenu : Amfani : zufar mutum, albashi. Samu, amfani kan wata sana'a.

Revision : gyaran fuska : kawo sauye-sauye ga dokoki ko ƙa'idodin ƙasa don dattat da su da tsarin mulki. Yi wa usular jam'iyun siyasa gyaran fuska.

Révocation : kora : tsige mutum daga aiki, sokewa. Korar ma'aikata daga aiki.

Révolte : Tawaye : bore ; tadin ƙayar baya : ƙin daratta doka, zanga-zangar jama'a baƙi ɗaya. Tadin ƙayar bayan jama'a.

Révolution : Juyin juya-hali : yin tadin ƙayar baya ; tarzoma, yin zanga-zanga da niyyar kawo sauye-sauye cikin wani tsari. Juyin juya-hali na neman sauye-sauye a ƙasar Sin.

Revue : jarida : littafi mai ƙumshe da sharhin labaru daban-daban wanda yan jarida ke wallafawa. Jarida mai bayyana kowane sati.

Richesse : dukiya : albarkar ƙasa, arziki. Dukiyar ƙasa.

Rigueur : tsanani : tsauri. Doka mai tsanani.

Risque : Haɗari : kasada. Yin kasada

Rite : Al'ada : tabi'a, abun sabo, ibada. Yanka raguna ga sallar layya na cikin al'adun addinin musulumci.

Rôle : matsayi : aiki, muƙami. Ya kyautu kowa ya san matsayinshi don tafiyar da aiki da kyau.

Rouage : Hanyoyi ; sashe : ɓangaren wani abu. Sassan hukumanci. Rouage de l'économie : sassan tattalin arziki : ɓangarori daban-daban na tattalin arziki.

Royaume : daula : ƙasar da ke bin tsarin sarauta, wadda ke ƙarƙashin jagorancin sarki. Daular maroko.

Rubrique : hili : shire-shire, tsare-tsare. Sauraren hilin zaɓi-sonka.

Rumeur : jita-jita : ƙishin-ƙishin;,, zancen da bai tabbata ba. Baza jita-jita ko'ina.

Rupture : halin yankewa : tsaidawa, bari, katsewa. Yanke hulɗa tsakanin ƙasashe.

Rural : na karkara : wanda ya shafi halayen zaman karkara. Mazauna karkara.

S

Sabotage : zagon ƙasa : yin ƙafar angulu cikin tafiyar da wata haraka, ɓata wani abu. Yin zagon ƙasa ga tsare-tsaren ƙasa.

Sacrifice : halin bayar da kai : miƙa wuyansa wajen tafiyar da wani abu, halin sadaukar da kai, sanya kai. Ya bayar da kanshi ƙwarai wajen kariyar ƙasarshi.

Sagesse : Dattijantaka : aiki da hankali ; tsinkayen nesa, yin hatara wajen tafiyar da wani abu. Nuna dattijanka.

Sahel : sahail : busashen yanki mai fuskantar hamada. Ƙasar Nijar na ɗaya daga cikin ƙasashen sahail.

Saisir : tuntuɓa : shaidawa, taɓawa. Tuntuɓar koti a game da wata haraka.

Saison : zamani : lokacin da ke dacewa da wani abu cikin shekara. Zamanin damana. Lokacin damana.

Salaire : albashi : zufar aikin mutum. Samun albashi kan lokaci.

Salaire moyen : matsakaicin albashi : albashi ɗan ƙalilan wanda ma'aikaci ke samu.

Salaire de base : albashin da ya dace da wani aiki dangance da bakin karatun ma'aikaci.

S.M.I.G. : Ƙayyadadden albashi : bakin ƙaramin albashi da aka yanke.

Salaire brut : albashin da ba a yanke komi ba a cikinshi : albashin da ba a hidda ko dala ba a cikinshi.

Salaire à terme échu : albashi kan lokaci : biyan albashi daga wata ya mutu.

Salubrité : tsabta : aikin kawar da ƙazamta, ko salte a wuri. Kiyayewa da tsabtata gari.

Sanction : hakunci : ɗaurin da ake yi wa mutum a koti dangance da laifin da ya aikata. An yanke mishi hukunci.

Sanction populaire : neman ra'ayin jama'a : shirya zaɓe kan wata haraka don samun ra'ayin jama'a.

Santé : lafiya : halin mutumen da ke da ƙoshin lafiya. zama cikin ƙoshin lafiya.

Santé morale : kwanciyar hankali : zama lami-lafiya, samun cikakkar lafiyar jiki da ta hankali.

Santé publique : lafiyar jama'a : samun ƙoshin lafiya ga jama'a.

Saper : ƙetata : yin aikin baƙin ciki kan wani abu, hasada. Yin ƙeta ga wani tsari.

Satisfaction : cikakken jin dadi : samun biyan bukata, wadata. Samun cikakken jin dadi.

Sauvegarder : kiyayewa : karewa, yin tanadi. Kiyaye al'adun kasarmu.

Savoir faire : fusa'a : ilimi, dubarar aikata wani abu. Nuna fusa'a kan wani abu.

Sceau : hatumi : tambari. Hatumin kasa.

Scène : abin mamaki : abin kardawa, mai jan hankali. Ganin wani abun mamaki.

Scène internationale : fagen duniya : jama'ar duniya baki d'aya, ra'ayin jama'ar duniya.

Scène politique : fagen siyasa : abin da ya shafi fannin siyasa.

Science : kimiyya : fannin ilimi mai bayar da sani kan fannin fusa'a, bincike da gwaje-gwaje don kyautata rayuwar d'an adam. Ilimin zamentakewa.

Scolarisation : halin ilmantar da : aikin bayar da horo da ilimi. Ilmantar da kananan yan mata.

Scolarité : Tsawon shekarun karatu : yawan shekarun da d'an makaranta ke d'aukar karatu.

Scrutateur : mai nauyin shirya zabe : mutunen da ke sanya hannunshi cikin tafiyar da zabe. Zama cikin masu shirya zabe.

Scrutin : zabe : dukan shire-shiren da suka shafi harakokin jefa kuri'a. Zaben da aka shirya yana cike da kurakurai kwarai.

Scrutin uninominal : zaben d'an takara guda : tsarin zabe inda mai zabe ke jefa wa d'an takara guda kuri'a.

Scrutin plurinominal : zaben yan takara da yawa : tsarin zabe inda mai zabe ke jefa wa yan takara da yawa kuri'a.

Scrutin majoritaire à deux tours : zabe na rinjaye mai zagaye biyu : zaben raba gardama tsakanin yan takara masu kuri'u kusan guda.

Scrutin proportionnelle : zaben la'akari da yawan kuri'u : tsarin zabe wanda ake rarraba kujeru dangance da yawan kuri'un da jam'iya ta samu.

Scrutin uninominal à deux tours : tsarin zaben d'an takara mai zagaye biyu : zaben d'an takara guda mai zagaye biyu.

Scrutin uninominal à un tour : tsarin zaben d'an takara mai zagaye guda : zaben d'an yin takara guda mai zagaye guda.

Se prévaloir : d'aukar kai : gwadin kai, fadin rai, yin takama. Nuna d'aukar kai.

Séance : mafawara : zaman mafawarar mambobin wata kungiya masu yanke shawara. Babban zaman mafawara.

Scéssioniste : yan a ware : yan tawaye, masu neman ɓallewa, masu neman yanci. Yan a ware na zaman sansantawa da hukumomin ƙasa.

Sécheresse : fari : halin wurin da ba ya da ɗanyantaka. Fari ya addabi jama'a.

Sécheresse financière : rishin kuɗi : halin talauci.

Sécourir : agazawa : taimakawa, gudummuwa. Agaza wa maras lafiya.

Secret : sirri : dukan labarun da ba su kyautu ba a bayyana su ga kowa. Rikon asiri.

Secrétaire : magatakarda : mutumen da ke da nauyin tafiyar da harakokin wata ƙungiya. Sakatarin ƙungiyar ƙwadago ya gabatar da wani jawabi.

Secrétaire d'Etat : sakatarin ƙasa : mutunen da ke da muƙamin minista.

Secrétaire dactylographe : sakatari mai aiki kan mashin, mai karɓar baƙi kuma ta sanassar da zuwansu ga maigidanta.

Secrétaire de bureau : sakatarin buro : mutunen da ke kula da wasiƙa da kuma waɗansu takardu daban.

Secrétaire de direction : sakatarin magabata : mutunen da ke kula da rubuta wasiƙu da waɗansu takardun ma'aikata.

Secrétaire particulier : sakatari na musamman : sakatari na kusa ga maigida, mai bayar da shawara kan waɗansu abubuwa.

Secrétaire général du gouvernement : babban sakatarin gwamnati.

Secteur : fanni : ɓangare, sashe, dukan abun da ya shafi wani reshe na wani abu. Fannin kiwon lafiya.

Secteur privé : fannin masu harakokin zaman kansu : fannin da bai shafi gwamnati ba.

Secteur public : na ƙasa : abubuwan da suka shafi gwamnati.

Secteur économique : fannin tattalin arziki : dukan harakokin da suka shafi cinakayya da ayyukan juya kuɗi.

Secteur marchand : fannin saide-saide : dukan harakokin da suka shafi saye da saidawa.

Secteur social : fannin zaman jama'a : dukan harakokin da suka shafi jama'a.

Section : sashe : tsara wani abun ɓangare-ɓangare. Shirya wani abu sashe-sashe.

Secteur nationale : sashen ƙasa na fanni: wakilcin ƙasa.

Sectoriel : na sashe ; na fanni : wanda ya shafi wani sashe (fanni). Siyasa kan wani fanni

Sécuriser : kwantar da hankali : tabbatar da zaman lafiya, da kwanciyar hankalin jama'a. Kwantar da hankalin jama'a cikin ƙasa.

Sécurité : kwanciyar hankali : halin tabbatar da wadata kan fannin tattalin arziki, da shiryayen tsarin siyasa masu kawo kwanciyar hankali. Nauyi ya rataya wuyan gwamnati na kawo kwanciyar hankali cikin ƙasa.

Sédentaire : Na wuri ɗaya ; manomi : wanda ke zaune wuri guda, wanda ke tafiyar da rayuwarshi inda yake zaune. tafiyar da rayuwa irin ta manoma.

Ségrégation : bambanci : yin son rai, raba ɗayan biyu. Nuna bambancin launin fata.

Sélection : rairaya : zaɓa, zaɓen mutane ko waɗansu abubuwa dangance da sharuɗɗan da aka shinfiɗa. Yin rairaya.

Sémi privé : na gwamnati da masu zaman kansu : ma'aikata ko masana'anta na gwamnati da masu zaman kansu tare.

Semi présidentiel : Na tsarin mulki mai ruwa biyu : tsarin mulki wanda a cikinshi shugaban jamhuriya ba ya da cikakken iko.

Séminaire : taron ƙara wa juna ilimi : haɗuwar aiki, da masanyar ra'ayi don kyautata aiki. Ministan ilimi ya shirya wani taron ƙara wa juna ilimi don daidaitar rubutun harshunan ƙasa.

Sénat : zauren shawara : tsarin mulki mai bai wa ɣan majalasar da ke cikin zauren cikakken iko. Zauren shawarar ƙasar Amarika.

Sens : Ma'ana : manufa. Jawabi mai ma'ana.

Sensibilisation : aikin wayar da kai : yin bayanai kan wani abu don fahimtar da mutane, kawo haske. Wayar da kan jama'a kan ciwon sida.

Sensibilité : ra'ayi : tunani da hasashe daban-daban da ke bambanta mutane kan abubuwa. Ra'ayinsu guda da babbanshi.

Sentence : hukunci : yanke hukunci, shari'ar da aka yanke. bayyana hukuncin da aka yanke.

Séparation des pouvoirs : Ƙayyadewar iyakar iko : Nuna bakin ikon kowa.

Séparatisme : neman a ware : neman ɣancin, tawaye. Mai ra'ayin a ware.

Séquelle : shaida : sakamako, tambo, wani abin da yake tsayawa ko ma abin da ya haddasa shi ya wuce. Nuna shaida.

Sérenité : lumana : kwanciyar hankali, zaman lafiya yin aiki cikin lumana.

Service : aiki : aikin amfanar ƙasa, taimakon ƙasa. Aikin ƙasa.

Service militaire : aikin soji : bauta wa ƙasa kan fannin aikin soji.

Service public : aikin gwamnati : aikin da ya shafi ƙasa, wanda ba na masu zaman kansu ba.

Serviteur : bawa : wanda ke kashe kanshi wajen yi wa waɗansu aiki. Mai bauta wa ƙasa.

Serviteur du peuple : mai bauta wa ƙasa : mai aiki don ƙaruwar jama'a.

Servitude : bauta : zama ƙarƙashin mallakar wani. Bautar ƙasa..

Session : zaman taro : lokacin da wata majalasa ko wani koti ke zaman taron yanke shawara. Zaman taron da aka ƙayyade.

Session budgétaire : zaman taron kasahin kuɗi : zaman taron da ake ƙayyade kuɗin da za su shiga da waɗanda za su fita daga cikin aljihun gwamnati.

Session extraordinaire : zaman taro na musamman : zaman taron da dokoki ba su ƙayyade ba, zaman taron gaugawa.

Session ordinaire : zaman taron yau-da-kullum : da dokoki suka ƙayyade : haɗuwa ta lokaci zuwa lokaci wadda dokoki suka ƙayyade.

Session plénière : babban zaman taro : zaman taro mai haɗa dukan mambobin wata majalasa, ko na wata ƙungiya, ko jam'iyun siyasa.

Seuil : maƙura : lyakar wani abu, cin ma maƙurar talauci

Siècle : ƙarni : Adadin shekaru ɗari, lokacin da ake rayuwa cikinshi. Ƙarnin wayewar kanun mutane.

Siège : cibiya : 1) Wurin da wani abu yake girke. Cibiyar jam'iyya.

2) **Kujera** : cim ma wani muƙami bayan an shirya zaɓe. Kujerar ɗan majalasar dokoki.

Sièger : Halarta : halartar wata mafawara, samun kujera a majalasar dokoki.

Signal d'alarme : Alarmar fargar da : Alamar abkuwar wani abu, gargaɗi, fargar da jama'a kan abkuwar wani abu.

Signalisation : wutacen ƙayyade zirga-zirgar injina : amfani da wutace kan hanyoyin don sauƙaƙa zirga-zirga motoci kan titina.

Signataire : wanda ya rattaba hannu : wanda ya nuna amincewarsa da wani tsari ta hanyar sanya hannunsa. Zaman cikin waɗanda suka rattaba hannu kan wata yarjejeniya.

Signature : sa-hannu : shaidar amincewa da wani abu, ɗaukar alƙawali kan wani abu. Sa-hannu kan wata yarjejeniya.

Simple : mai sauƙi : wanda ba ya da wuyar warwarewa. Mai sauƙin fahimta. Matsala mai sauƙin warwarewa.

Sinistre : bala'i : abin al'ajabi, mai tayar da hankalin jama'a. Bala'in da ya auku ya tsugunnar da mutane da yawa.

Sionisme : kaka gida : tsari na siyasa da addini wanda ke fatan cin ma gurin kafa ƙasar izira'ilu cikin faɗin ƙasar palastin, kahin girkuwar ƙasar izira'ila. Palastinawa suna yaƙar yan kaka gida.

Site : wuri : cibiyar wani abu, inda ake samin wani abu. Wurin tonon zinariya.

Situation : hali : matsayin da mutum, ko wata ƙasa ke ciki. Halin da yan makaranta ke ciki na bayar da tausai.

Slogans : kalamai : mangan-ganu na taɗa wani abu, ko na habaici, ko kuma na tayar da jiyojin waɗansu magoya baya. Yan makaranta sun yi ta nuna kalamai na ƙiyayya ga gwamnati.

Social : na jama'a : dukan abin da ya shafi jama'a. Tsarin jama'a.

Socio-culturel : Na zamentakewa da al'adu : abin da ya shafi halin zaman jama'a da tabi'o'insu.

Socio-économique : Na zamentakewa da tattalin arziki : abin da ya shafi halin zaman jama'a da tattalin arziki.

Socio-éducatif : Na zamentakewa da tarbi'a : wanda ya shafi halin zaman jama'a da koyarsuwa.

Socio-professionnel : wanda ya shafi masu aiki iri guda.

Socialisme : ra'ayin gurguzu: tsarin siyasa da na tattalin arziki cikin ƙasa wanda ya bambanta da tsarin hujjar jari. Kafa tsarin ra'ayin gurguzu cikin ƙasa.

Sociétaire : wanda ya zuba jari : wanda ya zuba jari cikin tafiyar da wata masana'anta ko kampani. Zuba jari cikin masana'anta.

Société : Jama'a : dukan al'ummar da ke zaune cikin ƙasa iya zama tare da jama'a.

Société civile : Gungun jama'ar ƙasa : dukan jama'a da ƙungiyoyi daban-daban cikin ƙasa da ba na siyasa ba.

Société de développement : sabon tsarin ci-gaba : tsarin da aka shinfida da fatan cin ma kyautata rayuwar al'umma.

Sociologie : ilimin zamentakewa : ilimin halayyar zaman jama'a. Yin karatun ilimin zamentakewa.

Soins médicaux : Magungunnan likita : taimako kan fannin lafiya. Likitoci sun yi wa mutanen da suka samu hatsari da mota magungunna.

Solennel : Na gaban jama'a : wanda ake yi a bainar jama'a. An yi shagulgulan naɗin shugaban jamhuriya a gaban jama'a.

Solidarité : zumunci : haɗin-kai, dangantaka, huldɗa tsakanin jama'ar ƙasa. Tabbatar da zumunci tsakanin yan ƙasa.

Sollicitation : Buƙata : roƙo, gayyata, buƙata. Buƙatar wani abu.

Sollicitude : Kulawa ; buƙata: halin wanda ake da muradin shi saboda tsananin so ko ƙauna. Ba ya da izinin zuwa ko'i na saboda ana buƙatar shi ƙwarai.

Solvable : mai halin biya : mai halin biyan bashin da ake biyar shi. Ya ciyo bashi a banki saboda yana da halin biya.

Sommaire : taƙaitacce : wanda aka sauƙaƙa ; faɗin wani zancen a taƙaice.

Sommet : babban haɗuwa : taro, ranyo, mafawara , haɗuwa mai ɗumbin mahimmanci. Shugaban jamhuriya ya halarci babbar haɗuwa ƙungiyar haɗin kan Afirika (O.U.A)

Sondage : binciken neman ra'ayi : bincike don gano ra'ayin mutane daban-daban kan wata haraka. Shirya binciken neman ra'ayi.

Soulèvement : hargitsi : tadin ƙayar baya, tarzoma. Hargitsin jama'ar ƙasa.

Soumission : Miƙa wuya, bauta : yin ladabi da biyayya kan wani abu, darattawa. Bautar Allah.

Soupçon : zato, zargi : ƙazahi. Ana zaton ko shi ne ya yi sata.

Soupçonner : yin zato : yin zargi, yin ƙazahi kan wani. Yin zato kan mutum.

Soupeser : kimantawa : kwatantawa, aunawa. Kimanta darajar wani abu.

Source : Majiya : tushe, matsiri. Majiyar labari.

Source officieuse : majiyar da ba a tantance da ita ba : abin da ba hukumomi suka bayyana shi ba, wanda ba su tabbatar da shi ba.

Sous-alimentation : rishin cin isasshen abinci, mai wadatar jiki. A na zaton rishin lafiyar na da nasaba da rishin isasshen abinci.

Sous-commission : ƙaramin kwamiti : wani rukuni da ake keɓewa daga cikin kwamiti. Zama cikin ƙaramin kwamiti.

Sous-développé : wanda bai samu ci-gaba ba : mai neman samun ci-gaba, wanda bai cin ma tattalin arziki ba. Ƙasashen da ba su ci-gaba.

Pays sous-developpés : ƙasashe masu neman ci-gaba : ƙasashen masu fuskantar talauci, masu neman cim ma tattalin arziki. Ƙasar Nijar na cikin ƙasashe masu tasowa.

Sous-préfecture : Ofishin ƙaramin gwamnan jaha : ma'aikatar da ke karkashin

jagorancin ƙaramin gwamnan jaha. Ofishin gwamnan jahar Tasawa.

Sous-production : rishin wadata : ƙaramcin wani abu. Rishin wadatar abinci. ya kawo tsadarshi.

Sous-produit : abin da ake yi daga wani abu : wanda ko fitowa daga wani abu. Man gujiya ana samun shi ne daga gujiya.

Sous-réserve : Da sharaɗi : kan wani cika wani sharaɗi. Takardunshi sun samu shiga amma da sharaɗin sai ya kawo bak.

Sous-secteur : ƙaramin fanni : fannin da ya rataya ga wani babban fanni. Karamin fannin kasuwanci.

Sous-section : reshe : wata ƙungiya da ke rataya ga babbar ƙungiya. Reshen jam'iyar siyasa.

Sous-sol : ƙarƙashin ƙasa : wanda ke can ƙasa cikin ƙasa. Karkashin ƙasa ake tono zinariya.

Sous-titre : ɗan kai : karamin kai da ake rubutawa bayan an rubutu muhimmin kai. Rubuta ɗan kai.

Souscription : sanya hannu : amincewa, rattaba hannu, goyon baya. Sanya hannu kan wani alƙawali.

Soutien : goyon baya : amincewa da ra'ayin wani, ko na jam'iya ko ƙungiya. Kawo cikakken goyon baya ga jam'iyarsa.

Souvenir : Tuni : lissafo wani abu wanda ya daɗe, ko kuma wanda ya wakana cikin ƙaramin lokaci. Kowa ya yi tuni da bara bai ji daɗin bana ba.

Souverain : mai yancin kai : mai cin gashin kanshi, wanda babu damar mallakarshi. Kasa mai yancin kai..

Souveraineté : Yanci kai : halin ƙasar da ba ta ƙarƙashin mallakar wata ƙasa, mai tsarin mulkin kanta. Yancin kan ƙasa.

Spécial : na musamman : muhimman, wanda ba a amfani da shi sai cikin waɗansu halaye na daban. Manzo na musamman.

Spécialiste : shahararre : mutunen da ya lakanci wani abu, wanda ya yi suna kan abu, ƙwararre. Shahararren malami.

Spécialiste des droits de l'homme : Shahararren masani kan fannin yancin ɗan Adam : mutunen da ya ƙware kan fannin sanin yancin yan Adam.

Spécialité : shahara : tara ɗumbin sani kan wani fanni. Shahara kan fannin siyasa.

Spéculation : Baranda : harakokin kuɗi ko na kasuwanci wanda ake yi don cin riba ddangance da hawa da faɗuwar canji.

Sphère de l'Etat : yankunan hukumanci : dukan jahohin da ke karkashin hukumancin gwamnati. Yankunan hukumanci daban-daban.

Splendeur : girma, arziki, albarka : mai kyau, mai haske da wadata. Girman gari, albarkar kasa.

Spolier : Tauyewa : wawurewa, kwashewa. Tauye kayayyakin mutane.

Spontané : Na tak ɗaya : mai faruwa ba tare da an tsaya yin nazari ba. Bayar da amsa tak ɗaya.

Spontanément : wanda ke faruwa tak ɗaya : cikin ba a tantance da shi ba, cikin ba a shire shi ba. Tak ɗaya mutane duk sai suka gamu.

Sport : motsa jiki : tada jiki ta hanyar guje-guje ko tsalle-tsalle. Ana shirya wasannin motsa jiki a hilin kwallon kafa.

Sportif : na motsa jiki : wanda ya shafi motsa jiki. Tattalin kayayyakin motsa jiki.

Stabilité : halin daidaituwa : gyaruwar waɗansu abubuwa. Daidaituwar harakokin tattalin arziki.

Stabilité politique : daidaituwar yanayin siyasa : gyaruwar harakokin siyasa.

Stabilité économique et sociale : daidaitawar harakokin tattalin arziki da samun kwanciyar hankalin jama'a.

Stade : hali : yanayin da wani abu yake cikinshi, matsayi. Harakar ta kai mawuyacin hali. Halin ci-gaba.

Stage : horo : samun karin ilimi da kwarewa kan fannin aikinsa. Samun cikakken horo.

Standard : daidaitacce : tsayayye, mikakke. Daidaitaccen harshe.

Station : tasha : wuri da ake aje motoci da injina. Tashar motoci.

Statistiques : Ilimin kididdiga : dubarun lissafe-lissafen harakokin jama'a kan fannin zamantakewa da kuma kan fannin tattalin arziki. Alkaluman kididdiga.

Statuer : yanke shawara : tsayar da magana kan wani abu, kitse magana. Yanke shawara kan wani zance.

Statut : ka'idodi : dokoki masu kayyade halin tafiyar da wata kungiya ko wata jam'iya. K'a'idodin jam'iya.

Statutaire : kayyadadde : wanda dokoki suka kayyade. Zaman taron da ke kan ka'ida.

Stimuler : kara kuzari : kara karfi, kara himma wajen aikata wani abu. Jawabin madugun yan adawa ya kara wa magoya bayansu kuzari.

Stipuler : bayyanawa : kayyadawa, faɗi, faddin wani

abu a bayyane. Tsarin mulkin ƙasar Nijar yana bayyana cewa ƙasar Nijar guda ce, babu duk wani halin rarraba ta.

Stratégie : dubara : azanci, dukan hanyoyin da ake ɗauka don cim ma wani guri. Dubarun siyasa.

Stratégique : wanda ya shafi dubara : azanci, dubaru. Dubarun yaƙi.

Strictement : kan gaskiya cikin tsanani : aikata wani abu cikin matsuwa, yin aiki tsakani da Aly lah. Yin wani aiki kan gaskiya.

Structuration : sanya tsari : halin daidaita wani abu, tsarinta shi. Sanya tsari kan tafiyar da kashe-kashen kuɗin ƙasa.

Structure : sashe : kimtsi, ɓangare daban-daban na wasu abu, tsari cikin wani abu. Sassan ma'aikatun bayar da ilimi da horo.

Structure de participation au developpement : tsarin tafiyar da ci-gaba : tsare-tsare na tafiyar da ci-gaba.

Structure politique : jam'iyar siyasa : kungiyar siyasa.

Structure économique : tsarin tattalin arziki : tsarin tafiyar da harakokin tattalin arziki.

Studio : Ɗakin shirye-shirye : wurin da ake tsara silma, ko shirye-shiryen gidan radiyo da na talbijan don gabatar da su. Ɗakin magana.

Subordonné : bara : wanda ke aiki ƙarƙashin wani, ɗan gida ; zama baran wani.

Subsidiaire : na rataye : na ƙarin bayyanai, wanda ba ya da bamban mahimmanci. Tamba-yoyi na rataye.

Substitut : muƙaddashi : mataimaki mai halin maye gurbin wani muƙaddashin shugaban kotin ƙoli.

Subvention : tallafi : gudun-muwa, taimako da gwamnati ke kawo wa wata ƙungiya . Bayar da tallafi.

Subversif : Mai hura wuta ; mai dagular da tsari : mai yamutsar da tsari. mai burkutar da tsari. Dagular da tsarin wata haraka.

Subversion : ɗagula tsari : halin burkutar da wani tsari, ɓatawa. Duk ya zo ya dagular da tsarin.

Succéder : Mayewa, cin gado : ɗare kujerar sarauta. Ci gadon sarauta.

Succès : nasara : dacewa, samun nasara wajen tafiyar da wani abu. Samun nasara.

Sud-sud : Tsakanin ƙasashe masu tasowa, kudu da kudu : huldɗa tsakanin ƙasashe masu tasowa. Ɗangantaka ta kudu da kudu.

Suffrage : zaɓe ; ƙuri'a: ra'ayi na amincewa, ko na rishin amincewa da ake gabatar da shi

wajen zaɓe, ɗaukar abin da ransa ke so zaɓe.

Suffrage universel indirect : zaɓe wanda a cikinshi wakillai ne ke zaɓen ɗan takara.

Suffrage universel : zaɓen da ya shafi kowa da kowa : zaɓe wanda a cikinshi dukan yan ƙasa ke iya halarta a matsayin yan takara, ko a matsayin masu zaɓe muddin sun cika sharuɗɗan halartar zaɓen.

Suffrage universel direct : jefa ƙuri'a da kansa don zaɓen ɗan takara.

Suggestion : shawara : halin bayyana ra'ayinsa ga wani. Gabatar wa wani wata shawara.

Suivi et évaluation : bi sau-da-ƙafa da jimiltawa : zuba ido kan tafiyar da wani abu tare da ƙayyade amfaninshi. Biyar wani guri sau da ƙafa tare da jimilta shi.

Sujétion : zama ƙarƙashin mallaka : halin wanda ake mulki, mallaka, halin danniya. Zama ƙarƙashin mallakar wani.

Supérieur : na gaba : wanda yake babba cikin wani tsari. Girmama na gaba.

Supérieur hiérarchique : magabaci : wanda yake da babban muƙami cikin wani tsari.

Supériorité : hiyayya : hali, nuna girma. Nuna hiyayya.

Supervision : zura ido : biyar wani tsari sau-da-ƙafa, larwai, dubi. An gayyato shaharraru kan fannin zaɓe don zura ido.

Suppléant : kambaci, canji : mutunen da ke cike gurbin wani mai maye kujerar wani. Zaman kambacin ɗan majalasar dokoki.

Suppléer : Shiga kambanci, yin canjin... : cika muƙamin wani, tafiyar dai ayyukan wani idan ya kasance babu shi nan.

Supplément : na ƙari : abin da ke kyautata wani abu. Ƙarin wani abu kan hanyar taimakon jama'a.

Support institutionnel : Dokokin tsarin mulki : dokoki da hukumomi ke dogara a kansu, dokokin da tsarin mulki ya ƙumsa. Yin amfani da dokokin tsarin mulki.

Supporter : Kawo goyon baya : amincewa da wani ra'ayi, yarda da wani abu. Kawo goyon baya ga yan wasan ƙwallon ƙafar ƙasarsu.

Suprême : na ƙoli : wanda ya zarce kowa cikin wani tsari, mai cikakken iko. Kotin ƙoli.

Surestimation : ƙari : yin ƙari wajen lissafin wani abu. yin ƙari kan wani abu.

Sureté de la personne : kwanciyar hankalin ɗan Adam : halin tabbatar wa dukan yan ƙasa cikakkar kwanciyar hankali tabbatar da kwanciyar hankali ga jama'a.

Surexploitation : Tsananin yin amfani : aikin ƙwaruwa : wuce mizani wajen amfani da wani abu, yin amfani ƙwarai da wani abu, ƙwaruwa. Ƙwaruwar mutum kan aiki.

Surfacturation : linka kuɗi : ruɓanya kuɗin wani abu, yin ƙari kan kuɗin wani abu da niyyar cutar ƙasa. Ana tuhumar mutane da yawa da laifin linka kuɗi cikin kashe-kashen kuɗin masa'na'antu.

Sursis : Wa'adin kashedi : wa'adin da ake yanke wa mutum, idan wa'adin ya zarce mutumen bai yi wani laifi ba to sai a soke hukuncin da aka yanke mashi. Yanke wa mutum ɗaurin shekara uku tare da kashedi.

Susceptible : Mai yiyuwa, wanda kan iya faruwa : wanda kan iya wanzuwa, mai iya wakana. Abubuwan da kan iya faruwa.

Suspect : Na shakku : wanda ake da zata kanshi, wanda ake nesa-nesa da shi. Samun shakku kan mutum.

Suspendre : dakatar da : tsayar da wani abu har tsawon wani lokaci, jinginewa. Dakatar da aikin wata doka.

Suspension : halin dakatar da : halin tsayar da wani abu, dakatar da wani abu. Dakatar da wani mataki.

Symbiose : haɗin kai : zaman lumana, zama cikin cikakkar fahimtar juna. Kawo haɗin kai cikin ƙasa.

Symbole : Madubi ; shaida : wanda ke zama shaida cikin wani abu. Shugaban ƙasa shi ne shaidar haɗin kan ƙasa ; shi ne madubi a game da haɗin kan yan ƙasa.

Syndicat : sandika ; ƙungiya: ƙungiyar mai nauyin kare hakkin magoya bayan ta. Sandikar yan kasuwa.

Synthèse : taƙaici : rahoton wani aiki, ko na wata haɗuwa. Yin taƙaicin wata mafawara.

Système : tsari : kimtsi, shiri na tafiyar da wani abu. Tsarin siyasa.

Système éducatif : tsarin horo da bayar da ilimi : halin tafiyar da harakokin karatu cikin ƙasa.

T

Table ronde : mafawara : zaman tattaunawa kan wad'ansu matsaloli. Zaman mafawara kan matsalolin karatu a ƙasar Nijar.

Tailler sur mesure : Tsara abun da ya dace da guri : kafa dokoki na son rai, masu amfanar wad'anda suka kafa su. Y'an adawa na ƙorahin cewa magabatan ƙasa sun kafa dokokin da suka dace da gurorin da suke son cin ma.

Talent : Fusa'a, baiwa : halin aikata wani abu, baiwa. Kawo agaji ga matasa masu fusa'a.

Tare : cikas : babban rishin sanin abin da ta kamata a ce mutum ya sani, sakaci ; rishin fahimtar dokokin ƙasa babban cikas ne ga d'an siyasa.

Tarif : Allon bayyani na kud'i : allo wanda a kanshi ake bayar da bayyanai daban-daban kan kud'in abubuwa, ko kan kud'in aikata wani aiki. Allon bayyanan kud'i cikin wani shago.

Tarifaire : wanda ya shafi bayyanan kud'i: wanda ya shafi kud'i daban-daban da ake biya.

Taux : mizani : kashin da ake fitar da a cikin d'ari ; mizanin haihufa yana saurin ƙaruwa a ƙasashen Afirika.

Taux d'analphabétisme : mizanin masu jahilci : yawan mutanen da ba su koyi karatu da rubutu ba a cikin d'ari.

Taux de couverture sanitaire : mizanin kiwon lafiya : yawan mutanen da suke samun kula kan fannin kiwon lafiya cikin d'ari.

Taux de natalité : mizanin haihuwa : yawan mutanen da ake haihuwa a shekara cikin ƙasa cikin d'ari

Taux de scolarisation : mizanin yan makaranta : yawan yaran da suka samu zuwa makaranta cikin d'ari.

Taux d'intérêt : mizanin ruwa : ribar da ake samu cikin dala d'ari bayan an bai wa mutum rancen kud'i.

Taxe : tara : haraji, ko asangam da gwamnati ke karba a wurin talakkawa. Biyan kud'in tara.

Taxe professionnelle : jangali: kud'in tara da kampanoni ko masana'antu ke biya.

Taxe sur la valeur ajoutée : tara dangance da gwargwadon cinakin da mutum, ko masana'anta ke yi.

Technique : fusa'a : ilimin kimiyya mai bayar da damar ƙirƙira abubuwa masu kyautata rayuwar d'an Adam. Ilimin fusa'a.

Télécommunication : Gidan

waya : wurin daidaita harakokin sadarwa da watsa labaru cikin duniya. Aika sako ta hanyoyin gidan waya.

Téléphone : talho : hanyar sadarwa ta waya. Yanke wa mutum talho.

Télévision : Radio-mai-hoto, talbijin : radiyo mai hoto, kafar watsa labaru. Sauraren labaru a radiyo-mai-hoto.

Témoignage : Shaida : 1) godiya, jin dadi. Aika sakon zumunci.

2) shaida : tabbatar da gaskiya, ko rishin gaskiyar wani abu. Gabata gaban koti a matsayin mai shaida.

Témoignage de satisfaction: shaidar (sakon) godiya : shaidar farin rai, na jin dadi.

Tendance : Alama : manufa. Alamun suna nuna da yan adawa ke kan gaba wajen zabe.

Teneur : Abin da wani abu ya kumsa : manufofi daban-daban da wadansu kalamai ke dauke da su. Abin da wani jawabi ya kumsa.

Tenir en détention : Tsaro : daure mutum, kai mutum gidan kaso. Tsare mutum gidan yari.

Tension : tashin hankali : bacin rai, tarzoma, tashin hankali rishin jituwa, hargitsi. Tashin hankali ya yi kamari.

Tentation : Jan hankali : abin da ke jan hankalin, mutum. Daurewa a gaban wani abin jan hankali.

Tentative : yunkuri : tsira wata niyya, soma fara wani abu. Gano wani yunkurin juyin mulki.

Tenue : shiri : wani abin da aka tsara wanda za ya faruwa. Ana shaida wa jama'a da za a shirya shaushawa a duk cikin fadin kasa.

Terreur : Razana : ban tsoro, yin barazana, daukar matakai masu tsanani kan fanni daban-daban don girkar da mulkinsa. Daukar matakai don razanar da jama'a.

Territoire : yankin kasa : kasa, fadin yankin da jama'ar kasa ke zaune. Dokar da aka kafa ta shafi yankin kasa gaba-daya.

Terroriser : yin ta'adda : tsoratar da, dukan abubuwan tashin hankali da wata kungiya ke aikatawa don tayar da zaune tsaye. Tashi tsaye kan yan ta'ada cikin duniya.

Terrorisme : ta'addanci : halin aikata aikin asha, tayar da zaune tsaye. Aikata ta'addanci cikin kasa.

Test : jarabawa : hanyar gano fahimtar abubuwan da aka bai wa mutum darasi a kai. A kowace karshen shekara ana shirya jarabawa cikin maka-rantu.

Tester : jarabawa : hanyar gano bakin fahimtar mutum kan wani abu. Jaraba dalibai.

Texte : shirin ɗoka : dukan dokokin da ake gabatar wa majalasar dokoki don yanke shawara a kai. Y'an majalasar dokoki sun amince da shirin dokar da aka gabatar masu.

Texte définitif : amintattar doka : dokar da aka yarda da ita, wadda aka amince da ita.

Texte original : Doka ta ainahi : dokar da ba a yi wa gyaran fuska ba.

Texte législatif : kafaffar doka : dokar da ake zartar da.

Texte d'application : dokar zartarwa : dokar da ake tafiyar da aiki da ita.

Texte fondamental : tsarin mulki : tsare-tsaren dokokin tafiyar da hukumanci cikin ƙasa.

Thème : Jigo : abin tattaunawa a kai abubuwan nazari a kai, waɗanda ake mafawara a kai. Abubuwan tattaunawar wata mafawara. Jigon hira.

Théorie : Nazariyya : ilimin hasashe : tsararrin ra'ayoyi da ake gabatar da a game da wani fanni. Ɓullo wani sabon salo na nazariyya.

Thésaurisation : tsimi : tariyar wani abu da yawa. Yin tsimin kuɗi.

Thèse : ra'ayin : shawara, ko ra'ayin da ake amincewa da shi, kuma a yi ta kariyar shi ta kowane hali. Goyon bayan wani ra'ayi.

Tiers monde : ƙasashe masu tasowa : dukan ƙasashe y'an ba ruwanmu, ƙasashen da suka kasance mafi talauci a duniya. Taimakon ƙasashe masu tasowa kan fannin fusa'a.

Titre : shaida : takarda mai bayar da tabbacin uzunin gudanar da wani abu. Shaidar shiga kasuwanci.

Titre de transport : shaidar uzunin sufiri : uzinin gudanar da zirga-zirga da mota.

Tolérance : haƙuri da juna : fahimtar juna, yin haƙuri da juna. Addinin na kira ga yin hakuri da juna ; jimiri.

Tolérer : Yin haƙuri : yahewa. Ɗaukar haƙuri kan dukan al'amurrar duniya.

Torture : Azaba ; duka : shan kashi, ko shan wahala. Saka wa mutum azaba.

Tourisme : Yawon buɗa ido : yawan shaƙatawa. Tafiya yawon buɗa ido.

Touriste : ɗan yawon buɗa ido : wanda ke yawon shaƙatawa. Y'an yawon buɗa ido na ziyartar gidan kallon birnin yamai kowace shekara.

Tournée : rangadi : balaguro, ziyara. Ministan noma ya shiga rangadin kimanta damana.

Tournoi : kombala : gasar wasannin motsa jiki. Kombalar kokowar gargajiya.

Tradi-praticien : mai maganin gargajiya : mai warkar da mutane daga wani ciwo ta hanyar maganin gargajiya. Amfani da maganin gargajiya.

Tradition : al'ada : duk abun da ya shafi gargajiya, tabi'u, abin da yake na ƙashin kan al'umma. Kowace al'umma na da al'adunta.

Traditionnel : na'al'ada : wanda ya shafi al'ada, wanda ya shafi gargajiya. Tattalin al'adun ƙasa.

Traduction : fasara : bayyanawa, mayar da wani jawabi daga wani harshe zuwa wani harshe. Fasarar jawabin shugaban ƙasa.

Trafic : sarande : satar hanya, fasa ƙwabri. Saranden miyagun ƙwayayyaki.

Trafic d'influence : nuna muƙami : amfani da matsayin da ake da shi don samun gyara ko rangwame kan waɗansu harakoki.

Trafiquant : ɗan sarande : mutunen da ke yin sarande. Saraden makamai.

Trahison : cin amana : halin tayar da alƙawali, daratta alwashin da aka ɗauka. Ayyukan cin amanar ƙasa.

Train : hali : halin rayuwar da ake ciki, yanda harakoki ke tafiya. Sauya halin rayuwarsa.

Train de vie : halin rayuwa : gwargwadon yanda ake tafiyar da rayuwarsa.

Traité : yarjejeniya : amincewa, yarda ; rattaba hannu kan wani abu da niyyar amincewa. Rattaba hannu kan wata yarjejeniya.

Traités régionaux : yarjejeniya tsakanin jahohi : yarjejeniyar da ake rattaba hannu a kai tsakanin jahohi masu iyaka da juna.

Traite des esclaves : fataucin bayu : jagwal da aka ɗora yi ta hanyar hurhuren baƙaƙen mutane da waɗansu abubuwa ko kayayyaki.

Traitement cruel : dukar rishin imani : duka mai tsanani, ta rishin jin tausai. An yi wa wani ɓarawo duka irin ta rishin imani.

Trajet : hanya : titi, hanya. Gamuwa da wani kan hanya.

Tranche : Aji : kashi, ɓangare. Ajin matasa.

Transaction : harakokin kasuwanci : hada-hadar kasuwanci. Harakokin kasuwanci.

Transfert : wakilta : bai wa wani izinin wakiltar jama'a. Wakilan ƙasa.

Transfert de technologie : masanya kan fannin ilimin fusa'a : masanya tsakanin ƙasashe musamman kan fannin ilimin fusa'a.

Transformation : sauyi : yin gyaran fuska, canji. Sauyar da halayen jama'a.

Transition : wucin gadi : lokacin rikon kwarya. Gwamnatin wucin gadi.

Transitoire : na wucingadi : na rikon kwarya, na karamin lokaci. Paraminista na wucin gadi.

Transmettre : isar da : Kaiwa, bayar da. Isar da sakon gaisuwa.

Transmission : Isarwa : bayarwa, sadarwa. Isar da wani jawabi.

Transparence : haske : kai waye, yin wani abu cikin adalci. Kawo haske cikin tafiyar da harakokin jama'a.

Travestir : karkatar da : sauyawa, juyar da ; karkatar da ra'ayin wani.

Trésor : 1/ dukiya : Arziki, ɗumbin kuɗi. Tara dukiya ta haram.

2) **Betalmanin kasa :** ma'adanar kuɗin kasa. Betalmanin kasa.

Trésorerie : kudi : dukiyar kasa kan fannin kuɗi ; matsalolin kuɗi cikin kasa.

Tribunal : koti : gidan shari'a, hurimi. Ya shigar da kara a koti.

Tribune : Dandali : hilin wasanni, ko wata mafawara. Dandalin soyayya.

Tributaire : malakakke : wanda ke karkashin mallakar wani ; zama karkashin mallakar wani.

Trouble : hargitsi : tarzoma, zanga-zanga, tashin hankali. Tayar da hargitsi cikin kasa.

Tutelle : rataye : reshinan ma'aikatu da ke rataye ga waɗansu ma'aikatu ; zama karkashin wani abu.

Ofishin yan sanda, rataye yake ga ma'aikatar ministan cikin gida.

Tuteur : wakili : mutumen da ke da nauyin tattalin wani ɗa da ba na shi ba. Ana gayyatar wakilan yan makaranta.

Tyranie : muzguna ; zalunci : kama karya, nuna tsananin hukumanci. Mulkin muzguna.

U

Ultérieur : zuwa gaba : abin da ke isowa, wanda za ya wakana a gaba. An ɗaga ranar mafawarar har har zuwa gaba.

Ultimatum : wa'adi : yin kashadi, yanke wa gwamnati wani lokaci don ya aikata wani abu. Y'an makaranta sun yanke wa gwamnati wa'adi a game da koke-kokensu.

Ultime : na ƙarshe : wanda ake yi daga baya, a ƙarshe ; yin kira na ƙarshe.

Unanime : Na baki ɗaya (yarda) : wanda kowa ya amince da shi. An ɗauki wata niyya tare da yarda kowa.

Unanimité : yardadde baki ɗaya : wanda ya samu amincewar kowa. Abin da ke yardadde ga jama'a.

Unification : haɗi : gamewa wuri guda, ƙarfafawa. Haɗin-kan ƙasa.

Unifier : haɗawa : jonawa wuri guda. K'arfafawa. A haɗa ƙarfi.

Uniformiser : mayar da bai ɗaya : daidaitawa, mayar da iri ɗaya. Mayar da ayyuka daban-daban bai ɗaya.

Unilatéral : Na niyyar kansa : ɗaukar niyya ba tare da an shawarci sauran mutane ba, bugun gaba. Ya tawaye sun ɗauki niyyar kansu ta tsagaita yaki.

Union : 1) Haɗuwa : daidaitar ra'ayuyyuka, shiri tsakanin juna. Aikata wani abu cikin haɗuwar hankula da zukatu.

2) **ƙungiya :** gamuwa. Haɗaɗɗiyar ƙungiyar yan makarantar Nijar .

Union locale des coopératives : ƙungiyar manoma : gamuwar manoma don kafa ƙungiya cikin wani yanki.

Union nationales des coopératives : ƙungiyar manoma ta ƙasa : Haɗuwar manoman ƙasa don kafa ƙungiya.

Union régionale de coopérative : ƙungiyar manoma ta jaha : haɗuwar manoman jaha don kafa ƙungiya.

Union sous-régionale de coopérative : ƙungiyar manoma ta ƙaramar jaha : haɗuwar manoma cikin ƙaramar jaha don kafa ƙungiya.

Unité : haɗin-kai : shiri da juna, zama hankali kwance, cikin lumana. Haɗin-kan y'an ƙasa.

Unité africaine : haɗin-kan y'an afirika : zumunci tsakanin y'an afirika.

Unité nationale : haɗin-kan y'an ƙasa : zumunci tsakanin dukan y'an ƙasa.

Universalité : halin abu sananne ga duniya : abin da

duniya gabaɗaya ta shaida da shi. Sanannar doka a duk faɗin duniya.

Universel : na duniya : abin da ya watsu ko'ina a duniya, wanda ya shafi duniya baki ɗaya. Ilimin kimiyya abu ne da ya shafi duniya baki ɗaya.

Université : jami'a : makarantar koyon ilimi mai zurfi. Yin karatu a jami'a.

Urbain : na birni : wanda ya shafi birni. Birnin yamai.

Urbanisation : Gyaran gari : zamanantar da gari, yin gyare-gyare cikin gari.

Urbanisme : Ilimin gyaran gari : ilimin tsarantar da gari, kawo gyare-gyare. Fasalin gyaran gari.

Urgence : gaugawa : halin abin da ke buƙatar hanzari. Kafa tsarin shire-shire na gaugawa.

Urne : Akwatin ƙuri'u : wurin da masu zabe ke saka ƙuri'u. Sojoji sun ƙwace akwatin ƙuri'a.

Utilité : amfani : halin abin da ake amfani da shi. Amfanin karatu na da yawa.

Utopie : hasashen banza : hasashen da ba su da kan gado, waɗanda ba su la'akari da waɗansu halaye. Jawabin da ya gabatar, ba ya ƙumshe da wani abin ƙwarai sai hasashe-hasashen banza.

V

Vacance : Hutu : 1) Lokaci da ma'aikaci ko y'an makaranta ke shiga hutu. Hutun y'an makaranta.

2) Halin wani mukami da ba kowa kanshi.

Kasancewar wata kujera hukumanci kanguwa.

Vacance de la présidence de la république : kasancewar kujerar shugaban jamhuriya kanguwa : lokacin da shugaban jam'huriya ya yi murabus, ko rai ya yi halin shi kafin wani ya maye kujerar.

Vacance de la république : roshe tsarin demokarad'iya : lokacin da aka soke tsarin mulki kuma aka rushe majalisar dokoki bayan juyin mulki cikin kasa.

Vacance de poste : gushewar wani aiki : lokacin da ma'aikaci ke barin aikinshi ba tare da izini ba, lokacin da kujerar wata ma'aikata ke kasancewa kanguwa.

Vacances présidentielles : lokacin hutun shugaban jamhuriya : lokacin da shugaba ke shiga hutu.

Vacant : kango : wanda ba a tsare ba, wanda ba komi cikinshi. Kangon d'aki.

Vaincre : cin nasara : samun ya yi galaba kan abokin hamayyarshi. Ya ci nasara kan abokin hama yarshi.

Vainqueur : wanda ya ci nasara : wanda ya ci nasara wajen wata kombala ko wata takara, zakara cin nasara wajen zabe.

Valable : datattace : na kirki, na kwarai, mai amfani ; kawo datattun hujjoji.

Valeur : Daraja : bakali, halin wanda ake kauna. Mutane sun zabe shi saboda darajar da Aly lah ya yi mishi.

Valeur culturelle : abubuwan gargajiya : dukan abubuwan da suka shafi al'adu.

Valeur refuge : hannu jari : sayan wad'ansu abubuwa saboda tsaron fad'uwar hannun jari.

Valeur sociale : al'adun jama'a : dukan abubuwan da suka shafi akida da tabi'u da kadarorin jama'a.

Valider : tabbatar da : amincewa bayyanawa. Kotin koli ta tabbatar da sakamakon zabe.

Validité : Inganci : tsawon wa'adi : tsawon aikin wani abu, mai amfani. Inganci katin dandite shekara biyar ne a kasar Nijar.

Valoriser : Bayar da daraja ingantawa : daranjatawa,

darattawa. Bai wa harshunan gida daraja.

Vandalisme : dabanci shashanci : ɓannatar da kayayyakin ƙasa ko na jama'a. Yin aikin shashancin cikin gari.

Variété : iri : abu mai yawa, halin abin da ke da yawa. Al'adu iri-iri.

Végétale : tsanwa : ciyawa. Kayan lambu.

Veiller : bi sau da ƙafa : kula da, kiyayewa, yin la'akari da wani abu. Bi sau-da-ƙafa yadda ake zartar da dokoki.

Vente : sayarwa da : harakokin kasuwanci, sana'a. Sayarwar da kayayyaki a kasuwa.

Vente d'action : sayarwar hannun jari : Sayarwar da hannun jarin da mutum ke da a cikin wani kampani.

Verdict : shari'a : shari'a, hukunci. An yanke shari'a.

Vérification : bincike : aikin tabbatar da wani abu, yin larwai a kai. Kwamiti mai nauyin gudanar da bincike.

Version : ra'ayi : ra'ayin mutum, ko na wata ƙungiya ; gabatar da ra'ayinsa kan wani abu.

Vert : tsanwa : mai launin tsanwa. Tsanwar takarda.

Vertu : aƙida : samun hankalin aikata abin ƙwarai tare da kauce wa na banza. Bai wa yaro kyaukyawar aƙida.

Vétuste : tsofaffe : abin da ya tsufa, wanda ya daɗe ; tsafoffin kayayyaki.

Vice : Mugunta ; lahani : mugun nufi, laifi. Yin lahani ga wani.

Vice président : mataimakin shugaba : wanda ke bi ma shugaba wajen tafiyar da wani aiki.

Vicissitude : hali : sauye-sauye, abubuwan alheri da na baƙin ciki masu biyar juna. Halaye daban-daban da suka danganta da rayuwar ɗan Adam.

Victime : wanda wani abu ya sama : mutunen da ya yi rauni ko ya rasa ransa, ko ya yi hasara a dalilin wani abu. Magajin gari ya ziyarci mutanen da ambaliyar ruwa ta haddasa wa hasara.

Victoire : nasara : cin galaba wajen wata kombala, wata takara. Cin babbar nasara kan zaɓe.

Vide : kango : hili, wurin da babu komi cikinshi, wanda ba ya ƙumshe da komi. Kangon aljihu.

Vide juridique : rishin tanadin ƙa'ida kan wani abu : rishin kafa dokar da za ta ƙayyade waɗansu abubuwa.

Vie : rai : halin zaman duniya, halin rayuwa. Ya rasa ranshi cikin haɗarin mota.

Vie nationale : zaman ƙasa : zaman mutane cikin wata ƙasa, rayuwar ƙasa.

Vie privée : zaman kansa : girka wad'ansu harakoki na cin moriyar duniya, baicin wani aiki can daban da mutum ke yi ; abin da ya shafi rayuwar mutum.

Vigilance : hatara : lura, kula kiyayewa kan wani abu. Yin hatara a game da tafiyar da wad'ansu ayyuka.

Village : ƙauye : garin da ke cikin karkara. Mazaunan ƙauye sun kafa ƙungiya.

Ville : birni : maraya, yanki mai ƙumshe da jama'a da yawa dangance da harakoki daban-daban.

Violation : halin takawa : karya doka, ko ƙa'ida, ketawa. Wanda ya taka doka za a yi mishi hukunci.

Violer : takawa : karyawa, ketawa. Babu duk wani halin taka doka ga y'an ƙasa.

Visa : izini : shaidar damar da ake bai wa mutun na ya shiga wata ƙasa. Samun izinin shiga ƙasar Amarika.

Vision : ganuwa : halin fahimtar wani abu, ra'ayinsa a kai. Samun cikakkar ganuwa kan fannin siyasa.

Vital : muhimmi : halin abun da ke taimakawa ƙwarai, wanda sai da shi ake iya tafiyar da wani abu kishin ƙasa muhimmin abu ; ne cikin tafiyar da ginin ƙasa.

Vitalité : kuzari : himma, ƙoƙari wajen zartar da wani abu. Kuzari wajen tafiyar da harakokin duniya.

Voeux : fata : nufin alheri ga wani, fatan alheri, barka. Yi wa mutum fatan alheri.

Voie : hanya : titi, santa. Ana gyaran hanyoyi da kud'in haraji.

Voirie : shara : abin da ya shafi ma'aikatar da ke kula da gyaran fuskar gari. Biyan kud'in shara.

Voix : ƙuri'a : ra'ayin da mutum ya gabatar wajen zaɓe ; lissafin ƙuri'u.

Voix consultative : ra'ayi na mai zaman shawara : ra'ayin da ba ya shiga cikin lissafi wajen yanke wata shawara.

Voix déliberative : ra'ayi na yanke shawara : ra'ayin da ke shiga cikin lissafi wajen yanke shawara.

Volontaire : Na sa kai : mai aikata wani abu ba tare da an cilasa mashi ba, na niyyar ƙashin kai. Sa kai wajen tafiyar da ayyukan ci-gaban ƙasa.

Volontariat : Aikin sa kai : bayar da kai. Y'an aikin sa kai ba su da y'ancin shiga yajin aiki.

Volonté : niyya : amincewa, cikakkar niyya. Nuna wata niyya.

Volonté politique : niyya kan fannin siyasa : cikakkar niyyar tafiyar da wad'ansu harakoki daga hukumomi.

Volume : Ci : bakin ɗaukar wani abu. Bido mai cin litir goma.

Volume des échanges : yawan masanya kan fannin kasuwanci : yawan abubuwan da ke shiga da fita tsakanin ƙasashe kan fannin kasuwanci.

Votant : mai zaɓe : mutunen da ke jefa ƙuri'a, wanda ya halarci zaɓe. An liƙa jerin sunayen masu saɓe a bakin rumfunan zaɓe.

Vote : zaɓe : ra'ayi, ko zaɓen wani da hanyar jefa ƙuri'a. Zaɓen yan majalasar dokoki.

Vote personnel : zaɓe da kansa : zaɓe wanda a cikinshi mutum ke jefa ƙuri'a da hannunsa.

Vote par procuration : zaɓen wakilta : zaɓe wanda mutum ke wakilta wani ya bagatar mishi da zaɓenshi.

Vote a bulletin secret : zaɓe na siri : zaɓe wanda a cikinshi mai zaɓe kaɗai ya san abin da ya zaɓa.

Vote à main levée : zaɓen ɗaga hannu : zaɓe wanda a cikinshi ake nuna amincewarsa ta hanyar ɗaga hannunsa.

Vote sanction : zaɓen nuna ƙiyayya : zaɓe wanda a cikinshi masu zaɓe ke nuna wa ɗan takara ƙiyayya ta hanyar ƙin zaɓen shi.

Vouloir : buƙata : so, nema. Buƙatar wani abu.

Vulgarisation : Yaɗawa bazawa : halin sanassar da wani abu, bayyana shi, wayar da kanun mutane a kai. Yaɗawar fusa'o'in noma ko'i na cikin ƙasa.

Vulnérabilité : halin kamuwa : halin cin ma waɗansu matsaloli ko kamuwa da waɗansu cututtuka dangance da wani hali da ake ciki. Kaƙanan yara su ne suka fi kamuwa da cututtuka dabandaban.

Vulnérable : mai iya kamuwa : wanda wani abu kan iya cin ma. Kashin mutane masu kamuwa da waɗansu bututtuka cikin ƙasa.

X

Xénophile : mai ƙaunar baƙi : mutumen da ke son mutane, mai marhaba da baƙi. yana ƙaunar baƙi ƙwarai.

Xénophile : son baƙi : marhaba da baƙi. Nuna ƙaunar baƙi.

Xénophobe : mai ƙyamar (tsanar) baƙi : wanda ba ya ƙaunar baƙi, wanda ke adawa da duk wani abu wanda ba na ƙasarsu ba. Zama mai ƙyamar (tsanar) baƙi.

Xénophobie : Ƙyamar (tsanar) baƙi : rishin son baƙi gudun baƙi. Tsanar baƙi ba abin alheri ba ne.

Z

Zizanie : rishin jituwa : rishin fahimtar juna, rarrabuwar kawuna. Kawo rishin jituwa cikin jama'a.

Zone : Yanki : ɓangaren ƙasa. Matuƙin jirgi ya ratsa cikin yankin da aka haramta mishi.

Zone désertique : busasshen yanki : yanki mai hamada.

Zone nomade : yankin makiyaya : yanki inda makiyaya suke saboda ciyawa.

Zone rurale : yankin karkara: ƙauye, yankin da y'an ƙauye ke zaune.

Zone urbaine : yankin birane : maraya, yanki mai ƙumshe da jama'a da yawa. Yankin sefa : dukan ƙasashen da ke amfani da kuɗin sefa.

Zone franche : yankin yarjejeniya kan fannin kasuwanci : yankunan da ke maƙobtaka da juna inda ake tafiyar da harakokin kasuwanci ba tare da biyan kuɗin duwan ba, ko waɗansu kuɗi can daban.

Zoologie : ilimin sanin dabbobi : ilimin kimiyya da ke nazari kan dabbobi. karatun ilimin dabbobi.

Zootechnique : ilimin dabbobin gida : ilimin da ya shafi bincike kan rayuwar dabbobi don kyautata ta. Goguwa kan fannin ilimin dabbobin gida.

X

Xénophile : mai ƙaunar baki : mutumen da ke son mutane, mai marhaba da baki. yana ƙaunar baki ƙwarai.

Xénophile : son baki : marhaba da baki. Nuna ƙaunar baki.

Xénophobe : mai ƙyamar (baƙanar) baki : wanda ba ya ƙaunar baki, wanda ke adawa da duk wani abu wanda ba na ƙasarsu ba. Zama mai ƙyamar (baƙanar) baki.

Xénophobie : ƙyamar (baƙanar) baki : ɗabi'ar son baki gudun baki, ƙyamar baki ba abin alfahe ba ne.

Z

Zizanie : rashin jituwa : rashin fahimtar juna, tarzabuwar kawuna. Kawo rashin jituwa cikin jama'a.

Zone : Yanki : bangaren ƙasa. Matukin jirgi ya ratsa cikin yankin da aka haramta masa.

Zone déserdique : busasshen yanki : yanki mai hamada.

Zone nomade : yankin makiyaya : yanki inda makiyaya suke sabodin ciyawa.

Zone rurale : yankin karkara: kauye, yankin da yan kauye ke zaune.

Zone urbaine : yankin birane : maraya, yanki mai kumshe da jama'a da yawa. Yankin sela : dukan kasashen da ke amfani da kudin sela.

Zone franche : yankin yaƙe-jeniya kan tsarin kasuwanci : yankunan da ke makobtaka da juna inda ake tsiyar da haraƙokin kasuwanci ba tare da biyan kudin duwan ba, ko wadansu kudi can dabam.

Zoologie : ilimin sanin dabbobi : ilimin kimiyya da ke nazari kan dabbobi. Kerstun ilimin dabbobi.

Zootechnique : ilimin dabbobin gida : ilimin da ya shafi bincike kan rayuwar dabbobi don kyautata ta. Gogowa kan tsarin ilimin dabbobin gida.